Toh yanzu kawae ni danzo anjima kibani address,,,,,,,,,, lahhh rufamin asiri Dan Allah,,,,,,,,,,,,,,,, batarai yayi kaman Wanda take ganinsa,,,,,,,, dalilin ba kyasona shiyasa bakiso nazo yanda kike koh????? Marai raice murya tayi,,,,,,,,, No bafa haka nake nufi ba,,,,,,,,,, to me kike nufi in ba haka bah,,,,,,,,, Allah baban mu zaiyi fada,,,, me yasa zaiyi fada toh??????
Aishi se'an tambayeshi kafin afara zuwa hira wajen yarsa,,,,,,, mehakan yake nufi kenan,,,,,,,, cikin fargaba da zullumin abinda zaije yazo Dan batasan ya zai dauki lamarin ba,,,,,,, Ina nufin saida izininsa ake hira da yarsa,,,,,,,,,,, wani dadi ne yamaimaye masa rai donko ba komai shi bada wasa yazobahh,,,,,,,,,, kuwa yanaso,,,,,,, manya sushiiga maganar tunda wuri,,,, Kara matse fulon dake kirjin sa yayi,,,,,,,,,,,,

Da mamakinta cikin farin ciki taji Yana cewa,,,,,,,,,, barin je insamu Abba yanzu Dan ABARI YA HUCE SHIKE KAWO RABON WANI littafin (sumayya Abdulkadir),,,,,,,,,, nikuma bazan Bari kizama rabon wani bahh,,,,,,,,,,, kantayi magana diff,,,,,,,, yakashe Wayan,,,,,,,, dago wayan tayi sannan tabita da kyaya taccen murmushi,,,,,,,,,,,,

================

MASARAUTAR
KANO

Kiliishii,,,,,,,,,, ne ta kishin  Akan wani tuntu dakagan shi kasan na Gidan sarauta ne Dan bako wani irin tuntu bane da'ake samu ako'inah,,,,,,,,,,, kishin gideh take,,,,,,,,,,,,, wata budurwace Wanda Baza tafi kimanin shekaru ashirin da hudu ba 24 kykkawace sosae fara sol ga dara daran idanuwanta Masu rikita mutane tanada tsayi sosai Ga hips boobs dinta kamar wanda suke shirin fasa yar yaloluwar rigar dake jikinta,,,,,,,,,,,,,

Magana takeyi cikin tashin hankali,,,,,,,,,,, wallahy momy Idan ban aureshi ba bazan Bari wata ta aure shi ba,,,,,,,,,,,, idanu wanta ne yacicciko taci gaba da cewa,,,,,, inason sa inasonsa mumy kitaima min yanzu ko wayansa nakira baya dauka,,,,,,,,,, tun kafin nayi hauka kawae ku aura min shi,,,,,,,,,,, aiba shi ya haifi kansa zebi umarninku,,,,, ,,, na tabba ta idanna aure shi zansashi yasoni,,,,,,,,,, duk wani girman Kai dayake ji dashi sayya sauke shi,,,,,,,,,,,,,,,,,, Kai niko bazai Soni ba Allah sanda nake masa ya ishemu rayuwa,,,,,,,,,,, magana takeyi kamar me tabin hankali,,,,,,,,,,,,,,

Kiliishii,,,,,,,,,,, Wanda randa ke kuna zuciyarta kamar tafito kasa tafado haka take jinta,,,,,,,,,, Dan taki jinin abinda zai bata ran tilon yar yar uwartata ,,,,,,,,,,,,

Kiyi shiru intyy nah Sai nasan yadda nayi mai martaba ya amince da auranku,,,,,,,,,,, Danni ma hankali na zaifi kwanciya bazanso ace wannan dumbin mulki da dukiya yafita ahannun mu ba,,,,,,,,,,, ki kyale komai a hannu na Abdallah Dani yake zancehhh,,,,,,,, Bai Isa ya wulakanta ki nabarshi bah,,,,,,,,,,, nide narufo musu kofa nace ta Allah bata Kuba Dan duk sharrin ku Abdallah yafi karfinku danshi da Allah yadogara,,,,,,,,,,

===============

Bayan wayan ta katse neh takira Amira sukasha hira,,,,,,,,,,
Wanda Har yasa amira yin mamaki,,,,,,,,,,,  Dan tadade rabon da taji tana farin ciki haka,,,,,,,,, beb wai wani albishir ne haka najiki cikin farinciki,,,,,,,, um akwae labarae dayawa kede daga school kibiyo gidanmu,,,,,,,,,,,,,,,
Kisha story,,,,,, OK beb ganinan zuwa,,,,,, toh saikin zo,,,,,,,,,,,,,,, sallama sukayi,,,,,,,,,,, sannan taci gaba da yin game awayanta (cooking fever) tanasan game din sosai Dan Yana ebeh Mata kewa,,,,,,,,,, kasancewar duk yayyun ta Wanda suka fito ciki daya sunyi aure,,,,,,,,,,,,,

Babban Yaron anty hajja ne yashigo Dan kimanin shekaru Sha daya,,,,,,,,,,,,, ummah wai kizo inji mamin mu tana falo,,,,,,,, toh cemata ganinan zuwa,,,,,,,,,,,,,,,,

To be continued

Ur's
Z33iiyyb3rw3r

BIBIYATA AKEYI

Bismillahirahmanirrahim

Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

.

6s Maryam where are u???? Ga page dinki ya danno❤😊

Dedicated to u Maryam bawa luv u so much

Page 11

*
Fitah tayi tanufi falo,,,,,, Dan amsa kiran da anty take Mata,,,,,,,,,,,
Yawwa,,,,,,,,, zoki tayani cire wannan kayan gwamma in cirewa kowa nasa tun yanzu nahuta,,,,,,,

A'a anty gaskiya kibari kawae ba yanxu ba Danni bawani aikin da zanyi nagaji yanzu fah nagama yin break fast,,,,,,,
Juyawa anty tayi da mamaki takalli mama,,,,,,,
Mama yanzu haka kike barin yarinyar nan tayita zuba San jiki san ranta,,,,,,,,, Idan tayi aure to waye zairinga Mata aiki,,,,,,,,
Turo baki gaba tayi Allah ni Sai indauki mai aiki,,,,,,,,, mai aiki??? Anty ta maimaita da mamaki dauke a fuskar ta,,,,,,,,
ehh aini ba yar aiki akakai masa ba,,,,,,,, saurin katseta Anty hajja tayi,,,,,,,
Kulll karna karaji kinyi zancen yar aiki Dan bakisan hatsarin dake dauke da daukan yar aiki bane,,,,,,,,,,
Kirufawa kanki asiri daga ke Sai mijinki aiki ba gagaranki zaiyi ba,,,,,
Kehh to in takaice miki,,,, wannan yar aikin ta gidansu,,,, ogan abbansu Mamii (yar Anty hajja

)aita aureshi daga hajiya tatafi umrah tadawo tasamu ya aure yar aiki,,,,,,,,

Tabb aikuwa da anyi tsiya Dan bazan yarda ba saidai yazaba,,,, koni ko itahh,,,,,,,,,, Kehh da Allah ai maganin Bari Kar afara ai sayya rabu dake Idan idansa ya rufe akanta,,,,,,,,,,

Yawwa dama maganan wannan najeeb din damuyi dake,,,,,,

Kinsan me ake nufi da soyayyar sirri,,,,,,,,,, saurin girgiza Kai tayi toshi zakuyi,,,,,,, dan kinsan Idan muna hadawa da addu'a dole kuma,,,,, muyi taka tsan tsan,,,,,,,,,,
Kiyi yanda zakiyi kihanshi zuwa gidannan koma meyene kuringa yinsa awaya ,,,,,,,,
Idanma yamatsu sai kun hadu,,,,,,,, to yafi ace kunhadu agidan fatima (anty maman amal ) dannasan,, bazata taba bari kiyi wani abinda bai dace ba ,,,,,, duk wani kula nasan zata bakishi,,,,,,,,,,,,

Kar ki yadda ki bar wata Baraka da agidannan za'a fahimci wani Abu,,,,,
Abari a kullum Akan bakida wani mai sonki,,,,,,, ko awaya yakiraki karki dauka acikin gidan,,,,,,,,,

Gyada Mata Kai kawai tayi,,,,,,,, tunani fal ranta shin Idan tace masa yaringa zuwa gidan anty bazai fahimci akwae wata matsala ba?????

Sallamar Amira ce ta katseta saurin Juyawa tayi tatafi da gudu ta rumgumeta tsamm,,,,,,,,,,
Karasa shiga sukayi ta tsugunna harkasa tagaida mama cikin fara'a mama ta amsa,,,,,, sannan tajuya tagaida antyy hajja duk da bawai tasanta bane Amma ta amsa Mata da sakin fuska,,,,,,,,,,,,

Cikin zumudi ta jata sukayi cikin daki,,,,,,,,,,
Suna shiga Amira tayi saurin yaye rufin gyalen dake kanta na Dan kwalin doguwar rigar dake jikinta ne tajefa Kan gado,,,,,,    beb bani infara sha plx,, barin inkawo miki ruwa,,,,,, beb kibar ruwannan kawai nakagu in farajin labarin,,,,,,,,,
Dawowa tayi ta zauna,,, beb badai angama lectures ba nop ba'agama ba kawai bazan iya jira bane Shiyasa,,
Toh ya skull?? beb banasan iskanci Idan kinsan bazaki baniba kawae intashi intafi,,,,,, tafada tana kokarin jawo veil dinta dake Kan gado,,,,,,  saurin janye gyalen tayi meye haka Dan Allah daga wasa,,,,, Toh kina wani jamin rai,,,,, sorry Toh nabari,,,,,

Labari tafara Bata tundaga lokacin da wayannan mutane suka fara *bibiyarata* Har zuwa haduwansu da najeeb,,,,,

shiru tayi sannan daga bisani tadaura dacewa beb shekara biyu kenan da lura danayi Suna *bibiyata* kuma na tabbata sunfi tsawon wannan shekarun kawai Dai lokacin Dana ankara ne,,,, sannan tadaura mata da mafarkin da tayi yau,,,,,,,,,,, beb wallahi tsoro nakeji,,,,,, kuma Allah inason najeeb sosai plx beb kiban shawara,,,,,,,,,,

Damamakinta tana dagowa saitaga Amira na hawaye,,,,,,, plx Amira kibar kukannan kinema min mafita,,,,,,

Bawata mafita dazanne ma miki Dan da kindaukeni Kamar yadda nadaukeki baxaki boyemin wannan al'amari ba,,,,,,,,,

Amma tunda hakane Naga alama Gara nayi baya dake,,,,,,,, Dan nalura zamanmu kaman takura miki nakeyi bakyason hakan,,,,,

Tana Gama fadin haka tazari jakanta da gyalanta da niyyar ficewa,,,,,, saurin shan gabanta tayi ta rumgumeta tsam,,,,,, tafara maganan cikin muryar kuka,,,,,,,,
Beb wallahi ba haka bane banason insaku cikin damuwa ne ko kinsan cewa ko mama akwai abinda na boye mata,,,,, banfada mata cewa ana *bibiyataba* plx NAYI NADAMA liittafin ( *Aisha* *Ali* *garkuwa* ) bazan kara boye miki damuwa taba,,,,,,

Dagota tayi sannan ta share Mata hawaye itama da share nata,,,,,, komawa sukayi suka zauna Akan gado,,,,,,,,,,,,

Kiyi hakuri Dan na tabbata WATA RANA littafin ( *Asmy* *b* *aliyu* ) Sai labari kinji beb,,,,,,,,,
Amma Ina tunanin gaskiya ba mugayen mutane bane,,,,,,,,,, Allah Dai yasa wani Dan mai mulki ne yaganmu yace yanaso yasa ake gadinmu,,,,,,,,,,, dukan wasa *hanna* takai mata,,,,,, kima daina tunanin haka kawai nabarsu a matsayin marassa aikin yi haka Dai suka ci gaba da tattaunawa Amma Amira ita Sam najeeb be kwanta mata bah,,,,,,,
Hankalinta yafi karkata da wayannan mutane,,,,, itama har takagu tasan suwaye ????

================

MG Abdullahi gabaki daya kwananan yarasa meyake damunsa,,,,,,,,,, yanaji akwai wani abunda yake shirin faruwa dashi,,,,,,,,,,,,,,,,,,,
Kullum zuciyarsa zafi take masa kamar Wanda ake huramai wuta kuma yarasa dalili,,,,,,,,,

Ummii ne tashigo tasameshi Ida nuwansa sunyi jawur gabaki daya tarasa Gane Kan dannata akwanakin nan,,,,,,,,,,
Ibnii takirashi dagaowa yayi ya kalleta,,,,,,,,,,,,,,,

To be continued

Ur's
_Z33yyb3rw3r_

BIBIYATA AKEYI

Bismillahirahmanirrahim

Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

Sadnaf nagode da addu'arki gareni!!!!!! Naji dadin fadan alkhairan da kikamun!!!!!!! Nagode luv u so much ❤😘

Page 12

*

Dagowa yayi ya kalleta da rinannun idanuwansa wanda suka sauya kala,,,,,,,,,,,  zama tayi kusa dashi tasa hannu tana shafa gashin kansa ahankali tafara magana,,,,,,,,,,,,,,
Ibnii,,, kadena sa damuwa aranka banajin dadi kullum Ina ganinka cikin tashin hankali shiru tayi sannan   taja wani gauron numfashi,,,,,,
Taci gaba da cewa,,
Kokasan duk lokacin da naganka cikin damuwa da kunar zuciya nake kwana,,,,,,,,,,,,
Kokasan damuwar ka tafi dagamin hankali fiye da damuwar kowa aduniyar nan,,,,,,,,
Dan Allah kacire duk wata damuwa aranka,,,,,,, duk da nasan duk wata damuwarka bazata wuce akan yarinyar nan ba,,,,,,,,,
Kasani inaji ajikina wannan yarinya taka ce,,,,,,,, sau da yawa nakanyi mafarkin,,,,,,,,
Naga jikanuna da wata yarinya wanda bantaba ganin fuskar taba ko yaushe fuskar ta bata bayyana agareni,,,,,,,,, Amma a kullum idan Ina mafarkin nakan kasance cikin kwanciyar hankali,,,,,, nakanji hankalina ya kwanta da wannan yarinya,,,,,,,,
Koda ace na farka nakan kasance cikin farin ciki a wannan rana,,,,,,,
Sai alokacin yaji hankalinsa yafara kwanciya Dan duk yanda yakai da bacin rai mahaifiyarsa tasan magan ganun da xatayi su kwantar masa da hankali.

Ahaka tayita lallashin sa harsanda zuciyar sa yaji tayi sanyi Dan ita kanta taga canji daga ga reshi ,,,,
Fuskar sa ta sake bakaman dazu ba,,,,,,,
Bata Fita adakin ba sanda ta tabbatar yaci abinci sannan itama,, tafita,,,,,,,

================

Saikusan yamma amira tabar gidansu *hanna*  Bata Fita ba sanda ta tabbatar ta Bata shawar wari masu amfani,,,, har anty hajja tazata tafi sanda tabata tsarabar turare da kayan makeup,,,,,,
Wanda takawowa *hanna*  ta ebi wasu aciki tabata Dan yarinyar ta kwanta Mata arai tanada tarbiya,,,,
Taji dadin kasance war *hanna* tare da amira Dan Taji irin shawar warin kirikin da tayi ta bawa

*_hanna_*

Har bakin titi taraka amira domin naiman abinda zai kaita gida ,,,,,,,,,, beb juya gefen dama,,,,,,,,,,,
daki gansu acikin wancan Yellow Range rober,,,,,,,,,
Saurin juyawa amira tayi aikuwa tarr tagansu Dan motar bame tinted bane,,,,,
Sanda takare musu kallo sannan tajuya ga *hanna*
Beb soldiers nefa,,,,,
Keh da'allah yaya akayi kika sani,,,,
Wallahi beb kiduba sarkokin wuyansu kigani,,,, oh oh baxan juya ba zasu gane muna kallonsu zasu zargi wani Abu,,,,,,,,,, ni tsoro bai taba barina na lura ba,,,,,, Allah beb inaji ajkina wani alkairi ne yake *bibiyar* rayuwarki amma kici gaba da addau'a Allah zai kawo Miki karshen matsalolinki basu dade awajan ba tasamu adaidaita,,,,,,,,, cike da kewar juna sukayi sallama tatsare adaidaita tatafi

Da dare yayi haka najeeb yakira ta suka sha hirarsu sasoai damashi mutum ne mai surutu sosai Sai wajan shabiyu 12:00pm da anty tagaji da surutu tanasan yin bacci,,,,,,, tayi ta Mata fada kafin tamasa sallama takashe wayan ta kwanta cike da kewar juna bacci yadaukesu,,,,,

Da sassafe kamar kullum tayi shirin makaranta tagaida babansu kafin ta wuce makaranta,,,,
Bayan sun fito daga lectures amira tace beb kirakani office din abba inkarbo aika hanna batayi Mata masu ba,,,,,,,,, Dan itama tagaji da zaman waje daya,,,,,,,
High court suka nufa Dan acan baban amira yake aiki,,,,, ,,, cike wajan yake da sojoji da kuma SS koba'a fada ba kasan manyan mutane ne acikin wajan,,,,,,,,,,,, ko mutum daya fa'a bari yashiga wajan,,,,,,,,

OK kinsande ni bazan koma ba,,,,, bakina kallanki da farin idoh ba ko balarabiya ce ke bazasu barki ki shiga ba,,,,,,,,,, dukan wasa amira takai mata banasan iskanci kawae muje ta baya mujira tafiyansu,,,,,,,,,,,
Bayan tangamemiyan court din suka nufa Bayan wani window dake cikin court din suka zauna wanda kana kallon window din kasan mai office din yanada matsayi Dan ya banbanta da duka windows din,,,,,

Zama sukayi awajan ba'afi minute da zamansu ba kunnuwansu yafara jiyo musu maganar dake kokarin tarwatsa kwakwal warsu gabaki daya zancen da'akeyi yafi karfin kwakwal war yara yan 19 year's

Gaskiya nayi iya bakin kokari na Amma abin yaci tura,,,, bamu da karfin dazamuja da mulkin sa,,,,,,,,,,,,
Bamuda karfin da zamu iya kwatan wannan shaidu ta karfi,,
Duk wani shaida tana hannunsa yanxu abinda yafi kawae muhakura,,,,,,,,,

Haba!!!!!!!! Haba!!!!!!!!!justice wani irin zance ne wannan Idan Har muka bari wannan takardu

suka futo,,,,,,,,
Da'samu babbar matsala

Dayan dake gefe ne yake zaune wanda daga ganin sa kasan babba ne akannan,,,,,,,,,,,,, yajuya ya kalli gefen sa wai shin chief ba'abinda zakayi akaine ambar karamin yaron da dukanmu mun haifeshi Yana caja mana Kai,,,,,,,,,, karfa ka manta munbarka a shugaban sojojin kasar nanne dan musamu abinda mukeso,,,,, shiru chief yayi sannan daga bisani yace,,,,,,,,,, karfa ku manta ba'a karkashina wannan yaro yake ba shifa sojan kasa da kasa ne,,,,,,,,,,, abu kadanne zai sameshi kasashe su mana gayya,,,,,,

Dayan wanda shi ba'abinda yace kawae ya daura daya akan daya Sai jijjiga kafa yakeyi saida kowa yagama sannan yace Idan kun shirya saina raba mana alhaki dan ni nadade da shirya abinyi,,,,,,,,,,,
Kallonsa sukayi duka da Alamun tambaya,,,,,,,,,,,,
Daga musu Kai yayi abinda zuciyoyinku suke tunanin shizan aikata kunsani duk wanda yashiga gonata kasheshi nakeyi ,,,,,,,

Amma yallaba!!!! Saurin katsesu yayi nasan tambayarku tayaya zan aikata kusani duk lokacin da nayi niyan abu saina aikatashi,,,,,,,,,,,,,
Amma yallabai kasan yanayin tsoro nakasan Dubai bakaman na kasar nan ba,,,,,,

Ai mutum daya ne zai aikata hakan bana bukatar taro,,,,,,,,,,,
Saurin karbe maganan chief yayi,,,,,,   ,
Mutum daya ne zai iya kasheshi????? Ya tambaya cikin tsananin mamaki

Kudaina min wasu tambayoyi kawae kusa aranku cewa nan da kwana biyu duk wata damuwar ku tagushe ko labarinta banaso asake dagowa,, yafadi haka tareda daurawa da murmushi irin na manya

Amira ne tayi karfin halin jan hannun *hanna*  harsuka Fita acikin wajen bbu wanda yalura dasu,,,,,,,,
Abin hawa amira tatsara musu *hanna*  kanma saida taturata ciki sannan suka tafi kaitsaye gidansu amira suka wuce

Kwankwasawa amira tayi mai gadi yabude musu kofa,,,,,,,, haka taringa jan hannunta kamar wata tababbiya

Kaitsaye part dinta suka wuce kasan cewar babansu Amira yafi babansu *hanna*  dukiya sosai shiyasa kowa keda part dinsa,,,,,,,,,,,,,,,,,,
Kuma yaransa biyar ne kacal da Mata daya uku maza biyu Mata macen shekaranta biyu daaure

Suna shiga daki tayi sauri tasa ki sannan tajuya zuwa ga *hanna* dake tsaye kaman gawa *hanna* *hanna* takirata ta jijigata Amma shiru daga hannu tayi tabata lafiyayyan mari Wanda

ba shiri tadawo hayyacinta (kusan cewa Koda amakaranta kike kawarki tanemi kirakata wani waje toh kikira gida kifada kafin Dan kikan iya fadawa halaka su iyaye sunbar yaayansu akan suna makaranta) Dan gashi kusan haka tafaru da *hanna*

*Hanna* dan Allah mubar Wanda magana Dan fitowarta kamar rasa rayukanmu ne mu binneta kinji daga Mata Kai kawai tayi ammaa tasamu kanta da addu'ar Allah yasa kar suyi nasara akansa

To be continued

_Ur's_
_Z33yyb3rw3r_

BIBIYATA AKEYI

Bismillahirahmanirrahim

Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

_Asmy_ _b_ _Aliyu_
Nagode da addu'arki ki gareni Allah yabar zumunci

Page 13

*

Haka kawai ta tsinci kanta da masa addu'ar kariya daga sharrin su

Haka amira tayita kwantar Mata da hankali Dan tasan Abu kadan ke dagawa kawar tata hankali gata dasa damuwa,,,,,,,, bata barta ba sanda taga tadan sake!!!!!! ,,,,,,,
Ni wallahi amira abinda yadaga mun hankali Sai kace abinda yake faruwa a film bantaba dauka yana faruwa a zahiri ba,,,,,,,,
Yanzu deh mubar wannan maganan barin duba mana abinda zamuci Fita tayi zuwa kitchen Dan dafa musu indomie Dan shi yafi komai sauki,,,,,,,,

================

Ina labarin najeeb ne??????

Yana katse wayan ya nufi falo a guje Dan fadawa mahaifinsu yaje nema masa aure,,,,,,,,,

Turus yayi tundaga bakin kofan falon zumudi yasa gabaki daya ya manta da babansu yayi tafiya,,,,,,

Murmushi yayi tareda sosa keyarsa  yajuya Amma ya kudirta duk randa akace dad yadawo maganar da zaifara masa kenan,,,,

Haka yashare sukayi tacin soyayya awaya shida sweety dinsa duk da rashin ganinta yana damunsa Amma,,,,, yakudurta gobe saiya sata a idanunsa,,,,,,,,,

Babban abinda ke damunsa dukda a'ido tana nuna masa tana sansa Amma abaki bata taba furta masa ba
Ya alakanta Hakan da kunyan da take dashi

Duk bata kasance bafula tana ba,,,,,
amma tanada matukar kunya,,,,,,,,,,,,, ita cikakkiyar bahaushiya ce Wanda kana kallonta zakaga cikar zatinta na hausawa,,,,,,,
Da asalin kyawu irinna hausawa ya bayyana ajikinta

================

Wayan da take gefen sane ta dauki ruri!!!!,,,,,, Koda ba'a fada ba yasan wayan da ke kiransa,,,
Wani irin faduwar gaba ne yake damunsa kuma yarasa dalili,,,,,,,,,,,,,,,,,,,,,
Hakanne yasa kallon yanayinsa captain Ahmad yafita daga office din zaiba shi privacy,,,,,
Dan MG Idan yana cikin wani yanayi baya bukatar kowa kusa sanin halinsa ne yasa Idan suna tare dashi suka ganshi a wannan yanayi suke bashi waje shi kadai??????

Captain Ahmad yazo Fita ya umurceshi da ya ajiye masa phone dinsa guda biyu,,
Da Wanda mahaifinsa ke samunsa da kuma Wanda yake talakawa masu complain suke samun sa,,,,,,,,
Sai akayi rashin sa'a dake phones din iri daya ne  ya'ajiye  Wanda manyan mutane suke nemansa,,,,
Ringing din da wayarsa keyi ne ya tabbatar masa da ba phone din dayace a ajiye aka ajiye bah,,,,,

Tsaki yaja sanda wayan tayi rurin ta tagaji bai dauka ba,,,,,,,,,
Sai da aka sake kirane sannan cikin nutsuwa yadauki phone din tare da picking din call din
Dan kiran daga mr presdent na Nigeria ne,,,,,,
Gaisawa sukayi cikin mutun tawa sannan yake fada masa sunada meeting da zasuyi a Dubai a burj al_arab kuma suna gayyatarsa tareda bukatan matakan tsoro

Haka kawae ya tsinci kansa da rashin son zuwa wajen Amma zaije kodan kare lafiyar al'umma

================

Sai karfe uku sannan amira takira driver yakaisu taraka *_hanna_* gida
Suka fito sannan sukayiwa Ammin su amira sallama har kofar gida suka kaita,,   sannan suka juya

Bayan shigar ta gida tayita kokari ta danne damuwarta, dan ko mama bata fahimta ba
Tun karfe tara najeeb yakira ta Dan hatta mance da abunda yafaru da rana hira sukasha sosai daga nan Sai kusan 10:30 sukayi sallama Dan anty hajja ta hanata wayan dare sosae.

Wayanta tasauka tahau bincike a iya bincikenta bata samu wata masaniya akan wannan mutumin da akeson kashewa ba,,, Haka bacci yadauketa da taradda din wayannan mutane

Baccine mai cike da mafarkai kala kala,,,,
Akarshe ne tayi mafarkin wannan mutumi wanda awancen lokacin tayi mafarki ya harbi najeeb,,,,
Ya gurfana agabanta yana kuka amma takasa jin abinda yake fada
Ahaka tafarka cikin tsoro Amma hankalinta baikai na wancen karan tashi ba waigawa gefe tayi taga anty hajja nata sharar bacci itada yaranta Mata biyu Aisha (mammii) mai sunan mama Sai halima Wanda taci sunan yayar babanta
Sauka tayi tanufi toilet tadauro al'wala salla taringa yi tana neman zabin Allah saikusan uku bacci yadauketa akan sallayan

Kiran sallan farko ne yatasheta tatashi takara dauro al'wala taga batar da sallah
Sannan tatashi anty Dan itama ta gabatar da nata sallan,,,,,,, koma wa tayi ta kwanta nan da nan wani bacci mai dadin gaske yayi awon gaba da ita

Kamar a afarki taringa jin muryarsa a cikin bacci komadda idanuwanta takarayi tarufe can kaman Wanda tatuno wani tayi saurin mikewa tayi cikin falo aguje tana ihu,,,,,

To be continued

_Ur's_
_Z33yyb3rw3r_

BIBIYATA AKEYI

Bismillahirahmanirrahim

Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

Page 14

*

Falo tayi da gudu, tana zuwa kuma tatsaya da mamaki dauke a fuskar ta,,,,,,,,,
Juyowa sukayi suka kalketa,,,,,,,,
Aikaman jira takeyi takarasa dagudu ta rungumeta,,,,
Cikin farinciki itama ta rungumeta,,,,,,,,
Muryar sane ta daki dodon kunnu wansu,,,
Oh ni tunda ba'a murnar ganina Sai in koma saurin saketa tayi ta riko hannunsa,,,,,,,
Yaya ba haka bane fah,,,, rausayar da kansa yayi!!!!!!!!
Toh meye Idan ba haka bah!!!!!!!
Kankantar da murya tayi,,,, yaya please OK ya wuce,,,,,,
Saurin sakinsa tayi tunowa da tayi bafah muharraminta bane,,,,,,!!!!!
Ankuma yafada acikin zuciyar sa,,,,,,,,,,,
Zama sukayi nan tadi ya barke tsakanin yan uwan da suka dade basuga juna bah,,,,,,,
Hira sukeyi sosai har ma ta manta tanada lecture's
Can wayan ta ta dauki ruri,,,,,,
Tana kallan mai kiran saida gabanta ya fadi,,,,,,
Alokacin ta tuno tanada lecture's
Saurin daukan wayan tayi,,,,,,,,,,,
Beb wai me kikeyi a gida ne tun 9 fa muka shiga lecture's kuma zuwa 12 zaiyi test ai batasan lokacin da taduro akan kujera ba,,,,,,
Daki tawuce tashiga wanka batafi 15minute ba tafuto,,,,,,
Shiryawa tayi cikin blue da red din atampha,,,,,
Bakaramin kyau tayi ba sannan ta dauko ribbom tayi parking kanta,,,, duk da gashin kanta bai cika tsayi ba Amma Idan tayi kitso yakankai kafadunta, cikan da kanta ke dashi ne yakan hana kallan tsayinsa sosai,,,,,,
Cikar da gashin ke dashi ne yasa da tayi parking yataso kamar Wanda tasa ribbom na acuci,,,,,,,,,,,,,
Dankwali tadaura sannan tadauko khimar dinta dogo sosai ta daura,,,
Sannan tafesa turare mai sanyin kamshi wanda saika matsa kusa da ita kafin kaji kamshin,,,,,,,,,
Takal minta ta dauko plat dake tanada Dan tsayi yasa tayi dass dass gwanin sha'awa,,,,,,,

Futowa tayi dauke da side back dinta mai tsadan ba jebbu ba,,,,,,,
Dan mama da yayunta na kokari wajen sayamata kayayyaki masu tsada,,,,,
Tsugunawa tayi tasauko phone dinta da tabari akan kujera,,,,,,
Juyawa tayi ta kalli kujeran da hameedah ke zaune,,,,, subhanallah wani irin kama naga sunayi da wannan yarinyar wanda bazasu wuce sa'anni ba Sai tsiran da bazaifi na months ba,,,,,

Tabbas suna kama saidai bambamcin da baza'a rasa ba,,,,,,,,,
6s muje koh,,,,,,
Muje inahh???? Skull mana kinsan ai tunda kinzo toh tare zamu,,,,,, Dan bawani uzurirrikan da zandauka,,,,,

Tashi tayi suka dugun zuma kitchen dan yiwa mama Sallama,,,,,, me nake gani badai wani wajen daku je ba,,,,
*_Hanna_* tayi saurin karfe zancen,,,,,,
Ehh mama school zamuje,,,!!!! Amma ai kyabarta tahuta yanxu fa isowarsu daga kano,,,,,
Ko ruwa batshaba balle wani abinci,,,,,
Zamuci a makaranta tafada tareda jan hannun hameedah,,!!!!!!

Saikusan 11 suka isa makarantar,,,,,
kiran amira tayi sukaje yanda take suka sameta,,,,,
Gaskiya Beb kuna kama da 6s dinki sosai,,,,
Harya wuce yanda kike fada,,,, saidai tafiki kyau tafada tareda kashe Mata idoh daya dukan wasa *hanna* takai Mata kinfiye sa idoh kekam kinji jiki,,,,,,
Kyaleta kawai dannasan tafada ne kawai kowa yace kinfini kyau
Dan idanuwanki yafi nawa girma kuma kinfini dogon hanci
Cewar hameedah!!!!!!!
Dariya sukasa kede kawai kin tsorata da wayan nan idanuwan tanne amma bawani kyawun da ta fiki,,,,,

Beb bamu karya bafa,,,, lallai bakida hankali kikabar bakuwa da yunwa harara ta galla Mata wacece bakuwar,,,,,,,
Ninaga alama in muka biyeki Sai munrasa test dinnan,,,,,
Uhm kawai amira tace sannan suka nufi hanyan _barhakkk_ dake gefen hostels na school din danyin breakfast,,,

Sanda sukeyi ordering kafin suka zaune tadi sukeyi wanda zaka rantse amira sundade da sanin juna da hameedah!!!!!!!!!! Dan duk su ukun bbu baya wajen surutu!!!!!!
Wayan *hanna* ce tadauki ruri jin kidan yasa tasan wa yake kira Dan ringing dinsa dabanne,,,,,
Daukan wayan tayi,,,, sannan tajuya gefe da gefe aikuwa caraff idanuwanta ya sauka akansu,,,,,,,,,,
Saurin juyawa tayi sannan takara wayar a kunnenta,,,,
Hellow°°°°sweety
Na'am kina school ne????? Eh!!!!! Ina zuwa yanxu kijirani
Haka kawai ta tsinci kanta da faduwar gaba!!!!!! No plx karkazo,,,,, karnazo???? Dalili?????
Shiru tayi tafara kame kame " """"hmm dama nasani baki da wani abinda zakice nadade da fahimtar bakya sona nikadai nake hauka akanki,,,,,,,,
Tabbas kina shirin jefani wani hali Dan har ikika gujeni mutuwa zanyi plz karki barni nizan koya Miki yanda zaki soni Amma plx karki rabu dani yafada cikin sarkewar murya,,,,,,

Wani irin tausayinsa da sansa ne suka kara ninkuwa cikin zuciyar ta!!!!!
Mekaki fadi haka kasan Nima bazan iya rabuwa dakai ba
To meyasa bakyason muhadu????? Kijirani agidan anty Idan nafito a lecture's zanzo,,,,,,, OK bye luv u saurin katse wayan tayi dan bazata iya bashi amsa ba,,, tadaga wayan akunnenta tana murmushi,,,,,

Zuba Mata idoh sukayi kaman wanda tayi wani abun,,,,, meye hakan da'allah kun wani tsareni da idoh kaman tsoffin mayu,,,,, ko gizau basuyi ba sukaci gaba da kallanta hameedah harda karawa da tagumi,,,,,,,,
Amma cikin ranta wani dadi takeji na ganin yar uwarta tasamu masoyi,,,,,,,,,,,,,,,,
Tsaki taja sannan taci gaba dacin abincinta,,,,,,,,

Waye shii?? Cewar hameedah najeeb tabata amsa atakaice yatsine fuska amira tayi ""
""sannan tace zaiyi yabari afusace da dago bangane me kike nufii ba cikin bacin rai!!!!!!!!!!

To be continued

Ur's
z33yyb3rw3r

BIBIYATA AKEYI

Bismillahirahmanirrahim

Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

This page is Dedicated to u___anty rash wish u success in your exams

Page 15

*

Ni na tabbata akwae wanda yarigashi kuma haka kawai zaizo yayiwa wani wucel aiba haka akeyiba
Cikin bacin rai *hanna* tace toh saiki mutu Amma aure kam na auri najeeb angama saikuje kuyita haukanku keda su
Tajuya gun waynnan mutanen ta maka musu harara,,,,,
Jan jakarta tayi tana shirin barin wajen
Saurin riketa hameedah tayi sannan takalli amira ku fahimtar dani mana har yanzu bawai nagane yanda kuka dosa bane

Juyar da kanta *hanna* tayi tarike kugu tana karkada karkada jikinta ida adole ranta ya baci
Dakyar suka shawo kanta ta zauna Dan Sanda amira tabada hakuri tukunna,,,,,,,,,,,,,,,,
Labari suka fara bawa hameedah ba abinda suka boye Mata tass suka kwashe komai suka

fada Mata,,,,,
Ai nan da nan idanuwan ta sukayi jawur,,,,, Kai Amma wannan Ammah nan anyi tsinanniya na tabbata da umma(mamar hameeda) tasani Sai ta Mata tass tass ai tasanta
Ke matar wan mahaifinki kike tsinewa,,,, ai wallahi Sai na Mata tsiya tunda ba yanxu zan tafi ba ai zata gane kuranta,,,,,,, adai Mata sassauci sukace tareda tuntsirewa da dariya,,,,,,
Amma kinsan me ni Allah banga laifin amira ba Nima inaji kaman akwae wani alkairi a tattare da waynnan mutanen tafada tareda kallonsu ta kasan idoh,,,,,
Harara *hanna* ta galla Mata da'allah malama rufa mana bakii!!!!!
Amma kinsan me kemafa banga laifinki na zurfafa ason najeeb ba danna tabbata gayan yayi danke ko akaya baki zaben jebbu!!!!!!

Kallan wayanta tayi subhanallah ke time din test yawuce,,,,
Wani test kum``````saurin rufe bakinta tayi da tafukan hannunta tunowa da tayi karyar data shirga mata dazu

Kallo mai cike da tuhuma *hanna* tayi mata,,,,,,,
Sorry Beb Allah narasa yadda zanyi kizo Skull ne nadau zancen jiyannane yahanaki zuwa shiyasa,,,
Dakiyi ma yafi haka,,,, ita kuwa hameedah banda dariya ba abinda take musu

Fita sukayi ta niyyar wucewa gidan anty  ai kuwa acan suka sami najeeb Dan zumudin ganinta bayan sungaisa da najeeb dinne,,,,,,
Suka shige suka barsu su kadai itakuwa anty murnar ganin yar uwarta hameedah yasa ta manta dasu,,,,,

Soyayya sukasha kaman bbu gobe kamar karsu rabu saidai duk wani Soyayyar su sukanyi ta cikin sanin yaka mata Dan basu taba goce hanya duk wani abinda addini yahana basa yinshi Domin  albarka Soyayyar suke nema,,,,,,,,

================

Dubai

Kasar dubai aranar yau tatashi cikin wani irin cikowar mutane sakamokon taron kasa da za'ayi gobe MG kokadan baysamu lokacin kansa ba danko lokacin cin abinci bai samu ba sakamokon yadda garin yake makill da jama'a yanata kokarin yadda zaikare lafiyan al'umma
Garin acike yake Dan manya manya sunfara suka duk wani waje da kuka sani nacikin Kasar Dubai acike yake Dan bakinmu na Nigeria  a wani katon estate yasauke a _emarr_ _sidra_ _hills_ _eatate_
Inda sarakunan larabawa kuwa sunsha karrama ansauesu a _arabella_ _town_ _houses_
Wanda wasu da yawancin su sunje ne Dan yawan bude idoh Dan dubai kasaace Wanda taci gaba sosai afadin duniya

Shirya sojojinsa kawai yakeyi inda bayaso asamu wata matsala awannan taron
Bakin Nigeria sun isoh Wanda suka hada da manya manyan yan shiyasa aciki kuwa hadda wanda suke neman rayuwarsa,,,,, shikuwa yananan yana shirin kare tasu rayuwar

Sanda yaje airport yataresu yasada su da masaukin su sannan yawuce zuwa wani wajan
Dan taran wasu shuwa gabannin
Dan kowani shugaba burinsa daya yakaaance MG yana daya daga cikin masu taryan sa awannan lokaci

Har kusan tsakiyan dare MG baisamu hutu ba dakyar su captain Ahmad sika yakiceshi Dan yasa mu hutu,,,,,

Futa sukayi suka shirya masa motoci 9 hadu na bayansa hadu na gaban sa Sai kuma tashi atsakiya,,,,,,,
Captain Ahmed ne yake tuki gefensa kuma daniel ne Wanda Shima MG ya yarda dashi sosai
Dan yanada rikon gaskiya shiyasa Har yabarshi yashiga jikinsa sosai

Koda suka isa gida daniel ne yayi saurin fitiowa ya bude masa kofa fita yayi cikin takun sa nakasaita Wanda ko ba'afada ba kasan jinin sarauta ne

Kai tsaye cikin gidan yanufa,,,
Kowani soldier yazauna awajan tsayuwar sa captain Ahmed da daniel ne suka rufa masa baya hannu yadaga musu alamun su tsaya sannan yacewa captain Ahmed yabiyoshi akwae sakon dayakeson bashi bbu musu daniel yatsaya shikuwa captain ahmad yabishi abaya Dan karban sakon

Bayan shigansu ne daniel ya cije libs yarasa me captain Ahmed yafishi da MG yake nuna bamban ci atsakaninsu
Kuma hakan Yana matukar yimasa zafi aransa
Amma ya alakanta hakan da bambam cin addini dasuke

Abinda be saniba shine duk cikin sojojin MG yafiji da Ahmed duk da yafishi agirme dakuma matsayi hakan bai hanashi zama yayi shawara da, Captain Ahmed ba

Tunda yashiga yariga da yasan ummii tayi bacci to baibi takanta ba,,,,,,,,,, abinda baisaniba shine ko karfe nawa zekai nadare ummii,,,, saitaga dawowanshi dake iya runtsawa sake labulen dake hannun ta tayi sannan taje ta kwanta,,,, koba komai ranta yayi dadi naganinsa cikin kwanciyar hankali,,,,, bandaki yawuce ya watsa ruwa baifi mintuna kadan da kwaciya ba bacci yadaukeshi,,,,,,,,,

Asuban fari ya farka wani irin mummunan faduwan gaba yatashi da ita Wanda yarasa dalili wanka yayi ya shirya cikin kakinsaa mai fitar da ainihin kyawunsa da cikar zatinsa

Dakin ummii yawuce yasameta tana bacci baiso tada ita ba hakan yasa yajuya yatafi Amma irin wannan taron yaso ace yafita da addu'ar mahaifiya akansa,,,,
Sanda suka tsaya amasallaci musulmen cikin suka gabatar da sallah kafin suka nufi burj al'arab hotel din da za'a gabatar da taron

To be continued

Ur's
Z33yyb3rw3r

BIBIYATA AKEYI

Bismillahirahmanirrahim

Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

_
_This_ _page_ _is_ _Dedicated_ to _u_ :: *hajja* *_ceh_* * _kece * * _mutum_ * *ta* farko _datafara_ _bani_ _kwarin_ _guiwan_ _rubutun_ _littafi_ _tanks_ _alot_ _I_ _luv_ u _so_ _much__

Page 16

*

Sai wajan karfe uku 3:00 sannan suka bar gidan anty,,,,,,
Amira ta wuce gida suma suka wuce gida,,,,,,,,
Bayan isansu gida sunyi sallar la'asar wani sabon hira suka dasa
Kai sis wallahi najeeb ya hadu wani farr tayi da idoh duk farin ciki ya cikata anyabi abin sonta
Allah koh tace,,,, eh mana kunyi bala'in da cewa
Saleem ne yashigo kanin *hanna* anty hameedah wai kizo inji Ammah yafada yana kallon wayarta,,,,,,,,,
Kai meye kawani zubawa wayarta ido da'alllah fice kabawa mutane waje,,,,,,
Kai sis kinfiya takura Ina ruwanki kokuma wayarki ya kallah zonan Saleem karba,,,,,,
Zuwa yayi ya tsaya medakayi da phone din sosa keyarsa yayl game yafada atakaice karba katafi,,,,, itakuwa *hanna* murmushin dakisan waye Saleem tabita dashi,,,,,,,,

Ke wai ba Ammah ne kekiran kiba kikatsaya yatsine fuska tayi kyaleta kawai bawani akyaleta tashi muje,,,,,,,,

Nasan wani abin take nema Sai kiji dadin bata amsa,,,,,,,,,,,,
Mikewa tayi suka nufi dakin Ammah
Suna shiga suka sameta itada yaranta rabi'ah da hafsat suna zaune
Afalo Sallama sukayi basusami amsawa hakan baida mesu ba suka zauna,,,,,,,,,,,
Juyowa tayi ta kallesu gidan ubanki ne nan dazaki isoh tun safe bakizo kin gaishe niba,,,,,,
Maciya amana ko yanzu kuma dawani cin amana uwartaki ta aikoki,,,,,,

Ko uwarki bata isa tazonan gidan,,,,, tanuna batasan inanan ba,,,,,
Balle ke karamar marar kunya,,,,,,,
Iya bacin rai ransu yakai kololuwa wajan baci,,,,,
Hameedah ce cikin bacin rai tabude baki zatai magana s damke hannun ta *_hanna_* tayi da karfi kallon ta tayi ta girgiza Mata kayi kawar da kanta tayi cikin takaici na hanata ramawa da *hanna* tayi

Juyawa tayi ta fuskanci Amma kingama akwai Abu me mahimmanci da mukeyi tafada hadeda wani murmushi wanda Ammah takasa tantance namiye shi,,,,,,,,
Sake baki tayi Dan uwarki aibake nakira ba,,,,,
Rashin kunyan ki haryakai ki Har yakai agaban idanuwamu kiyiwa mahaifiyar mu raini,,,
Hafsat ce tatashi da niyyar dukanta,,,
Ammah tahanata kull karki tabata kibarni da uwarta zanyi ni,
Jan hannun hameedah tayi wadda ga baki daya ji take kaman ta fashe tsabar bakin ciki,,,,,,,,,
Janta tayi Har sunzo bakin kofa Ammah tace shegiya mai bakin jini,,,,,,
Saurin tura hameedah waje tayi tadawo cikin dakin wani kallon kaskanci tabi hafsa dashi,,
Wato kece Har zaki dakeni ko tabani wallahi saina miki shegen duka,,,
Sannan tajuya gun Ammah da gabaki daya al'ajabi yahanata cewa komai,,,,,,
Idan Har zaki iya duban idona kice mun mai bakin jini kamata yayi ki fara aurar da nagabanki wanda duk cikinsu bbu wacce bata bani sama da shekara ba tukunna kisamo bakin gori,,,,,,,,,

Tana fadin Haka tajuya tafice tabarsu cikin jimami
Samin hameedah tayi tsaye tana jiranta a bakin kofa,,, dayake taso biyota Amma takulle kofan,,

Murmushi tabita dashi saurin kawar da kanta tayi tafice fuuuuuuu
Binta *hanna*  tayi abaya Har suka shiga dakin mama ganinsu Ahaka yasa anty takirasu tana tambayarsu,,,,,,,

 *Hanna* taso boye Mata amma hameedah takwashe komai yafada mata ran anty yabaci Amma Sai ta danne kawai Dan yanada kyau tun yanzu afara koya musu yin hakuri kafin auransu

Ahaka yaya jalal yashigo yasamesu,
Kallon *hanna* yayi wai Ina kuka shiga ne kam tun safe,,,, gidan anty fa mukaje,,, shine ba gayyata yafada tareda zama kan kujera,,,,, yaya daga makaranta fa muka wuce,,,,, Haka suka zauna sukayi ta tadi Dan Har sunmanta da bakin cikin da Ammah ta durka musu

Sallar magrib ne ta tashe su sukayi sallar suka dawo akasake sabon hira,,,,,,,,,,,,,
Saikusan 9:00 najeeb yakirata suka sha soyayyarsu sanda tafara jin bacci kafin sukayi Sallama takwanta Dan hameedah ta dade da bacci,,,,,,,,,,,,
Irin mafarkin jiya data karayi ne yatashe ta,,,,
Tarasa me wannan mutumi yake nema da take kallonsa gurfane agabanta,,,,,,,,

Datarasa mafita kawae ta dauro alwala tagiba dayin nafila Har bacci yadauketa,,,,,,,,,,
Har ta makara a sallar asubahi Sai wajen 6:30 ta tashi tayi sallah
Tunda ta farka ta tsinci kanta cikin wata irin matsanan ciyar faduwar gaba
Gabaki daya Tanaji kamar akwai wani abunda ke damunta amma tayi duk iya tunanin ta tarasa dalilin damuwar tata

================

Taro yayi iya Taro Dan duk wani manyan duniyar nan sun halacci wannan Taro
Amfara gudanar da taro komai na tafiya daidai Ina tawajan MG haryanzu faduwar gabansa tsananta takeyi

Duk wani tsaro daya kamata awajan antanadar
Inda layin da MG yake zaune layin manyan mutane ne wayar sace tadauki ruri ganin yanda wajan yake a cike yasa yatashi dan amsa wayar, mahaifinsa ne yake kira yasa bazai iya kindauka ba

Kokarin fita daga wajan dayake yake niyyar yi soldiers suka taso Dan bin bayansa daga musu hannu yayi alamun su koma,,,
Bamusu suka tsaya inda captain Ahmed yabi bayansa,,,,,,,

To be continued

Ur's
Z33yyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirahmanirrahim_

Writting by
© _zaynab bawa_
_( z33yyb3rw3r)_

*_Edited_* *_by_* _KSA_ _precious_ _Hajjah_ ce

*Dedicated to*
_*Ummi  Aysha* (haske Writter) novel d'in ki na mijina sirrina yayi sosai Allah ya kara basira da zakin hannu_

Page *17*

*
Fita yayi cikin sauri dan amsa wayar da mahaifin sa ke kira.
Ga baki d'ayan sojojin suka bi bayan sa cikin sauri. d'aga musu hannu yayi alamun su koma.
Bbu musu suka jah suka tsaya a inda suke.
Captain Ahmed ne ya bi bayan sa
Dan ya san hatsari ne barin shi yafi ta shi daya.

Amsa wayar ya yi sannan suka gai sa. tambayar sa ya keyi da cewa.
Yareemah...!!! Kana lafiya?" cikin murya mai cike da da muwa yace "lapya na klau abba, wani abin ne ya faru?"
A'a bbu babu komai ka kula da kan ka kaji ko?
Kuma na kira mahaifiyar ka tace mun bata san lokacin fitar kaba.
Ya kama ta Karin ga sanar da ita, ai addu'ar mahaifiyar ma yana da Amfani kaji ni?"

Yareemah yace "In sha Allah."

"To Allah ya kare ka daga sharrin ko wani irin halitta."
Ameen yace sannan ya kashe kiran.

Juya wa yayi zai tafi Sai ya ga daniel tsaye yana murmushi tare da sosa kyeya kaman Wanda yake neman wani alfarma.
Kallon sa yayi sannan ya kawar da Kai yana kokarin mai da wayar sa cikin aljihu.

"Sir MG please ina son magana da kai."
Kallon sa yayi tare da cewa "Ehem! ina jin ka."

Yace "Sir Idan ba zaka damu ba mudan matsa tacan? ya nuna wani waje da bbu mutane ta cikin hotel d'in.

Kallon sa yayi batare da wani tunani a ransa ba ya nufi wajan.
Sanda suka isah MG ya d'an jin gina ya lumshe idanuwan sa ba tare da ya kalle shi ba yace "Kai nake sauraro."

Duk wani abin da yake faruwa akan idon captain Ahmed ne.
Amma da yake Shima ba abin da ya kawo a ransa yasa ya tsaya nesa dasu sosai.
Ganin daniel na shirin ciro Abu daga cikin aljihun sa ne kuma ya nada tabbacin bindiga ne ya

sashi fara shan jinin jikin sa.
Ga shi Kuma idon MG a rufe yake. Da sauri ya fara kara sawa wajan da suke a tsaye.

Amma dake da rata a tsaka nin su kafin yayi rabi harya karasa fitowa da bindigan. magana ya farayi cikin garaji Wanda hakan ne yayi sanadin bud'e idon MG amma kafin ya bud'e ido Sai sau kan harbi kawai yaji a gefen cikin sa.

Karar har binne ya jawo hankalin jami'an tsaron da ke wajan.
Bud'e idanuwan sa tarr yayi ya zuba su akan na daniel. Wanda ke wani irin dariyar mugun ta. A lokacin Idan kaga MG baza ayi tsammanin a kwai harbi a jikin sa ba. Sai dai Idan ka lura da yadda jinin kebin jikn sa.
Wani irin huci yake fita da shi Wanda duk d'auri yar mutum a wannan lokaci Idan ya gan shi sai ya razana. Dan idanuwan sa sun sauya kala sunyi jawur.

Wani irin shaqa ya kai wa daniel. Kan wani Dan lokaci idanun daniel ya fara zazza rowa. ganin yana shirin hallaka shine ya sa ya kara d'aga bindigan ya sake masa a gefen kirjin sa.
Ganin Haka yasa captain Ahmed cira bindigan sa Kan ya 'iso ya sakewa daniel ita a goshi.

A lokacin jami'an tsaro suka isoh wajan a kayi saurin rirreke MG da jikin sa gaba ki d'aya ya 6aci da jini. captain Ahmed ne ya kara so ya tallafe shi.

Ga baki d'aya gun ya cika da sojoji. kai kace wani taron sojoji akayi. ga baki d'aya hankulan su a tashe yake Ganin shugaban su cikin wannan ya nayin.

Motar tai makon gaggawa ne tazo in da yan jaridu sun cika wajan makil. kowa koka rin d'aukan abun da ke faruwa ya keyi.
Nan da nan a kayi dashi babban asibiti dake cikin dubai. inda moto cin sojojin dake gaban su da Wanda ke bayan su sun Kai akalla mota sha biyu.

Kai tsaye *_(mass general hospital bostoon International)_* aka nufa da shi.
Manya man yan likitoci ne suka shiga theatre dashi. kokari su keyi na ganin sun ciro harsashan dake cikin jikin sa.

Ummii ne zaune a falo ita da wata 'yar aikin ta tana matsa Mata kafa. ji tayi ga baki d'aya ba ta cikin nutsuwar ta.
Hakan yasa ta umarci d'aya 'yar aikin da take yan ka mata friut data kunna Mata TV. Hankalin ta baya Kan tv d'in Amma labaran da taji a nayi ne yayi saurin jawo hankalinta wajan.

Idan ba kunnuwan ta karya suka Mata ba, taji a na cewa an harbi MG Abdullahi Abdul-Aziz lamido. Wanda a halin yanxu ba'a san yana raye koh yana maceh ba.
Hawaye ne ya fara bin fustan ta bbu abin da take nana tawa Sai inna lillahi wa'innah ilaihi raji'un.! Wanda hakan ne yaja hankalin yan aikin ta suma ju yawa su kayi Dan kallon abin da ya razana ta. ihu d'aya daga cikin su Wanda ya jawo hankalin sojojin dake bakin gate da cikin

harabar gidan shigowa.

A razene suka yiyo cikin gidan, dan ganin abun da yake faruwa. Kan Wanda tasa hanu akayi tana kwalla ihu su kayi suna tambayar ta abunda ya faru dan basu lura da ummi data dade da zama mutum mutumi ba a kwance. Wanda bata gane komai a lokacin. TV ta nuna musu da ga baki daya hankalin su ya Kai kololuwa wajan tashi.
Ihu da sambatun sojojin ne ya dawo da Ummii han kalin ta tashi cikin tashin hankali ta musu umarni da su kaita a sibitin. Dan kuka yaki zuwa Mata gani ta keyi kaman karya ne.

Fita suka yi Dan rakata asibitin motoci uku ne suka cika da sojojin Sai Wanda Ummii take a cikin d'aya. Kai tsaye asibitin suka nufa dan ganin abun da yake waka na....

To be continued

_Ur's_
_Z33yyb3rw3r_

*BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

*Dedicated* *to* *_ummi_* *_aysha_* (haske Writter )

Page 18

*
Wata irin faduwar gaba ne yake damunta ayau, kuma tarasa dalili.
Hakanne yasa ko waje batayi sha'awan fita ba.
kasan cewar ranar asabar ce, bbu lectures, zama tayi kawai tana tunanin dalilin wannan faduwar gaban tata
Can zancen mutanen na shekaran jiya yafado Mata.
Addu'a tasamu kanta da kara yimasa na Allah yakareshi.
Dakyar taya kice damuwaar aranta, domin kar hameeda ta fahimci wani Abu.

Cigaba sukayi da hidimominsu kamar bbu abinda yake damunta,
Amma Can cikin zuciyarta damuwa ce sosai.
Kusan karfe shadaya 11:00
Tashiga falon babansu dake yana gida bbu office.

Da Sallama Tashiga ya amsa Mata cikin farin ciki,
Nadauka yar tawa yau baza tazo taya abbanta hira bane, saboda akwai yar uwarta kusa da itah.

Murmushi tayi sannan takarasa shigowa ciki, tazauna akasa kusada kafar sa.
Dama wannan ka'ida ne duk ran asabar tana tareda mahaifinta tana tayashi hira "sannu da hutawa baba, yawwa sannu *hannatun* baba.
Murmushi tayi najin dadin sunan da baba ke kiranta dashi.
Tad'i suka fara yi "irin" na d'iya da mahaifinta, cikin farin ciki da annashuwa.

Aljazeerah! Yake kallo, Amma hankalinsu gabaki daya yanakan tad'insu, tunda ta shigo yamaida hankalinsa kanta, danjin ko akwai Wata damuwa atattare da ita.

Saurin daukan remote yayi "yana kara sauti, subhanallahi, Kai mutane babu Imani, wato duk wani mai gaskiya Sai sunga bayansa.

TV take kallo haikam.
wanda tagama tabbatar wa wannan da yanxu ake fadin an harbeshi, A Aljazeerah"
Shine Wanda ranar sukaji Ana zancen kasheshi,
Batasan lokacin da hawaye yafara bin fustan taba, tsan tsan tausayin sane ya cika Mata ruhi, Lallai wa 'yan nan mutane sun ciki azzalumai marassa imani.

Juyawa baba yayi gunta dan yimata magana,
Tsintar ta yayi hawaye daya nabin daya.
Juyawa yayi yaga yanda take kallo.
TV takurawa idoh, sanin zancen da' akeyi a tv din yasa yayi tsammanin tausayi,
Yabata.

Dan yasan itah! Mutum ce" mai tausayi.
Lallashinta yashiga yi" sannan yace taje daki ta kwanta ,
Tashi tayi ta fita, yabita da kallon tausayi,

Shiga d'aki tayi, takwanta rub da ciki akan gado, Sai zullumin wayannan mutane takeyi aranta.

Hameedah ce" tashigo daka Mata duka tayi, ke Ina kika shiga inata nemanki, saida ta'iso kusa talura da halin da 'yar uwar tata tashiga.
Zaunawa tayi kusa da ita!! Taci gaba da Lallashinta, dan ganinta awannan yanayin tasan ambata Mata rai ne.

================

Koda zuwan su Ummii basusha wahalan shigaba.

Dan akwai abinda sojoinsa suke d' aurawa adam tsen hannunsu.
Ganin haka yasa bbu bata lokaci suka cika cikin asibitin.

Cikin dakin Theatre kuwa,,
Angano dayan harsashin rigar bullet proof dake jikinsa ta tare,
Inda dayan na gefen cikin sa " harsashin bulawa yayi ya fice.
Amma dayake ba Kowani irin harsashi bane, anyi shine na musamman mai hade da guba yasa yaratsa jikinsa sosai.
Gubar mai karfi ce.
Koda kirjinsa da yake da riga Amma sanda wajan yayi shatin baki.

Sun dauki akalla awah hudu akansa.

Kafin sukayi iya kokarin na ganin sun kashe karfin Gubar.

Saida suka kammala komai. lokacin awansu hudu da rabi da shiga theatre.

Inda haryanzu maganin bai fara aiki ba, Sai yayi 1hour ajikinsa kafin yafara kashe Gubar.

Lokaci daya suka gama aka futo dashi, ko numfashi bayayi.

Aka kaishi zuwa wani d`aki mai tsaron gaske.

C I D camera ne takowani sako na dakin.

Nan aka ajiyeshi.

Dan zuwa nan da 2hours numfashinsa zai iya dawowa.

Yanxu roban numfashi ne amaqale a hancinsa.
Wajen dakin kuwa sojojine masu tsaransa birjik, tundaga gate din asibitin.
Ummii kuma na kofar dakin da yake, addu'a kawai takeyi, kokadan tunaninta bai kawo ta "khira mahaifin sa ba.

================

Mai mar taba ne zaune a faadaa.
Wayar sa da ke hannun wani bafade ne, tadauki ruri.
Kallon sa sarki yayi alamun ya amsa, amsa kiran yayi tareda karawa mai martaba akunne.

Sallama akayi ya amsa.
Meh????? Yaushe???? A'inah?? Shine abinda sarki yace, inna lillahi wa'inna ilaihi ra'ji'un kawai yake nana tawa, wanda hakan yaja hankalin fadan.

Rike kansa yayi dayake wani irin sara masa.
Lokaci daya kuma yafara ganin duhu.

To be continued

_Ur's_
_z33yyb3rw3r_

*BIBIYATA AKEYI*

_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

_Wannan_ _shafin_ _nakine_ *nafii* _nagode_ _da_ _yadda_ _kike_ _nunawa_ _liittafina_ _soyayya_
_Kodan_ _ke_ _Sai_ _na_ _kara_ _yawan_ _pages_ 😜

Page 19

*

Duk wani tashin hankali, mai martaba yashigeshi. Jin cewa d`ansa mafi soyuya yananan, rayuwa akwai ko babu.

Ganin mai martaba, cikin wannan yanayi yasa akatashi fada Alokacin.

Dakyar mai martaba, Ya tashi ya shige, sha shinsa.

Kunsan yanda zance baya 6uya, barin ma amasarauta, mai girman gaske irin ta kana.

Har yakai kunnan kilishi, alokacin da'akazo Mata da zancen suna tare da intisar da yayanta guda biyu.

Affan Wanda bazaifi kimanin shekara ashirin da biyar ba. Da halima Wanda tayi aure yaranta biyu. Kanwar Affan ce"

Bakaramin tashin hankali suka shiga ba, jin mahaifinsu na wani irin yanayi, wanda gab yake da tashin ciwansa.

Nufan shashinsa sukayi, cikin matsanancin damuwa, basu jira anmusu isoh ba,

"Shiga kawai sukayi"
Nan suka ganshi ya kifa kansa,
Affan ne yanufeshi cikin sauri, yarikoshi,

Abbah meye yafaru???????
Dagowa yayi ya kalleshi,
Muhammadu je kayi mana tanadar mana jirgi zuwa dubai,
Tafiyan Karya wuce nan da awah biyu"
Abba me zamu jeyi dubai??????
Yareemah!!!!! Yareemah!!!!!!! Kawai yake fadi cikin sarkewar harshe.

Abbah"" mai yafaru da yaya yareeman??????

An harbeshi!!!!!
Fadin irin tashin hankalin da suka shiga ma bata bakine.
Dan affan kuka yaringa yi kamar Wata mace.
Intisar da halima kuwa kuka sukeyi kamar Wanda akace yamutu.

Kilishi" ne tayi kafin halin cewa, aibe kamata mutafi mu kadai ba,
Mukira sauran yan uwansa sannan muwuce.

Hakan kuwa akayi cikin Kan kanin lokaci akasanar da sauran 'yan uwansa. cikin awawin da basu wuce hadu ba duka suka hallara. Fadin irin tashin hankalin da suka shiga ma bata hannu wajan typing ne😭😭,
Sosai suka shiga tashin hankali.
Sai wajan bakwai na dare, kafin jirginsu ya daga. ✈.

================

Anyi iyah bin cike , Dan gwano wayanda suke da hannu awannan aika aikan ankasa, Dan kokadan bbu Wata shaida da zata nuna hakan.

Wannan aikin dole dasa hannun wasu manyan acikinsa, dama daniel yana raye ne to da akwai hanyoyin da zasubi Dan gano wayannan masu laifi.
Amma tun harbin da captain Ahmed ya yi masa, daniel ko shurawa baiyiba ya mutu
Amma a nanan an kara karfafa tsaro da bincike.

Bayan kaman awah biyu da kaishi dakin hutu, wani likita yashiga dan dubashi,
Alokacin kuwa hankalin Ummii yakai kololuwa wajan tashi, dan Har yanzu bawani gamsheshen labari gameda halin da d`anna ta yake ciki.

Likitanne yaje shiga tayi saurin tsareshi, tana tambayarsa yasanar da ita!!! Halin da d`anta yake ciki , Idan ma yamutu ne kawai yasanar da itah"
Mam" d`anki bai mutu ba yana nan araye mana iya bakin kokarinmu na ganin mun ceci rayuwarsa.

Daga Fadin Haka yajuya.

"Yashige dakin"

Turus yaja yatsaya Ganin sa a zaune, kamar ba shine wanda dasu ko numfashi bayayi ba, kallon gefe da gefen dakin yafara yi Dan atuna ninshi ba mutum bane.

"A iya saninsa wannan gubar yakan dauki tsawon lokaci kafin yasake mutum,  harya fara gane mutane.

Fita yayi cikin sauri dan kirawo sauran `yan uwansa likitoci, Ganin yanda yafita a gigice yasa hankalin Ummii dasauran sojojin kara tashi.

Ba'a dade ba yadawo da wasu likitocin guda uku abayansa.

Ganin su cikin sauri sun shige dakin yasa Ummii fashewa da wani matsanancin kuka, basu dade da shiga ba _afeeya_ tashigo Wanda ita kebin MG da yaronta zasuje excotion egypt ne tabishi, Sai kuma wannan abun yafaru shiyasa tabar yaron acan tayiyo nan asibitin, cikin tashin hankali.

Farkon isanta sun hanata shiga ne, sanda takira ummi taturo captain Ahmed yashiga da ita!!! Ganin Ummii na kuka ne yasa itama tazauna ta fashe da nata kukan, bame lallashin wani.

Sai wajan 6 :00am mai martaba suka shiga asibitin, lokacin da suka isoh sun wuce gidansu dake nan Dubai "wato gidan Ummii sanda suka biya bashin sallolin da ake binsu, sannan suka nufee hospital din.

Ummii na ganin isowar mai martaba tatashi dasauri taje ta rungumeshi, sannan tafashe ta matsanan cin kuka, tana cewa sun kashe manashi, abinda take nana tawa kenan, bubbuga babanta mai martaba yahau yi, Dan Shima Idan yace zaiyi magana toh tabbas zai'iya yin kukan.
Allah kadai yasan yadda yakeji, sanin dansa dayafiso yana cikin wani hali,
Ohonsa nikam, tana fadin Haka tashige ta dauro alwala, bayan tafito *hanna* ma tashiga tayi wanka, bata damu Da yamma Da tayiba, ta d'ane gado sai baccin gajiya, dama rabonta da irin Wannan tafiyar tun tana yarinya."

Bayan hameeda ta idarda sallah ne itama tabita gadon, nan danan bacci mai nauyi yayi awon gaba dasu. "

To be continued

_Ur's_
_Z33yyb3rw3r_

*BIBIYATA AKEYI*

_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

*this Page is humbly dedicated To u maman manal yhur such a nice an wonderful person luv u

so much* ```nima inasonki kamar yadda kike sona``` ```muna mugun tare```👍

Page 29

*
Basu suka tashi daga bacci ba, sai kusan bayan magrib. "

Umma batsan da dawowarsu ba dan tajira har tagaji kuma takira waynsu *hanna* ba'a _picking_ yaya jalal dama ransa abace yake shiyasa yana isa yakashe wayansa, saleem kuma bayansa yabi suka shige daki."

Kusan _eight_ 8:00 wata irin yunwa tatashi *hanna*. " gani tayi hameeda tawani baje sai baccin take sharar bacci."

Dak'ar k'arewa tayi ta sake mata marii, a _back_ dinta sanda ta tashi zaune bbu shiri. "

Ke da'allah yunwa nakeji." shine dan rashin mutunci sai ki dake ni banza kawai, tafada hadeda komawa baccin ta. "

_Please sis wake up am terribly hungry_ , bakisan kofa ba kenan, tafada atakaice."

_But i said am srry_ *_hanna_* tace had'eda langa6ar Da kanta, banza marar mutunci tafad'a had'eda mikewa tayi hanyan futa, ai *hanna* dataga ba sarki sai Allah kuma tafiya zatayi ta barta. " a arba'in taduro akan gadon tabi bayanta."

Afalo suka sami Umma tayi tagumi, ai Da gudu *hanna* tawuce hameeda tafad'a jikinta. "

A razane Umma ta juya jin mutun ajikinta, ai tana ganin *hanna* cikin murna ta kankameta ajikinta, sai can ta sake ta."

Ba kunya *hanna* ta gyara zamanta dere-dere akan cinyan Umma, kod'od'uwa Da ita sai wani zuba mata shagwaba take zubawa kamar 'yar goye. "

Tsakin da hameeda taja ne yasa hankalinsu yakai kanta datake tsaye."

Ware mata hannu ummah tayi, sannan tasaki murmushi ta shige jikin Umma. "
Umma Haka Allah yayita dasan yaranta da kuma jansu ajiki."

Ture ture suka fara kamar wasu yan biyu,, dariya kawai Umma keyi musu, dan yanda takejin hameeda Haka takejin *hanna* kokadan bata tabajin banbanci akansu ba, hasalima dukansu da ita suke kama. "

Yaran ummah biyar ne Allah ya azirtasu dasu, babban danta ya auwal shike auran anty

hindatu yar mama, sai me bi masa yaya jalal, daga nan sai anty samha wanda za'ayi aure tagana degree dinta a buk." sai salman wanda hameeda ke bi masa, yagama degree dinshi agana yana service, kunsan yanayin karatun mu bad'aya dana muba dan anty samha tarigashi shiga da shekara daya amma tare suka gama, sai hameeda itace auta."

*Hanna* ce tarik'e cikinta cikin muryar shagwaba tace Umma yunwa, tashi tayi taja hannun su zuwa dining, sanda sukaci suka koshi sannan suka fara tamvayar wajen anty samha. " shaida musu tayi tana d'akinta aguje sukatashi sukayi dakinta, tana waya da mijin da zata aura saiji tayi kawai anzube akanta had'eda saka ihu."

Itama cikin razana ta saki nata ihun wanda sanda yasa abubakar dake zaune a kusa da MG yana waya saurin kawarda wayar a kunnensa, afili kuma ya furta su hameeda an isoh kenan. "

Gaban MG ne yafadi, yanason masa tambaya amma bayaso ad'ago shi, kawai saiya share."

Amma ransa fall yake da farinciki, ya tabbata *hannan* sa ta isoh lafiya. "

Juyowa tayi aikuwa tana kallonsu wani sabon ihun ta dad'a sakewa sanna ta rungumesu, Umma tana daga falo amma tanajin ihunsu."

Yan iska yaushe kuka isoh?? "

Tun da yamma" shine kuka shige daki? " kunsan tun yaushe nake jira kuzo kufutar da ashoben kanne yan iska kukaki zuwa."

*Hanna* Da hameeda ne suka kalli juna harsuna hada baki wajen cewa k'anne?? " *Hanna* ce ta tabe baki yanzu ke anty samha ku kunya bakijiba wajan cewa wai mu muyi ankon k'anne, hameeda ce ta amshe zancen haba anty yanzu dame kika fimu?" har mun daraki atsayi fa gaskiya aduba wannan zancen."

Daura kafa daya kan daya sukayi sai wani jujjuyata sukeyi, irinna mararsa mutuncinnan. "

Ita kuma anty samha tunda suka fara magana tasake baki kawai tana kallonsu, Ita kanta tasan gaskiya ne inba fuska aka duba ba ba'ace ta girmesu ba."

Idan ta jiki ne ma sai ace sun girmeta. "
Cikin rasa abin cewa tace ku6ude, _wadrope_ dina zaku kalli kalli kala biyar biyu na k'anne, uku na kawaye, green da yellow dinne na kannen saiku ebi na kawayan."

*Hanna* ce tatashi ta bude sif din, na kawaye tafara cirowa sanda taciro set uku, sannan tajuyo, taga yanda anty tazuba mata idoh, meye🤷‍♀️?? " *Hanna* hameeda amira tafad'a atakaice."

Hameeda ne tataso, Itama, " na kannen ta eba set biyu."
Kwasan kayan sukayi dasu fice, anty tatsaresu, me kuma dakuyi dana k'annen, owh anty dan munce baza musa abiki ba _doesn't mean_ ba maso, "  A'a kawai abikinne baza musaba." suna fadin haka suka fice suka barta _totally speechless_

Abubakar kuwa dariya yakeyi kamar dan itah aka aikoshi yi duniya."  tun lokacin bawai yakashe wayan bane, saima samusu Ita da yayi a _handsfree_ koh MG dako murmushi bawai yacika yi bane amma yau sanda yayi har hak'waransa yafito. "

Jin muryar ta da yayi yasashi awani irin nishadi, soyayyarta ne ke ratsa duk wani gabbai najikinsa,"  wanda har wani kasala yasaukar masa dashi, " sai wani shimfid'aden murmushi wanda ke kwance a fuskarsa dayasa, kuma tunshi suka zauna a lobe wato dimfull, wanda wasu ke kira da _beauty point_."

Damashi ko motsa bakin sa yayi, toh _side da side_ na _cheeks_ dinsa sai sun lotsa, "

Su *Hanna*  nashiga daki duk suka zube kayan ak'asa, *Hanna* ce tacire doguwar rigar dake jikinta, da niyyar shiga wanka, yarage daga itah sai _bra_ da short din wando wanda yawuce guiwa amma baikarasa kasaba."

Hameeda ce tashigo, daga falo taje dauko ruwan sanyi,, saurin daukan rigarata tayi da niyyar kare jiknta. "

Wata muguwar harara da hameeda ta watsa mata da'allah banza, with dis yhur platty tommy mai mutum zai kalla?"  eh din najidai futa da'allah. "

K'arasa shigowa tayi saikiyi kuma."

Tsaki taja ta shige _toilet_. "

================

Tashi yayi ya shige shaashinsa."  idanda sabo abubakar yasaba, shi bayayun sallama saidai kawai kanemeshi karasa. "girgiza kai abubakar yayi sannan shima yatashi yatafi."

Yana shiga dakinsa wani godon alfarmane aciki, wanda daka kalla ansan gadone wanda jinin sarauta ne kawai masu irinsa wanda ake kira da _royal bed_ . "

Farin _bed shit_  ne kall a kan gadon a shifideh, kamar yanda _paint_  nadakin yake fari, Dakin yakai akarsa gado uku aciki kawai dan girma da kyau."

Dakin a gyare yake tsaf-tsaf bazakace akwai mai rayuwa adakin ba tsabar yanda dakin yake so _cleanness_. " wani sanyi mai dadda dan kamshi ne ketashi wanda yahadu da kamshin _room_

_freshner_  dana turarukan dayake amfanida su yabada kamshin sanyi."

Wata kofar _glass_ yanufa ammata _design_ mai dan karan kyau, wasu numbers yadanna kofar tabude. "

Ashe wani dakinne aciki, shima komai nadakin farii fat _pics_ din *Hanna* ne akowani lungu da sako nadakin."  tun tana karama har lokacin da tadan tasa har izuwa girmanta nayanzu. "

Kurawa pics din idanuwa, sannan yakarasa ya6ude wata _drawer_ yadauko wani diary mai kyau harda bironsa a manne Ajiki."

Wasu yan rubuce rubuce sannan yamayar ya aji'yeh, ya tashi zai tafi yabige _drawern_ wani file ne yafado, takardun ciki suka watse, kurawa takardun idoh yayi."

To be continued

_Ur's_
_z33yyb3rw3r_

*BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

Page 30

*

Tsugunnawa yayi hankali ya tarataro takardun yana me kare musu kallo. "
Afili, ya furta subhanallah wat _boders me_ Haka dahar namanta da takardunnan."

Neman bakin gado yayi ya zauna, tabbas na gabatar da takardunnan."

Kiran captain Ahmad yayi,"   inason ganinka yanzu, ya ajiye wayan ba'a dad'e ba kuma sai yajin ring alaman anshigo falonsa. "

Tashi yayi ya nufi hanyar fita hadeda takardun a hannunsa, yana Futa kofan takoma tarufe, bakace dakine awajen ba saidai kayi zaton _locker_ ne haka

Sanda yafuta adayan dakin, sannan yanufi falo."

A tsaye ya samu captain Ahmad, yana kallonsa yayi saurin k'amewa, wata harara MG yabishi da itah. "

Da'allah malam sauke mun hannunka, cikin gidana muke ba _barrack_ ba." sauke hannunsa yayi hadeda dan sosa kansa. "

Zama yayi ya nuna masa waje shima ya zauna."

Mik'a masa takardun yayi sannan yace" shad'af na manta dasu, karba yayi ya bude, cigaba yayi da cewa " yaushe kaga yakamata mugabatar da su??"
Dan idan mata ki ne ma yskamata adauka tun da dad'ewa. "

Kallonsa yayi sannan yafara magana acikin lafazin da zaifahimceshi."

Yalla bai da mu d'an dakatar da wannan zancen tukunna kallonsa yayi da alamun tambaya? " dalili?" yafada atakaice. "

Dan zakudowa yayi akan kujeran, alamun yanaso zancensa yashiga."

Yallabai kaga nan bada dade waba kaza kama ango, harara MG yasakemasa wanda bbu shiri yashiga taitayinsa. "

Shiru yayi nadan wani lokaci." cikin hasala MG yace kaifa nake sauraro"

Yallabai be kamata ace angabatar da wannan shaidu, batareda, kayi aureba tukunna. "

Kasan lokaci k'alilan yarage faruwar hakan."

Wayanna mutane ba k'ananan _criminals_ bane dasu iya _hurting_ dinta. "

Dasuyi iya _investigation_ dan su ganota." maiyasa kace Haka?? " meyasa ni bazasu yi _hurting_ dinaba sai itah??"

Wani dan murmushi captain Ahmad yayi, naganin shawararsa tafara shiga."

Yallabai _i know_ yanzuma _may be_ _they have tried several tyms to hurt_ u but Allah baibasu ikoh ba. "

Dannasan bbu yanda za'ayi susan wyannan _evidence_ na hannunka wanda zai iya _destroying life_ dinsu kuma su zauna shiru," _u knw dat it can't be_. "

Atunanin yanzu haka suna neman abinda kafiso wanda zasuyi _treating_ dinka akansa."

Bincike bbu yanda bazai iya ba, karkasha mamakin su nemota kuma su sameta. "

Alokacin bbu wani _sucurity_ da zasu iya kareta, amma idan tana karkashin _she will be more safe_ _than_ ace tana gidansu" .

Yallabai idan tana karkashinka akwai * _sucurities_ masu bada duk family dinnan kariya, kuma hankalinka zai fi kwanciya da fargabar mai zasu iya aikatawa. "

Ni yanzu aganina _is good n better_ anyi abu cikin gaggawa, ayanzu _may be they planning or up To something terrible_ wanda faruwar sa bazaiyi da'di ba."

Captain bala da kalan kakin tawagar mu suke amfani baka ganin, wasu zasu iya binkice mai suke bi?? "

Shiru MG yayi yana tunani dan duk maganar captain Ahmad gaskiya ne."

Atake hankalinsa yatsahi gani yake kaman yanzuma nemanta sukeyi, atake idanunwasa suka kada sukayi red. "

Sosai captain Ahmad yashiga rudani, yafara cewa _sir am srry i dnt meant To hurt u."_
_No u didn't_ yafashi amsa atakaice."

Nagode da shawarka kiramun sajen ma'arof, tashi yayi cikin 2 minute sai gashi sundawo tare. "

Idanuwansa a lumshe dan yasan da shigowarsu."
Kaje kasamu wani Acikin soldier's d'ina, kutafi wajen captain bala, kace masa nina ce kuyi aiki tare, captain Ahmad zaimuku bayani, sannan kullum yaksance da _gun_ ajiknku, yana fadin haka ya tashi yashige daki. "

Wajen su hanna kuwa yau kwanansu biyu da zuwa garin kano, duk yadda za'ayi event abubakar yazo sungama shiryawa biki sai k'aratowa yakeyi."

Suna daki *hanna* na kokarin saka kaya yayinda hameeda ke zaune akan chair na dressing mirror sai kwalliya takeyi. "

Shiri sukeyi dan zuwa wajen kai dinku nan su,

*Hanna* Sis wai me yasa ya jalal baya fitowa ne kwana biyunna, ta6e baki hameeda tayi lokacin da take shafa, _lipgloss_
Barina je dakin sa nadu bashi tana fadin Haka tasakai tayi waje, dakin ya jalal tanufa, hameeda

uwar gulma itama aguje tabita. "

Sallama tayi amma Shiru babu amsa, kai tsaye tasakai ta shige,"

Ganinsa tayi yayi rigin gine, yayi zurfi atunani, Zama tayi a bed side drawer amma baimasan da shigowarta ba, aranta tace su yaya anfad'a fahh, dan wannan tunanin sai wanda ya nutsa kogin soyayya. "

Ya jalal!" ya jalal " takarkarewa tayi ta kwala ihunda yasashi mikewa zaune bbu shiri, Kada kai tayi sannan yafara rero waka."

🎼Alamar tambaya tanaga mai yawaita tunani 🎼🎼musamman yashiga halin soyayyar zamani🎼🎼yau gashi ciknta 🎼🎼yarasa wanda zai fiddashi 🎼🎼sai ita masoyiyarsa wanda sukayi kyau da kamanni🎼🎼

Kallon mamki kawai yatsaya yana mata, bai k'ara sarewa ba Sanda yaji hameeda tashigo tana nata wakar. "

🎼abinda yake ranka zaka fitar ka huce tunani🎼soyyace aranka🎼garaka fada bazata ficeba🎼🎼

Tunani yafara aransa, kaddai yarannan sun fahinci yana son *hanna* ne

*Hanna* ce takatse masa tunaninsa, ta6ashi tayi yajuyo gira daya tad'aga masa wacece? "

Kece yace" zaro kwala kwalan idanta tayi " saurin gyara zancen yayi Kece fitinanniyar dakika katseni daga tunaninta ai." sauke ajiyan zuciya sukayi daga itah har hameedan, toh yaya wacece? "

Katse zancen yayi kutashiku fita kubarmin daki, Haka dole ya korasu."

Maya fansu suka dauko suka fita dan kai dinki. "

Duk wani abinda ammahtasan zai kawowa amma kudi sanda tad'aga tasayar, yanzu Haka tagama hada kudin zuwa gobe dasuje gun malam."

Hanna sunfito daga gidan anty hindatu, kasncewar anguwar bame jama'a bane yasa titin bbu kowa. "

Kaitsaye suka nufi titin dan tsallake shi, a lokacin motocin MG suka danno hancinsu atitin."

To be continued

_Ur's_
_Z33yyb3rw3r_

[12/2, 9:26 AM] Anty Jamila D Ili: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

My first novel

_Wannan fage din nakune masoyana *maman zarah 😍* *murjanatu(admin)*
And *zuwairat(addansumy)* zaynab bawa na kaunarku kamar yadda kuke kaunarta *ILYSM*_

Page 31

*
Titin sukaje tsallake wa a lokacin motocin MG suka danno hancin motarsu Titin dake layin. "

*Hanna* ce ta juya da sauri sis na manta phone dina Adakin anty bari nadauko," sai kin dawo amma nikam barin tsallaka zan jiraki. " juyawa tayi da niyarr komawa ihun da hameeda ta sakene yasata juyowa da sauri, ganin hameeda tayii akasa, ashe lokacin da tajuya take yiwa Hanna magana a lokacin motocin sun rigada sun zo tsakiyar titin, hameeda bata luraba ta shiga sukuma basu tsaya ba sukaje gadan gadan kanta," aikuma kunsan base nafada ba kunsan sojojin bazasu tsaya danta tsallaka ba. "

Aikuwa hakan ya bala'in 6ata ran Hanna ganin ko tsayawa basuyiba dan duba lafiyarta, afusace ta dauki wani katoton dutse, dan niyar jifan motocin, hanata hameeda takeyi amma fir taki jefa dutsen tayi Aikuwa kamar ta saita sai motar da MG yake ciki."

K'aran dutsenne yadawo da hankalin MG dayake Waya, lokaci daya hankalin sojojin duk

yatashi. "dan sun d'auka hari aka kawo musu, MG ne ya umarci a tsaida mota, ganin fuskar da yafiso aduk duniya idan aka cire na mahaifansa, ta madubi sai huci takeyi."

Ganin antsaida motane yasa sojojin fir fi towa kowa da bindigarsa a hannu suka zagaye motar da MG Ke ciki. "

Umarta yayi da abude masa kofa babu musu suka bude, captain Ahmad dake gaban motanne yafitoh yana tambaya ina zaije amma ko kulashi baiyiba ya nufi wajan su *hanna* su sajen ma'aroof da motar su kecan gaba suna gadin *hanna* suma ganin haka yasa suka futo, suka nufi ogannasu. "

Su captain bala ma da suke can baya wanda dama sunga wucewar ogannasu amma ganin ya tsaya suka fito suka nufesu, hangosu yayi daga nesa ya musu alama dasu juya, bbu musu suka koma, ya karasa wajenesu *hanna* datake rikeda kafan hameeda tana mata sannu. "

Hameeda ce tafara kallonsu, ahankali tabugi *Hanna* tanuna mata ai suna kallonsu atake suka mike tsaye cikin su yahau lugude."

Yana karasowa gabanta yafadi, subhanallah yahadu Addu'oi kawai takeyi dan azatonsu gamo sukayi deyi wuya samun namiji mai kyansa, hameeda kanma dabadan kartayi karyaba datace har daukan idoh yakeyi, "

Ta6a Hanna tayi kinga abinda kikaja mana ko" kin ta6o mana dan balarabe. " yana karatosu wani ni'imtaccen kamshi na ziyartarsu" dakyar *Hanna* tattaro kuzarinta cikin jarumta dan kwarjini gareshi kamar zaki, duk sai taji yacika mata idanuwa idanuwa, adan zafafe tace. "

Tsayawa kazo yi ko kazo bata hakuri ne?? Shiru yayi ya tsaya kallonta, Eyhem tambayan ka nakeyi kawani tsareni da idoh" azafafe wani soldier yayi kanta da niyyar marinta, captain Ahmad ne yayi saurin tsareshi, katsira da aikinka kawai yafada masa. "

Rike k'ugu tayi tana karar raya, sannan taciga ba dacewa" ai dama nasan irinku bakusan darajar dan adam ba burinku kawai kuci mutuncin kowa." kokadan baiji zafin magan ganinta ba saima wani sanyi dayake ziyartar zuciyarsa, gawani irin girma kyau da cika idoh datayi masa, wutar santa ne take kara ruruwa acikin zuciyarsa. "

Hameeda ce take ta ta6a ta akan tabari amma ture hannunta kawai takeyi."

Wasu daga cikn sojojin ne sukayi kanta a hasale, daga musu hannu yayi alamun su koma Haka suka koma badan ransu yasoba saiwani huci sukeyi, araina nace yanzu yanda kuke zabga-zabga dinnan idan aka barku saiku daketa? "🤔. "

Karasawa yayi har gabanta alokacin sai faduwa gabanta yakeyi, gawani irin kamshi dayake shirin rikitata ." yatsunsa guda biyu yasa ya 6alle mata baki ai babu shiri tasaki ihun azaba, sannan yace" bbu kyau yin rashin kunya anah gaba dakai" yafad'a kamar mai yin rad'a, aikuwa tana sakee bakin tace Allah ya'isa na mugu azzalumi. "
aibaisan lokacin dayawaro idanuwansa ba, wato ita wannan yarinyar batada tsorone ko kad'an?" aikuwa bata ankaraba ya k'ara 6alle mata bakin, nanma tasake sa wani ihun Atake kuma tace Allah ya'isana, aibata k'arasaba yakara 6alle mata baki,"

Ihu tasa wannan karan kan harda bubbuga k'afa takusan sa MG dariya dakyar ya danne," Allah yahhh, aibashiri tasa tafukan hannunta tarufe bakin,"

D'an sunkowa yayi yace Allah yayime? "wata uwar harara da doka masa," haderai yayi yace, idan kika k'ara yiwa wani rashin kunya nidake, yafada had'eda nuna kansa da ita wanda inba ita data ganiba bbu wanda yafahimta."

Yana juya baya tace kuma sai Allah yasakamun, a hankali kaman mai tsoron yajita, aikuwa karaf a kunnensa juyawo yakara yi atsorace tayi baya, dakatar da ita yayi sannan yamatso yanda bbu wanda zaijishi, yace idan kikayi hakuri kwannan ma zaki rama da kanki, yana fadin Haka yajuya yabarta adaskare agun takasa gane wannan maganarsa ta karshe. "

Juyawa yayi wajen hameeda, sake fuska yayi, yayi wani _killer smile_ yamata wanda yasa hameeda sake baki kamar wata doluwa."

Cikin kwantar da murya yace _sorry_ _dear_ bansan haka zaifaru ba kiyi hakuri. "

Hadiye wani miyau tayi bakinta har yana 6ari tace bbu" ""babu komai. " wata 'yar dariya yayi, ok ko zaki shigo musaukeki?"

Wani bakin ciki ne ya turnuke *hanna* ganin yanda hameeda ke binsa da ido kamar sokuwa. " haka kawai ta tsinci kanta da jin haushinsu duka, fuuu tabar musu wajan tayi ta nufi gidan anty hindatu."

Kallo suka bita dashi, sannan yadawo da kallonsa kan ta, muje ko yace mata, kallonsa sa tayi sannan tace, idan na tafi bazataji d'ad'iva kuma kaga ita bakuwa ce batasan gari bah. " tafad'a irin bahaka taso dinnan ba."

Karki damu, kije ki kwantar mata da hankali naga kaman ranta yabaci karki barta cikin bacin rai."

Kallo mamaki tatsaya yimasa, kanne mata ido daya yayi sannan yajuya, ya nufi motarsa, captain Ahmad yagani sai wani rike dariya yakeyi, harara ya 6alla masa. "

Kai tsaye mota yawuce, suka rufa masa baya suka tafi."

Duk abinda malam yabukata Ammah ta shirya Kai tsaye suka Kai masa, ya umurcesu dasu dawo gobe. "

Kaitsaye washe gari sassafe suka wuce ya shaida musu cewa komai ya wakana amma bazaiciba harsai randa hanna suka had'u da najeeb."

Abinda Ammah tamanta shine tacewa malam ya rabata da najeeb amma batace masa ya rabata da kowani saurayi ba. "

Yaune ranarda su chief suka yanke danyin meeting akan MG, suntaru awani office wanda duk kujerune anzagaye da kujeru, zama sukayi sukafara gudanarda abunda yakawo su."

To be continued

_Ur's_
_Z33YYB3RW3R_
[12/2, 9:27 AM] Anty Jamila D Ili: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

My first novel

*

Tana shiga da gudu takarasa kamar wanda aka jefota, atsorace anty hindatu tatashi tana tambayarta maiyafaru amma ko kulata batayiba, tashige daki ta fad'i rub akan gado tafashe da wani irin kuka maicin rai. "

Tunda take arayuwarta bbu wanda yataba mata cin mutumci irin wannan _he just ambarass her in public_ agaban jama'a atake wani irin tsanarsa da baibayeta zuciyarta jitayi batada wani mak'iyi kamarsa wani irin * _hatered_ takeji wanda bata tabayiwa kowaba."

Ringing da wayar ta tafara akan dressing mirror ne yakatseta, da kaman bazata dauka ba sai wata zuciyar tace mata ko najeeb ne, dan ita yanzu abin najeeb har mamaki yake bata. " saiyayi 2days bai kirata ba kuma some tyms kota kira baya picking."

Wiping din tear's nata tayi tanufi kan dressing mirror ta dauki wayar, To her biggest suprise sai taga amirace ke kiranta, with full of happiness tayi picking, beb u just foget about me, badai kunkamo hanya ba?? " nop bamu kamo ba, but wen dear??" is only 2days yayi remainig afara event fahh, " srry To say dat but beb inaga zuwannawa ma zaiyi wuya, " dan dady ya han,,, ai bata bari tagama ba tayi hanging call din, sosai ranta ya6aci, wani irin bakin ciki ne ya turnuk'eta she feell much more anger than abunda aka mata recently."

Anty hindatu na falo gabaki daya she worried batasan maiyasamu sister dinta ba, jiran shigowan hameeda kawai takeyi. "

Can kuwa sai ga hameeda, dasauri anty ta taryeta, hameeda wat happen To dis stubborn naga ranta abace."

Is nothing fa anty, kawai mun d'an haura ne, " wani tsaki anty taja mtsww, wawiya shine da d'agamin hankali, tana fadin haka tanufi daki."

D'aga cutton din dakin tayi, da'alla wawiya zoki fucemin agida, azuciye *hanna* ta d'ago da'alla awani gidankin da ko kyau bbu, eh naji dai. "

Suran phone dinta tayi, sanda tazo dai-dai ita, wani dirty look da wurga mata sannan tace idanni ne Wallhy saikinzo neman, with dis ur crumpy leg's, duka takai mata tayi saurin go cewa" kiyi ki fad'i akan wannan katon ciki naki ki haifi dan wata takwas bbu ruwani danni gida zanwuce, eh toh banza inaruwanki, tafita tana mita tsafar rowa sai kuyi gida 2 bed rooms dan karkowa yazo ba, dama haka halin anty hindatu da *hanna* saidai basu haduba sai anhaura amma na'yan minute suka rabu kowa yafara missing dan uwansa."
Dama haka mabiyi da mabiyi suke dan *hanna* ita takebin hindatu kuma tsakaninsu ratan 1 and half year ne shiyasa suka taso kamar sa'anni dan *hanna* gani takeyi kamar rana daya aka haifesu. "

Hameeda ta tarar a falo tana jiranta, wuceta tayi kaman bata ganta ba dan wani irin haushinta takeji."

Binta hameeda tayi tana bata hakuri dan gaskiya she feells very bad ace wajen nema mata 'yanci an 6ata ran' y'ar uwarta. "

Dakyar *hanna* tasauko maimakon suyi gida sai suka wuce yawo, sai closed to magrib, suka nufi gida."

Mota suka kalla afake, cikn sauri suka karasa dan haka ya nuna musu mama ta isoh, ciki suka shiga da gudu suka fad'a kan mama ai ba shiri tafara turesu da'alla kutshi karku karyani."
*Hanna* ce tatashi abinda cinyar kinma bawani dad'i na Umma yafi, tana fadin Haka tatashi tayi daki, hameeda ce tabita da gudu zata daketa, itama gudun tasa sukayi daki ganin mutum akwance akan bed dinsune yasasu tsayawa cirko cirko."

Hameeda ce takarasa ai ```to her biggest suprise``` amira ce akwance akan bed d'in tai saurin d'ale gadon tana ihu ta bata wani, ```huge hug``` ai *hanna* na ganin haka itama tayi ```landing```akan bed din tayi hugging nasu duka sanda suka ciki gidan da. ```Screaming``` dakyar suka ```letting go``` na ```hug``` din *hannace* tace ```OMG beb u suprise us``` i knw shine dazu hadda hanging dinmun call ai, srry beb kinban haushi ne shiyasa, to ba ganiba, sai abude chapter na rashin mutumci," hameeda tace nikam book guda zanbude ba chapter ba, dariya duka sukasa, hameeda ce ta k'ara cewa ke beb bakisan mai yafaru recently da wannan beb dinba, *hanna* ce tayi doka mata harara kinga bansan iskanci Wallhy, leave her beb nidai kawai bani nasha, haka hameeda tayita koro mata labari, ai dan dariya amira har riqe ciki takeyi, da'alla banza ```stop lough ding at me``` dakyar ta tsagaita wallahy kalan luv dinku ne so muaahh 💋, banza baki ganshi bane wannan dan ego din,"
uhm dama ki fad'i gaskiya amira tace. "

Can kuma kaman wanda aka soka mata allura tace" hameeda baki noticing ba lips dinshi is like yana shafa janbaki, amirace tayi saurin cewa anzo gun, dai-dai gunma kuwa inji hameeda, shiru tayi musu kawai, amira ce takara cewa beb dont tell me dat his lips are so lucious?"

Banza tayaya zansani,
```oh i see🤔 but I definitely knws dat u feell like kissing him dat tym```iya k'ulewa *hanna* tak'ule, she feells kaman ta aikasu lahira,
anahaka hameeda takara cewa watoo dama yana magana ke lips dinshi kika tsaya kalla ta fad'a, ```oh ya rabb🤦‍♀️ am leaving dis room right now``` tana fadin haka tatashi tafuta had'eda banko musu kofa, hameeda ce tadaga murya yanda zata jita tace tasbahy alah khair habibty, dantasan abu mai wuyane tadawo dakin. "

Direct dakin da aka killace anty samha danyimata gyaran amare ta nufa." tanashiga shiga tasamu anmulke ta da kayan gyara kala kala. " zaunawa tayi itama tace sai 'anyi mata Ahaka Matar tazauna itama ta mulketa tsaff." dan ita aganinta kudintane zaikaru bbu ha'incii tamulketa kamar yadda tamulke samha haka itama tamata. "

Umma ce tashigo hannunta rikeda abu a kofi." tayi mamakin ganin *_hanna_* amma saita share, ganin *hanna* amulke take dariya takamata aikuwa tahau yinta bakakkauta, turobaki tayi Umma menayi kikemun dariya? "
srry My doughter mikawa anty samha kofin hannunta tayi, cikn nuna kyama samha takarba takafa kai, tafarasha, ganin tana shirin shanyewa yasa *hanna* tayi saurin faucewa."

Wani discusting look anty samha tabita dashi, Umma kuwa tatsaya kallon ikon Allah." turo baki tayi yanzu anty inwajen saiki shanye? " tana fadin haka batajira amsaba takafakai, aibashiri zata dawo dashi, Umma ce tqkatseta, Wallhy ```if u dare``` saina ebo wanda yafishi ```an then feed u like a baby``` bashiri ta shanye tasss."

Blanket taja tarufe su sannan tafita, anty samha ne ta juyo sukayi facing each other, habibty, Yes aunt, who's the luckiest guy?? "
Hmm"
Why humming dear?" "tell me."
Hawayene yafara sintiri a fuskanta, oh god dear, a ranta tace sumtin is behind that tearness, Tashi tayi tazauna itama ta tayarda itah. "
D'ago fuskanta tayi, habibty tell me whats wrong?".

Ai kaman jira takeyi tafada jikinta tafashe da kuka." plz habibty stop crying and tell me whats wrong?? "
Rarrashinta tayi tayi Ahaka hartayi shiru ta, zayyane mata everything, sanda tayi kwalla dan tausayin kanwarta da tsanar hali irinna Ammah. "

Cikin kuka tacigaba da cewa" aunt i love him i dont wanna loose him, he's all i got and i want, he's driving me crazy aunt," am dying without him, saurin rufe mata baki tayi,shhhh stop saying those horrible things dear, yaushema kika sanshi just afew months back, har daza kiyi tunani bazaki iya rayuwa babu shiba," u had to be strong my dear, ". try hard to show him u can live without him either kinji dear?" Daga mata kai kawi tayi."
```

Haka tayita rarrshinta hartayi bacci.".  Tadaura niyyar saita cire mata najeeb arayi. "
Ita hankalinta yafi karkata da masu binta, Dan tanagani kamar wanine yake dakon Santa kuma bazata bari wani najeeb lokaci daya ya masa shigan sauri ba. "

Araina nace kaji Mata saikace Wanda takeda tabbacin hakan🤔🤔 ahaka bacci ya kwashesu."

Read more😜

To be continued

Ur's
z33yyb3rw3r
[12/2, 9:29 AM] Anty Jamila D Ili: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

My first novel

Page 33

*
Sai wajen three 3:00 am suka farka."
Matan dake dama already agidan take har tazo dan itama ta tashesu. "
Warm water tafara hadawa samha ruwan yasha different types na turaruka, wanka taje tayi, sai

bayan tafito ta had'awa *hanna*  wankan itama tayi,"  tun a toilet din take kallon skin dinta, yayi wani soft an silk, sai sheki takeyi yadda kasan skin din nicky minaj. "
  After she come's out ba anty samha bama har  maigyaran sanda tatsaya kallon ta."  tanada irin oily skinny ne mai shegen daukan gyara, anty samha ne tahad'e hanna yenta👌 looking gogeous 😍my dear, " wani dan rangwada tayi had'eda farfari da idoh sanna tace tanks aunt😘."

Kallonta anty samha tacigaba dayi, habibty baki ganji bane harzaki tsaya yin kuka akan wani najeeb, aikin wucewa nan."
U alway's look more beautifull My dear. "
 *Hanna* ce tace, anty toh idan wani aiki ne yake keeping dinsa busy fa??"  karnayi saurin yanke decision  da zanyi regretting, at the end. "
Juyo da ita tayi suna fuskantar juna, sannan tad'an tallafo face nata tace," no  My dear" if he really care's he will always find a chance. "
Is not fair been busy to the one's we love?" kwace fuskanta tayi ganin haikan tadage so take ta rabata da masoyinta. "

 Cut the crap aunt, i knw sumthin Is behind, and i won't let U to ruin my relationahip, no matter how couse." kallon mamaki damata tarasa wacce irin yarinya ce, saikace wanda yamata black magic. "   ita kwata kwata bai kwanta mata ba, bazata lamunci," yaringa sa mata yar uwa cikin tashi hankali ba. "

  Habibty kinaga kaman inason rabaki dashi ne, amma Allah yamana za6i," amin tace. "

  Anty kinsan maiya faru jiya?" nop my dear saikin fada "
Kowani tunani tayi kuma saitace, just foget it,  Kallonta tayi maiyasa zanbari fadamin kawai, nop anty ki mance kawai,"  Allah yashiryeki kawai anty tace, ita kuma ta amsa mata da ameen. "

Mayukan da anty samha take shafawa itama ta mulke jikinta dashi."
Dama already tayi alwala, sallah tagabatar, sannan takoma bacci bata tashiba saikusan 9:00 . "

  Fita tayi zuwa falo, ganinsu mama azaune da sauran 'yan uwa yasata gaishesu."  sannan tashige side din dasu hameeda suke."
  Shiga tayi bbu wacce takula aciknsu tanufi inda tabar phone dinta. "
  Dauka tayi tazauna tana danne danne, jira takeyi sumata magana amma bbu wanda yakulata."
Wani bakin ciki ne yatokareta, tashi tayi taje gabansu, beb baku kalli yadda skin dina yayi bane, "
Nunawa sukayi basusan tanan ba."
Bebs am talking,
Ainanma ko susan tanayi, Bebs are you deep? "
Ganin bbu me kulata ne yasa tayi hanyan Fita azuciye."

Dariya suka fashe da ita sannan suka tafa. "
Bakin ciki yasata banko musu kofa."
Tayi dakiin yaya jalal. "

================

Zaune suke awajan meeting din kowa ya hallara." juayawa yayi ya kalli wani mutum da fuskar sa ko kyan kallo bbu. "
Ka nemomin tarihinsa kamar yadda na bukata?? Eh nasamo," Ka tabbata baka fidda ko mutum d'aya ba aciki? " eh" toh, lets watch. " video din sukayi playing."
Anyi sa'a ansamu tun farkon fitowar *hanna* daga gidan maman amal, harkarshe. "

Kashe video din sukayi," daya daga cikinsu ne yafara magana, gaskiya wannan ba setup bane kamar yadda muke tunani, "
Dole yanada wata alaqa da wannan yarinyar."
Fadowa kawai yayi akan d'anka,"
Amma kuma hakan bawai yana nufin ya kyalemu bane, dole mudauki mataki tun kafin ya waiwayemu. "

sadam"" yes sir ", inason yanzu katashi kabamu labarinta duk wani abinda yasha feshi."

To be continued

Ur's
Z33yyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by
© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

My first novel

Page 34

*

Dakin yaya jalal tanufa, dirct, knocking kofan tayi, shiru akayi can takara, yaya is mee
Shiru nanma ganin haka yatabbatar mata yabayan juyawa tayi ta nufi dakin anty samha. "

Shiga tayi tasamu anty samha sai waya takeyi batasanma tashigo ba, sai wani Kashe murya takeyi, biten din lower lips dinta tayi, sannan tayi shaking head dinta, arqnta tace, u always trying 2 seprate me from My very own, amma ke kinwani zage sai shan soyayyarki kikeyi, daki gane tafada, sannan tayi kwafa. "
Gefenta taje ta zauna, chicks dinta ta tallafe da hannunwanta takura mata ido, dan d'aga wayar tayi akunnenta, d'aga mata gira d'aya tayi sannan tayi lowering voice dinta tace," what happen dear?"
Shaking kanta tayi sannan tace bbu komai," ok why d look?, "
Kawai kunbirgenine, 👌 mayar wayan kunnenta tayi sannan tacigaba da phn dinta."
Kamar wanda aka cikareta tace, anty da alama kinasonsa dayawa? "
Shiru anty tayi for a while, sannan tamasa sallama juyawa tayi, tayi facing nata."
Magana tacigaba, anty baki ta6a tunani kamar yadda kikeson yaaa abubakar, haka nekeson najeeb ba. "
May be ma irinsonda nake masa yafi wanda kika yimasa."
Wani irin tausayin *hanna* ne yakamata, a hankali tace iknw how u feel dear, but yakamata koyaya destiny dinki yazo kikarbeshi hannu bibbiyu, sai kikalla Allah yasaukaka miki. "
Ahaka tayita rarrashinta har yamma suna daki suna tad'ii da anty samha batakarabi takan su amira ba."

Najeeb na zaune adakin sa, tunani yakeyi yau kusan satii d'aya da yiwa abbansa magana, amma Shiru haryanzu, be nemeshiba, kuma bai bashi wata kwakkwaran evidence nakin zuwa nema masa aure ba."
Gashi yarasa meyake damunsa ko waya ya dauka zaikira *hanna* sai yarasa dalilin sa zai hanashi."
Wani iri yakeji wanda idan bai ganta acikin wannan week dinba sai ahankalii. "
Yanke shawara yayi kawai zuwa nanda 2days zaije kano, dama already yasan address din."

Umurtar sadam yayi daya tashi ya basu labarin MG. "
```Wai shin waye wannan MG d'inne daya addabemu kam??```
```

*WAYE MG*

Abdullahi Abudulaziz lamido ne asalin sunansa."  asalin yan garin kano ne, masarutar kano."
Kakansa shine sarkin kano mai rasuwa. "
Abdullahi muhammad lamido, yanada yara shida,"
Abudulaziz shine babban d'ansa sai abudulrahman sai khadija da kuma halilullahi, sai hannatu da kuma autarsu sa'adatu. "
Shekaran babansu talatin akan mulki Allah yamasa rasuwa, alokacinne Gashi babban d'ansa baiyi aure ba."
Shine aka samu yar gidan k'aninsa mahaifinsa wanda yariga mahaifin nasa rasuwa. "
Aka daura musu aure badan yana sonta ba."
Sannan aka damka masa sarautar k'asar kano. "
Mutane sunajin dad'in mulkinsa dan halinsa d'aya sak da mahaifinsa."
Talakwa kai hadda ma masu kud'i suna yabawa kwazonsa. "
Shekararsu d'aya da aure Allah ya azurtasu da yaro namiji, asaka masa isma'il sunan mahaifin kilishi, sosai yaron yariga ran mutane, magajin sarki."
Iya gata yarima isma'il naganin gata sosai. "
Alokacin tanada cikin secound born d'inne yad'auk'eta, zuwa dubai (abu dhabi) danyin shopping."
Wani tamfasetsen shago sukaje dake cikin marina mall (abu dhabi) . "
Shagon duk kasuwar yafisu girma, kowani kalan zinare kakeso awannen shagon daka sameta, duk prize dinsa."
Nufan shagon sukayi dan sayan zinare, bayan sunshiga, ne kilishi tafara za6a. " alokacin wata yar yarinya tashigo, wanda asa'anni zata Iya kaiwa kilishi, dan auren wuri akayiwa kilishi tuntana 15, gashi yanzu almost 3yrs da aurensu."
Kallon yarinyar yatsayayi dan lokaci d'aya yaji yakamu da sonta luv at first side. "
Hartagama abinda zatayi tafice, dawayo yabi bayanta, yaje yasameta, bata nuna kyankyaminsa nakasancewa bakar fata ba."
Kwatancen gidan su tamasa be dauki lokaciba yaje dafarko iyayenta sunki yarda, hqr takaiga kullum, yana kofar gidan amma bbu mai kulashi. "

Ita kuma Allah yadaura mata sonsa sosai, yadda kullum cikin kuka take."
Takurin daya ke musu ne yasa suka yanke shawarar bashi amma sai sunyi bincike. "
Binciken da sukayi ne ya nuna musu matsayinsa bakaramin mamaki sukayi na ganinsa babban mutum amma yake irin kwantar dakaiba."
Dan mahaifinta yasan kasar kano kuma yasan irin mutanen dake cikinta. "
Amma ace wanda yake mulkarsune ya kwantar dakai wajn neman auren 'yarsa."
Haka akaturo magabata aka gama komai. " kilishi
Bakaramin tashin hankali ta shigaba da wannan zance."
Sanin bawani sonta yakeyiba yanzu kuma yasamu wacce yakeso, kuma balarabia. "
Da zigin mahaifiyarta suka fara shiga bokaye da sunan malamai amma bbu abinda yafasu dan aurekam sanda akayishi." sai bayan aurnne yasan cewa wannan shagon daya ganta ashe

shagon mahaifinta ne, sosai yake iya gwargwado na nuna adalci atsakaninsu. "
Amma duk da haka kilishi tananan da kishinta, saidai kokad'an batada bakar zuciyarda zata cutarda raheema (ummii)."
Hakadai zamnnasu yake ita bawani shiri sukayi ba amma kuma ba fad'a ba. "
Bayan auren da wata biyu da koma Dubai dan k'arasa karatun ta."
Tafiyanta ta da d'an wata hudu kilishi ta haihu ta haifi mace, yamayar mata da sunan kanwarsa khadija. "
Ummii tazo suna, gama ta arkizi ta had'o mata dan harda zinare."
Lokacin ita kuma cikinta na kinamin wata biyar. "
Ganin cikin baid'agawa kilishi hankali ba dan tasan ko yanzu itace da gida."
Bayan wata hud'u tagama karatunta. "
Ak'asar haihuwa ta sameta."  anan ta haiho danta namiji kyakkyawan gaske. "
Kafin suna suka dawo Nigeria."
Asuna yaro yaci sunan kakansa Abudullahi. "
Iya buduri anyishi,
Wanda kowa mamakin hakan yakeyi dan ko sunan isma'il yareema, ba'ayi buduri haka ba."
Aikuwa yaron yashiga ran fulani, mahaifiyar mai martaba. "
Kullum yaron yana wajanta, hakan kuwa bakaramin k'ona ran kilishi yayiba,"
Wajen mahaifiyar ta taje ta shaida mata da kuka. "
Ran mahaifiyar ta yabaci tana ganii ga wanda yafito d'an dangi nan sai wani bare zataso."
Bayadda basuyi naraba shi da itaba amma abu yaci tura haka dai aikinsu baiyiba su kuma basu hakura ba. "
Yafara girman a kullum kyawunsa ne yake dad'a fitowa."
Yanad'an shekara shida aka daukeshi zuwa makaranta a russia. "
Fulani kuka tayi tayi akan baza'a kaimata jika kasar arna ba amma haka bayadda ta'iya, haka Ummii ba bawai taso bane."
Kowani bawan Allah yaji wannan abu saiya tsaya jimami ace yaro tunyana karami da'a daukeshi zuwa wata makaranta. "
Haka dai aka tafi dashi bawai danran kowa yasoba, abinda yad'an  ragewa Ummii zafi dalilin lokacin ta haifi afeeya."

Sai bayan shekara shidda, kafin yake dawowa hutu, sai dai iyayenshi suna zuwa wajenshi, makarntar ta sojoji ne tun suna k'anana ake kaisu, yakanyi wuya asamu wanda ya fara tundaka farko har ya gama." wasu idan suntafi hutu basa ta6a dawowa, wasu kuma yawanci da girman su suke zuwa ba rainon makarntar bane,
duk hutunda yazo yakanyi 5-6 month kafin yakoma. "
Shekara shidan farko yadawo yasamu labarin mutuwar yayansa, yareema isma'ill sakamakon

hatsarin mota."
Sosai mutuwar tashigi 'yan gidan dan yafara girman yakai kusan 16yrs lokacin. "
Shima mutuwar ta shigeshi sosai dan Kowani zuwanda za' ayi masa tareda yayansa ake zuwa."
Daga nan kuma duk wani soyayya ta tattaro tadawo kansa. "

Shekaransa 18 a makarantar alokacin yagama inda duk yanda sadauki da jarumta takai to yakai, masu karatu basaina tsaya yimuku vayani ba kunsan yanda sojojin rusia suke duk duniya bbu sojojin da suka kaisu horuwa, kuyi imagine wanda yayi shekara 18 yana horuwa akasar."
Duk ciki su uku ne suka fita shine wanda yazo nafaarko. "
Dan tunda suke ba'atabayin jarumin d'alibi kamarsa ba."
Hakanne da suka gani sun tabbatar idan yatafi k'asarsa wannan horo dasuka masa yatashi abanza. "
Ganin Hakanne yasa suka ce sudasu rikeshi."
Aranda akazo passing out dinsu ne, alokacin duk wani family dinsa sun hallara. "
Mamaki ne yacika mutanen gani duk bak'ak'en fata ne danginsa."
Sunga su kansu ma yafisu kyau. "
Duk wanda akagani awajen taron har inde daga family din MG yafito to karramawarsu dabannee."
Kowa nema yake ya gaisa dashi ko family dinshi,
Duk wani kyauta shiyasamesu,
Inda kasashe da dama suka bid'ar yamusu aiki. "
Ganin Kowani kasa na bukatarsa yasa, kowacce tasa hanu aka bugamar starm na sojan k'asa da k'asa."
Haka taron ya watse kowa na farinciki,
Barin family na MG dasukejin kansu asama. "
Tunda intisar tad'aura ido akansa, taji tanasonsa, dafarko yad'an fara kulata, amma tunda yayi wata yafiya yadawo yabirkicewa kowa dan ko kallon arziki bata samu."

Sadam ne yad'an nisa sannan yace "
Ayanzu haka labarin da nake baku, yaran mahaifinsu shida, khadija, abudullahi (MG), afeeya, affan halima da labba.

Sannan ya nisa yace wannane takaiceccen tarihinsa."
Daya daga cikinsu ne yace, amma duk wani pics da labarin bbu hoton wannan yarinyar aciki. "
Me hakan yake nufi kenan?"
Ita wacece idan ba daga cikin family dinsa takeba? "
Dayanne yace tabbas tana da mahimmanci awajensa, dan wayanna sojojinsa ne."

Sadam ne ya nisa sannan yace, tabbas dan alabarinda muka samo mungano tun shekarar daya dawo biyu daga cikin sojojin sa are missing kuma haryau bbu wanda yasan yanda suke. "

Nisawa yayi sannan yace toh kanemo mana ita wannan yarinyar wacece?".

To be continued

Ur's
_Z33yyb3rwr3r_

[12/2, 9:28 AM] Anty Jamila D Ili: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

My first novel

Page 35

*
Ahaka suka k'are meeting d'in, akan za'a nemo musu wacece ita?" kuma menene alaqarsu da ita? "

Haka yau takasance ma, agun anty samha ta kwana, su amira sun bata hakuri amma kaman bada ita sukeyi ba."
Haka yau ma takara mulke jikinta da had'i, sannan suka kwanta. "

Amma kokadan bata bawa anty samha kofar da zata mata maganar najeeb ba. "
Dasafe kuwa wani irin kyau tayi fiyeda najiya, kuma yau takasance ranar da za'afara event. "
Mama kasa hakuri tayi sanda ta tanka." ke wai mai kika fara shafawane kam?"
Turo bakinta tayi, "
Zaki fad'amun ko saina bige wannan bakinkin?"
K'in mayarda bakin tayi tak'ara turoshi, "
Tashi tayi da niyar bigeta, ganin haka yasa takwala ihu."
Aikuwa dama umma nawajen, "
Tashi d'aya tafara tahaukan Mama ta masifa,"
Ke banasan shashanci kina jina ko? "
Ina ruwanki da kalar da tafanta tayi?"
Hava yaya kikalleta fa sai kace wata mai bleaching ki kalla yadda fatarta tayi haske? "
Umma ce" tace yanzu ke aisha haryanzunki bazaki iya, bambamce farin bleaching, dana gyara ba? "
Toh tare ake musu gyara itada samha."
Jin hakane yasa hanklain Mama kwanciya,"
Hmm kawai Mama tace daganan bata sake cewa komai ba. "
Shiga d'akin su amira tayi, duk d'insu sakewa sukayi kamar wanda bbu wani abu dan sukansu fushin da sukayi kowa yaji jiki, hira sukeyi sosai, can wayar ta tafara ringing ganin anty samha ce mai kiran yasata saurin amsawa."
Hellow" anty, "
Kuzo d'akina kedasu amira, bbu 6ata lokaci ta shaida musu kiranna anty samha Tashi sukayi suka nufi d'akinta."
Shiga suka yi tana kan gado. "
Dawasu kaya awajenta."
Zama sukayi, harhad'a kayan tayi awata jaka mai kyau sannan ta d'ago ta dubesu, mikawa *hanna* jakar tayi, gashi dan Allah yanzu kukai fadah, fad'a baki sukeyi dukkansu suka ambaci fadahh?"
Eh " kanwar sace yar gidan sarki tadawo daga school kuma duk wani ankonta awajena yake, kunsan zuwa jimawa zata buk'ace su."
Ta6e baki amira tayi to ai anty sai abawa driver yakai mata danni wallhy bansan rainii takareshe maganar tana kawarda kanta gefe,"
*Hanna* kan wayarta tafara dannawa dan tasan wannan zancen bamai yiwuwa bane."
To ke anty ita baza tazo ta kar6a da kanta bane? "
Ko tsabar sarautar ne sai ankai mata?"
Dan Allah ni basaina tsaya magana ba idanna isa daku kukai mata. "
Idan kuma bazaukai ba shikenan."
Dan akwai abunda zata baku kuzomin dashi ne. "
Haka badan ransu yasoba suka tashi danzuwa kaimata,
Kuma abinda yafi ci musu raima shine wai ba driver bane zai kaisu a taxi zasuhau futa sukayi kowa sai k'unk'uni yakeyi."

MG ne zaune agaban mai martaba da'alamu bakinsa akwai magana sosai amma haryanzu yak'i cewa komai. "
Ganin haka yasa mai martaba ya sallami duka 'yan palace d'in."
Juyawa yayi ya fuskanci MG, sannan yace "
Yareemana da' alamu bakinka akwai zance dayawa amma kayi shiru."
Maza fad'amun damuwarka kasan idanba niba bbu typing wanda yadace ka fayya cewa damuwarka. "
K'asa yayi da kansa yanad'an sosawa ganin haka yasa mai martaba murmusawq,"
Yanajin dad'i MG ya tambayeshi abu duk girman abun yana iya barmasa. "
Ehem go ahead my son tell me, yafad'a a lokacin dayake ta6a kafad'arsa,"
Cikin alamun Jin kunya yace "
Dama abba inaso aje nemamun auren *hanna* ne."
Mai martaba bayyi tsammanin zancenda zaifuto abakinsa bakenan, baisan lokacin da ya mike ya zauna daga ki shine giden dayake. "
Cikin zumudi yafara magana, son da gaske kake?"
Allah nagode maka daka nunamin wannan rana, "
Nayi farinciki wanda nikadai nasan irinsa."
Yareema akullum ganin nakeyi kawai kana fad'in kakusa aurene dan ka kwantar mana da hankali, dukda cewa hakan amma idan kafad'a hankalina yana kwanciya, amma yau Allah ne kad'ai yasan irin farinciki da nake ciki, Allah yamaka albarka kuma yasa Alabarka azamnatakewar auranku. "
Cikin ransa ya amsa da amin."
Fad'amun yar gidan waye, zuwa gobe nasa amin bincike, dukda nasan cewa bazaka ta6a za6ar macen da batada tarbiya ba amma hakiinane amatsayin mahaifinka nayi bincike akan ta da mahaifinta."
Cikin ladabi yace Abba ai 'yar gidan wan mahaifin matarda Abubakar zai aura ne. "
Ikon Allah kenan wato duk wannan tsawon shekarunda muka dauka, kasanda cewa tanada kanin mahaifi anan?"
Gyad'a kansa yayi eh abba. "
Rashin sanine aida lokacinda akaje tambayan na Abubakar da anhad'a duka."
Amma yanzu komai da zafi zafi akeyi barina kira modiibo."
MG ne yad'aga wayar yamasa dialing ring uku aka dauka. "
Cikin girmamawa ya gaida middibbo, ya amsa Cikin kulawa."

Moddibbo aminin mahaifin mai martaba ne tsoho mai farar aniya, kuma babban malami duk wata amanar da sarki abdallah yabar masa, sanda yatabbatar yacikasu. "
Bayani mai martaba ya koro masa,"
Sosai ransa yayi fari dan murna har sujjudur shukur sanda yayi. "
Cikin farin ciki yace"
Allah yacikaman burinmu dazafi zafi zamuyi komai,"
Ran auren Abubakar sai muyi magana. "
Kannan muci gaba da addu'a Allah yacika masa burinsa dan idannasa yacika namu yacika."
Ahaka sukayi sallama kowa ransa farii tass. "
Nan da nan mai martaba yafara kiran dangi abunnema yasamu," Cikin yan mintuna kowa sai kira yake dan gaskatawa. "
Ummii dabatasan labarin mayyake faruwaba, kira kawai take gani ta ko'ina."
Kashe wayar kawai tayi dan batasan surutu. "  ni saida abinma yabani mamaki sai kace wanda akace yau ne d'aurin auren."

Su *hanna*  ne tsaye a kofar shiga fadahh, rigima sukeyi dan sunce bbu wanda ya'isa yasa Su cire takalmi, sunkai kusan 30 minute a kofar wajen har takai ga yanzu wasu dogarawa sunzo da niyar korasu. "
Tana kallo captain bala dake biye dasu tundaga gida."
Wajen dogarawa taga yanufa, "
Magana yamusu sai gasu sun nufo wajanta,"
Suna zuwa aikuwa hakuri suka fara basu, kamar wanda zasu tsugunna. "
Sannan suka umurci d'aya daya musu iso."
Hakan kuwa akayi." Suna shiga nan kallo yakoma sama ai basu ta6a tunanin fadan babban gari bane acikinta. "  sanda sukayi tafiya mai nisan gaske kafinnan suka isa wani sashi mai d'an karan kyau."
Adai-dai lokacin MG yafito daga kofar mai martaba. "
Gabantane taji yayi wani mugun fad'uwa sakamakon had'a ido dasukayi."
Saurin komawa baya tayi tariqe hameeda gam. "
Shikuwa d'auke idonsa yayi kamar baita6a kallonta ba."
Gani tayi daga fitowarsa sojoji sun masa runfa, tunani dama wato agidan sarauta yake, yatsine fuska tayi Sannan tace shiyasa yafiya girman kai. "
Tsaki taja mtsww wanda har yafito fili Suka juya Suna kallonta."
Ganin ko'ajikinta batamasan tayiba yasasu juyawa sukaci gaba da tafiya. "
Shikuwa anasa 6angaren baiyi mamakin gainta anan ba dan yanada tabbacin aikota akayi."
Wani plat suka nufa mai shegen kyau, dan tsarin baiyi kama da tsarin gidan bahausheba. "
Sak yanda larabawa sukeyin gidansu duk glass."
Tsayawa yayi abakin k'ofar sannan yayiwa wata kuyanga magana akan tayi musu issoh. "

Wani falo tashigar dasu falon bbu tarkace dan mai shashin batacikason yawan kayaba,"
Sai dai komai na falon classical ne. "
Juyawa tayi zata wuce, Saurin tsayarda ita amira tayi sannan tace wurin labba mukazo."
Amsawa tayi da kayi sannan tashige wani sashi.
Kafin d'an wani lokaci anchika gabansu da kayan marmari dasu drinks,
Ko kallon wanda takawo basuyiba balle sannu ransu yakai kololuwa gun baci, dan rainin hankali tawani shanyasu. "

Aiko ba komai sai tazo takar6i aikanta dansu bazama sukazoyiba. "

Can kusan tak'ara ten minute akai sai gatanan tafito."
Dan lokacin har amira tamike da niyyar fita, " ganin bazatafi sa'arsuba yasa ransu k'ara baci,
Karasowa tayi Cikin sakin fuska, binsu d'aya bayan d'aya tayi tana hugging nasu Cikin murna, nan tafara magana, dan Allah ku gafarceni nashiga wankane, ita kuma tatsaya jirana batazo ta sanar da Ummii ba ku gafarceni. "
Duk cikinsu bbu wanda jikinta baiyi sanyi ba ganin yadda sukayi tsammani ba haka suka sameta ba."
Hanna ce tace wallhy bbu komai dama sak'one, anty samha ta bayar akawo miki,
Cikin fara'a tasa hannu takar6i aikan godiya take surfawa, duk da cewa wannan bawani abu bane, amma tayi appreciating sosai. "
*_Hanna_* ce take satan kallonta ko tabbas kama sukeyi sosai da wannan mutumin,
Itama kyakkyawace ta ajin k'arshe ."
Saidai MG yafita kyau😜. " hameeda ce ta mintsini amira ta niyyar tatashi, amira tashi tayi,
Hava dan Allah badai tafiya ba?"
Eh wallhy muna sauri ne inji hameeda, to muje ku gaisa da Ummii, da kin gaisheta kawai daganan aika zamuje,
No aibazataji dad'i ba idanna fad'a mata, badan ransu yasoba suka nufi wani shashi, afalo suka sameta, wata kyakkyawar balarabiya suka gani mai kmada labba, tana kallonsu tasake fuska,
Sannan suka k'araso gaisheta sukayi, ta amsa Cikin sakin fuska,
Ummii kinga abinda suka kawomun, a'ah😃 to angode Allah yasaka, ta fad'a tana kallon *hanna* wanda tun shigowarsu yarinyar ta d'auki hankalinta, kuma tarasa dalili,
Tashi sukayi suka mata sallama,
Hava my doughters kujira zuwa jimawa mana, dan har Cikin ranta batasan tafiyar *Hanna* jitakeyi kamarta dad'e da saninta, kud'i ta d'auko mai yawa tabasu amma bayadda batayiba sukak'i kar6a. "
Ganin hakanne yasa tayiwa labba magana, sai labba tajuya samun kanta tayi ta riqe hannun *hanna* dasuke niyyar fita, lallausan hanu mai taushi ne taji ya riqeta, saurin juyawa tayi sukayi

idoh hud'u dana Ummii, saurin yin k'asa da kanta tayi dan haka kawai takejin nauyin matar, had'a idonda sukayi kuma yasa tajii wani iri kamar wanda tataba kallon kwayar idanun awani waje. "
K'ara damk'e hannun ta tayi my doughters, dagowa tayi tasake kallon ta sannan tak'ara sadda kanta k'asa,
Menene sunanki?"
Ita kanta batasan lokacin da tamabayar ta fito abakin taba,
*Hanna* tfad'a Cikin girmamawa da jin nauyin wanda akeyiwa magana,
Alhmdllh tafad'a a zuciya a fili kuma tace, sunanki da dad'i, nagode tafada ahankali,
Juyawa tayi gunsu, amira nan ma ta tambaya kowa ya fad'a mata, albarka ta samusu, anahaka labba tafito, itada wasu kuyangi da ledoji a hannunsu, har lokacin hannunta na riqe dana *Hanna* nan ma dakyar suka kar6a saida sukaga ranta ya6aci. "
Dakyar tasaki hannun ta hakan ba karamin mamaki yabawa Hanna ba,
Direba akasa yakaisu har gida, anan akayi tamusu fad'an kar6an kayan da sukayi."

Aikuwa yaje yasamu Abba ya fad'a masa."

Abba ne yace amma yaya gani nayi kamar yayi wuri dasun bari nan da zuwa koda satii ne sai,
"
Suzosu kaga yanzu bawani shiri mukayi ba."
Babane yace nima abinda nagani kenan,  amma idan mukace wani abu zasuga kamar basan abun mukayi ba. "
Kuma ni maganganunda yarinyar nan ta fad'a ranar auren samha sai ina kallo kamar akwai wani abuu ak'asa,"
Kaga kuwa yakamata mu amince musu ayi wannan zancen da wuri kamar yanda suka bukata."
D'an gwauron numfashi Abba yaja sannan yace nima nayi tunanin hakan dan inaga akwai masu yiwa yarinyar nan ba dai-dai ba tunda dakanta tace aidama tasan bazasu barta ba, "
Acika mata burinta kamar yanda ta bukata abarta tazauna haka,"
Ai yaya kanajin wannan magana zakasan da wani abuu ak'asa, "
Kuma ta iya yiwuwa yanzu haka ita yarinyar tajii da kunnenta ne yasa ta fad'ar haka."
Dan ni gaskiya yaya bazan 6oyeba gidankanna bakowa nayarda dashi ba kawai abun yafi yanzu mudage da addu'a sannan kuma musa ayita mana saukar qur'ani, "
Kasan mutum kai baka damu dashi ba amma kai yadamu da rayuwarka."
Baba ne ya nisa sannan yace toh Allah yataimaka sai musan abinyi dan nasan zuwa jimawa zasu iso. "
Shiga Cikin gida sukayi,"
Suka samu mama da umma kud'in aikin da za'ayi na Cikin gida aka basu sannan su Abba suka wuce dan tanadarwa bak'i snacks da kuma drinks, "
  Saleem ne ke fitowa daga dakiin su, Alokacin abokinsa yakirashi dan tun jiya sai samun kira yakeyi,"
Wa'yanda da ba frndz nasa bane, wanda then suna kallo mahaifinsa baida kud'in da zasuyi abota dashi yanzu haka sai kiransa sukeyi,"
Sunaso su jonehh. "
D'aukan wayan yayi cikin gadara."
Daga can Cikin wayan nayi ance palz yadai naji wani labari wai dagaske ne? "
D'an gyarawa yayi yafara koro Bayani yanayi yana wani gadara,"
  Aikuwa duk abinda yake fad'a a kunnen Ammah datake zaune abakin kofa,"
Rikicewa tayi wai metake jine waishin dagaske *hanna* aure zatayi?" kuma dan gidan sarkin kano zata aura?"
kamar yanda tajii Saleem yadad'a, "
Afili tace kai ina haka bamai yiwuwa bane."
Shikuwa Saleem baimasan tanayi ba."
Can garin kano kuwa MG harya gajii da amsa call, dan governor's minister's  ambasador's da president, "
Na k'asa she daban daban sai kiransa sukayi suna mai murna dan abu kamar wasa yabaza duniya sosai,"
Dayawa mutane ke sharing wannan video d'in. "
Aranar kuwa followe'r kamar zasu cinye, amira da hameeda."
Kai har takaiga radio's station, "
Tv chennel's,"

Bana k'asarnan zallah ba har na k'asa she da yawa."
Zance gabki d'aya ya karad'e duniya. "
Kowani tasha kika bud'e labaran kenan." MG daya gajine da recieving call, kawai sai ya yanke call saidai massag gashi har yanzu yan wshing basu barshi ya d'an samu tym yakira *hanna* ba. "
K'anin mai martaba ne zaune a falon mai martaba,"
Magana yake yi, yana cewa, "
Yaya aduba wannan lamari gaskiya baida ce ace ya auri yar gidan talaka ba."
Mahaifin yarinyar fa malamin makaranta ne,"
Kaduba matsayi da dukiya irinna yareema ga mulki, arasa wacce za'a aura masa sai yar gidan malamin makaranta yanzu yaya maiyaci yabawa iyalinsa har za'a gani ayi sha'awar aure? "
Ran mai martaba in yayi dubu yab'aci, dan irin maganganun da k'aninsa yake fad'i ya6ata masa rai,"
Amma dayake dattijo ne mai hakuri yasashi sharewa yabarshi yaci yacigaba da cewa ai wannan yakamata yayi tunda munada 'ya'ya mata sai qhad'ashi da d'aya aciki, "
Mai martaba ne ya nisa sannan yace,"
Mai dukiya dakuma talaka duk Allah ne yayisu, "
Kuma inaso kasani koda yar bukka yareema yakawo yace yanaso toh ita zan aura masa."
Balle mahaifin yarinyar yanada rufiin asirinsa duk abinda ake nema wajen aure to wannan yarinya da mahaifanta suna dashi addu'a yakamata muyi Allah yasanya alkhairii acikinsa. "
Duk da bahaka yasoba amma jikinsa yayi sanyi." Ammah bata tsaya ko inaba sai gidan kawar ta aminiyarta,"
Hajiya lamii tana zuwa tafara mata birgima tana cewa wallhy malam yacuceni duk kud'in da nake she ace baimin aiki mai kyauba, "
Shege dan iska halama boka ne," 😳nikuwa nace kajimin amman nan dama ke atunaniki wajan malami kike zuwa toka kin yaudarii kankii. "
Dan wannan ba malamii bane."
Hajiya lamii ne tayita rarrshinta sannan tace tayi hakuri su k'ara jarrava wani suganii,"
Cikin kuka Ammah tace mai nake dashi dazanje wajan wani kefa kina kallo na tattare duk kada rori na nasayar naba wannan macucin,"
Menake dashi dazan je wani waje,"
Cikin lallashi tace mata kiyi hakurii mutafii wani kauye abincika kinsan irinsu basusan zqfin kud'ii ba sai mu bincika."
Cikin d'an gamsuwa da maganar ta Ammah tayi shiru sannan tace to yanzu yaya zanyi tace kodaiyaya kisan yanda kikayi kika nemo kud'ii koda bbu yawa, "
Gaki da yara ai Had'a musu wuta zakiyi sai sun nemo miki."
Ahaka sukayi sallama Ammah tatafi bayan tagama kitsa mata makircii."

Can wajen su umma kuwa sunanan suna shiri iya dai-dai gwargwado sunyi k'okari sosai wajan tanadarwa da baki abun buk'ata. "
Alokacinne anty maman amal tace ashirya *hanna* dan tasan dangin sarauta yanzu haka da mata za'azo kuma zasu bukqcii ganinta,"

Governor na garin bauchi kuwa yasha mamakin ganin cewa MG yasauka agarinsa batare da yasani ba, "
Amma yanzu ankirashi akan cewa jirgin mai martaba yakusa sauka,"
Hakama yakira abokinsa sarkin bauchi yasanar dashi. "
Aikuwa nan ma aka fara shirin tar6an sa."
Duk ilahiran masu tarban sarkii sun hallara a airpot na Abubakar tafawa balewa."
Kafin su taso daga kano kuwa sanda zance yakai kunnen fulani kakar MG bakaramin farin ciki tayiba, "
Tunda tajii zancen zuwa tace ai atafar sai anje da ita zataje taga jikanta."
Dake tana samun kulawa sosai kuma ga kud'ii yasa tsufanta baiyi yawa sosai ba. "
Aikuwa hakanne tafaru aka shirya hadda gwaggonsu khadija k'anwarsu mai martaba da sauran 'yan uwah zuwa garin bauchin yakubu."
K'arfe 12 :00 dai-dai jirginsu yasauka a airpot, "
Kai tsaye fada suka wuce,"
Basu d'auki lokacii ba akayi gidan su *hanna*, "
Alokacin angama shirye komai dan, har Abokan baba samada biyar sun zo tar6an baki da kuma wasu dattijai,"
Yan anguwarsu duk aka had'u, "
Isowarsu ba jama'ar anguwar ba kad'ai har makwabtan anguwar fitowa sukayi dan ganin wa'yannan mutane ak'ofar gidan da suka sauka ne yasa mutane shan mamaki basu k'ara sarewa ba sanda sukaga har Governor awannna tafiyar."
Da fara'a su Abba da sauran dajjijan nan suka fito suka tar6e su Cikin amince, "
Suka wuce falon Abba dasu,"
Su kuma matan Cikin gida suka wuce aka wuce shashin mama dasu,"
Ammah ta window take leqe yayinda wani irin bakin ciki yacika ta har wani dushu dushu take kallo. "
Data sani takeyi marar adadi dabata rabata da najeeb ba da tabarta dashi akan ace ta auri wannan dan banzan mai kud'in." abin bakin ciki ma yanda algaitu ya ciki anguwar tako ina algaita ansan dangin sarauta sun shigo, "gaba ki d'aya anguwar sai ta d'auki kamshii dan duk yanda suka wuce akwai masu bin wajan da turaren wuta na gaushi. haka al'adinsu yake har indai za'aje neman aure a gidan sarauta to anguwar sai tasan da zuwansu."
Jiri ne yafara ebanta Aikuwa awajan ta sulale ak'asa Batasan yanda takeba. "
Gashi hafsat tatafii makarnat rabi'ah kuma tana gidan anty maryam jiya da tazo tare suka tafii."
D'aki aka shiga nan akafara gaigaisawa Cikin mutumta juna."
Nan da nan bada 6ata lokacii ba suka fara abinda yakawosu lokacin an kawo musu kayan motsa baki, "
Alokacin Momy kadija kanwar Abba tatashi tafita sai gata tashigo da dogarawa har guda goma sha biyu kowa da akwatii ahannunsa yashigo dashi ajiyewa sukayi sunayi suna kirari a matar yareema ahaka suka gama suka fice da baya-baya,"
Kallon kayan suka tsyayi nan aka musu bayanin kan cewa kayan naganii inaso ne. "
Nan mama tace ai atafar kayan sunyi yawa saidai arage,"
Fulanii ce tace ai matar yareema ta cancanchi fiyeda haka dan haka k'arna k'ara jin wannan abun ai muma yar muce. "

Ahaka sukayi ta hira kamar da ansaba da juna."
Fulani ce tace aishin zaku kawomin kishyata naganta ne kosai nabi duk dakunan ina bincikawa, "
Dariya dukansu sukasa Momy khadija ne tace wa Fulanii,"
Umma wannan kishiyarde ta tsorataki tun daga jinta kika rikice gabaki d'aya saikin ganta. "
Dariya duka d'akin ak'asa sannan Fulanii tace to ba dolena naji kishi ba,"
Tanason kwacemun wannan had'adden miji wanda ni kad'ai keda irinsa. "
Nanma dariya akayi sosai, sannan anty mmn amal tatashi tashiga d'aya daga Cikin d'akunan,"
Can jimawa tafito hannunta riqeda *hanna* kanta rufe da qyale amma fuskanta abud'e yake kanta yana k'asa, "
Tundaga nesa suke kallonta suna masha Allah,"
Dan *hanna*  tayi kyau sosai."
  Zuwa tayi ta zauna acan d'an nesa dasu tafara gidansu ahankali Cikin fara'a suka amshe yayinda Momy khadija taja hannunta zuwa gabanta, "
Tsugunawa tayi ta rungumeta sannan tace welcome to our family dear,"
Hakan kuwa ba karamin dad'ii yayiwa su mama da umma ba sunsan sunakai 'yarsu yanda ake sonta Ahaka kowacce mata tayita rungumeta Cikin farin ciki. "
Daga k' arshe fulani tariqeta gam kamar za'a kwaceta tana cewa aikwa bari mu gaisa ko,"
Aikuwa *hanna* taji dad'ii janta datayi yisukeyi kamar zasu cinyeta dan kowanne acikinsu murna sukeyi sunga matar yareema pics kam alokacin tasha bbu adadii. "
Fulani kam riqeta tayi gam tana cewa Allah yamiki albarka,"
Allah yamiki albarka, abunda take nana tawa kenan hannunta na riqe dana *hanna* duka biyun wanda hakan sanda yayi sanadiyar da yasa *hanna* zubda hawaye. "
Data tuna lokacin da ko mashinshini bata da shi har abin gorii yazama sai gashi waiyau itane Cikin dangin mujinda zata aura suna sonta kamar su halaka."
Fulani ne talura da hawayen ahankali tasa gefen gyalenta ta share mata bata bari kowa yaganii ba ta Girgiza mata kai ko ba'a fad'a ba tasan kukan farin ciki takeyi. "
Dan duk wani labarinta moddibbo yasanr da fulani shi yasa takejin son yarinyarda tausayinta."
Maza kuwa suma awajensu sungama yanke shawarar za'ayi aure nan da wata d'aya da satii biyu. "
Ahaka Cikin farin ciki aka gama komai kowa sai yaba halin kowa yakeyi dan daga wajen kowa anga halin karamcii," Daga mata aka futo da huhun goro da caton na mint da dabino, kowane gida abinda ake kaimusu kenan, "
Duk anguwar bbu gidanda baisamu huhun goro da caton d'in mint dana dabino ba kuma,"
Kuma ko ina idan aka shiga sai an shaida musu cewa na neman auren *hanna* ne, "
Duk gidanda aka shiga sai anyi mamaki dan tunda suke sunsan ba'at6a sallama ta cewa anzo wajen *hanna* ba sai gashi yau dogarawa ne ke raba goronta kuma wai hakanma goronda za'akai na neman auren wata shine ake rabashi kowane gida,"
Bayan angama komai suka fito sukasa akira musu matan su tafii. "
  Nan wani bafade yashiga yasanar dasu da suka taso tafiyane fulani ta bud'e gyalen *hanna*ta cusa mata wani d'an karamin akwai sannan aka fita rakasu."

Bqyan sun tafii ne ya auwal yayi waya ya shaida musu tun jiya adda hindu ta haihu, ta haifa

d'anta namiji wanda tun jiya yaki fada ne dan bayaso yaraba musu hankali. "

To be continued

Ur's
*Z33yyb3rw3r*
[9/24, 8:45 AM] +234 810 367 2210: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

*Alhamdulillahi am feelling much better,"*
*Thank u all for d du'a, care.* *Massages, luv."*
*Luv u all* ❤. "

Page 48

*
Murnane ya 6arke agidan, ga murnar auran *hanna* ga kuma na haihuwar adda hindu."
Basu tsaya jan lokacii ba aka shaida masa akan ana sallamarsu su wuce bauchi. "
Dan ga baki d'aya yanzu zaman su zaifii yawa a bauchi tunda shirye shiryen biki za'a fara duk da da d'an sauran lokacii amma kuma yakamata komai afara tanadinsa da wuri."
Awashe gari kuma abba zai wuce kano," domin aikinsa. "
Umma kuma sai anyi suna zata koma."
Da yamma su adda hindu suka kamo hanya itada yaya auwal, "
Alokacin da su abba sukaji bakaramin fad'a sukayiwa su umma ba."
Abba ne yana fad'a yana cewa inbanda shashanci yarinya da d'anyan jego zaku d'aukota kuma jegon farko ko wanka bata samu ba. "
Fad'a sosai abba da baba sukayi,"
Hakuri kawai suke bayarwa dan suma yanzu sun fara danasanin cewa suzo da sukayi ga gari

da nisa tsakani tafiyar samada 3hour. "

K'arfe shida dai-dai hafsa ta dawo daga makaranta,"
Ganin mutane cin cirindo acikin gidansu suna fitowa daga shashin mama. "
D'akin ammah tawuce nan tasamu ammah afalo a sume da gudu takarasa tana fad'in ammah, ammah, jijjagata tafarayi ganin bata ko motsi yasa tanufi fridge da gudu ta ebo ruwa ta fara yayyafa mata."
Koda ta yayyafa mata wata nauyayyan ajiyar zuciya tasake, "
Can kuma kamar wanda aka zabureta ta mike tana cewa na shiga uku wallhy boka ka cuceni daka bar yarinyar nan zatayi aure kuma dan gidan sarki Allah ya'isa tsakanina dakai."
Nan tayi shiru tafara dube dube afalon nan idonta yadauka kan hafsat da take binta da kallon tuhuma. "
Mai Mai ta kalmar tayi tace boka," boka fa kikace ammah? tana magana kuka na k'okarin kwace mata, "
Ammah dama kina zuwa wajen boka dan ya cutar min da 'yar uwa?"
Cikin in ina ammah tace um um malami nefa fa, "
Cikin kuka da tsawa hafsa tace ina bambamci ammah har indai zakije wajan wani da sunan ya cutar da d'an uwanka wallhy bokane ba malami ba," Cikin kuka tahad'e hannuwanta biyu👏 ammah na rokeku kudena 6atawa malamai suna idan zaku kirqsu da bokansu yafi, d'an jan numfashi tayi sannan taci gaba da cewa, "
Ammah nifa *hanna* bawai bana sonta bane karkiyi tunanin bazanji zafin cutarda ita da kikayi ba wallhy ammah dole sai naji zafi dan 'yar uwa tace,"
Hasalima abinda yasa nakejin haushinta irin yanda baba yake nuna bambamci atsakanine, bayaga haka bbu komai soyayyarta nanan dan k'are azuciyata."
*(gaskiya iyaye yakamata mu kula duk irin soyayya dake tsakanin yara har indai zaka nuna kafison d'aya ko kuma kafi kula da d'aya to jin haushin 'yan uwa zaishiga tsakani dan Allah iyayenmu akiyaye." nuna bambamci d mahaifin *hanna* *yakeyi tsakani shiyakawo jin haushi tsakaninsu amma bawai dan' d'aya baison d'aya ba dan Allah zank'ara roqon iyayenmu akan mukiyaye hakan idan yayi tsananin har gaba yake haifarwa tsakanin 'yan Uwa)*
Jikin ammah ne yayi sanyi, wani irin nauyin d'iyarta ne ya rufe ta, "
Yarda tahaifa itace ke gaya mata gaskiya."
Duk ilahirin gidan na tsaye abakin k'ofar ammah duk jikinsu yayi sanyi jin abinda yafaru,"
Shiga ciki sukayi nan idanuwan ammah yafara zuru-zuru kamar wanda tayi k'arya kodayake ai abinda tayi yafii k'arya. "
Kowanne yasamu wajen yazauna abinda su ammah basu saniba shine tun farkon fara maganar suke tsaye,"
Dan zuwa hafsa ganin mahaifiyarta akwance saita sakee k'ara wanda itakanta batasan lokacinda tayiba hakan yayi sanadiyar janyo hankalin gidan, "
Sun zo shiga sukaji abunda ammah ke fad'a wanda sunada tabbacin idan ta sun shiga bazasuji komai ba yasasu tsayawa."
Kuka sosai ammah takeyi takasa cewa komai."
Babane yayi gyaran murya, sannan ya kalli hafsa da kanta ke sunkuye ga baki d'aya kunyar kowa ya rufe ta yace. " Kiyi hakuri d'iyata nasan nayi kuskurenda mafi akasarin iyaye suke

aikatawa, "
Ki yafeni bawai dan nafison *hanna* bane yasa haka,"
Dukanku ina sonku kuma 'ya' ya nane kuma inasonku dan haka Kiyi hakuri kicire komai aranki hakan bazata sake faruwa ba da ikon Allah. "
Cikin muryar kuka tace babana na yafe maka, dukda nima nasan irin biyayyar da *hanna* take maka nima bana maka amma in sha Allah daga yanzu zakazaka sameni me yimaka biyayya."
Allah yamuku albarka baki d'aya aka amsa da amin. "
Sannan yajuya da kallonsa wajen Ammah yace kin kyautawa rayuwarki,"
Kin cutarda 'yarki Wallhy nayi danasanin aurenki Allah ya wadai irin halinki hak'ika wannan magana tayiwa hafasat zafii amma kuma, Ammah ita tajawa kanta. "
Sunkuyarda kai tayi Sannan tace dan Allah kuyafeni wallhy son zuciyane yajamin haka,"
Nayi danasani wannan rayuwa da nad'aukarwa kaina, "
Wai yau yar cikane takemun nasiha ita take gwadamun abunda nakeyi ba dai-dai bane,"
Wayyo Allah na kaicona. "
Dan Allah kutaimaka ku naima mun gafarar *hanna* bansan dawani ido zan kalleta ba na cutarda ita tuntana jaririya,"
Wallhy har kunyar kallonta nakeyi. "
Jikin mama ne yayi sanyi tabbas tasan care Ammah ta shiryu dan ita tazauna da ita na kimainin shekaru ashirin da biyar 25 kuma tasan halinta tasan tunda tafara neman gafara to tabbas ta shiryu."
Dan tunda suke ko yi hakuri bata ta6a ji dai-dai da baba ta ta6a cewa ba. "
Babane yace gafarar *hanna* zaki nema dan ita kika cutar,"
Juyawa tayi gun *hanna* gwuiwo winta azube ak'asa tana neman gafarar ta, tana cewa *hanna* nasan na cutar da ke iyakacin cutarwa kiyafeni *hanna* hatta saurayinki da kuka rabu kwanakii ma nice silar rabuwarku ni nasayarda komai na mallaka na rabaku kinga Allah ya nunamin ikon sa kinga irin mijin daya baki. "
Kukane ya kufcewa *hanna* jin cewa rabata da najeeb akayi har yanzu sonsa bai ragu kokad'an azuciyar taba kuma haryanzu ko d'igon son MG bata fara jiba."

Tashi tayi aguje tabar dakin, wani irin tausayin kanta da najeeb ne yarufeta. "
Kuka tayi iyakar iyawarta dan yanzu abin yadawo mata sabo fill."
Dakyar umma ta lallasheta tayi sallah, Sannan tashiga tad'aurawa su adda hindu abinda zata samu sucii irin wanda akeso masu jego su sha. "
Tana zaune ita kad'ai ad'aki hafsat ta shigo, zama tasamu waje tayi Sannan tace *hanna* wato bazaki yafewa mahaifiyata bako,"
Nasan tayi laipy amma yakamata ki yafe mata. "
Ta nemi gafarki fa."
Ce miki akayi ban yafe mata ba."
Kin yafe mata ne amma baki gaya mata ba kinsan haryanzu kuka takeyi taki sauraron kowa gani takeyi in baki yafe mata ba, zata shiga wani hali,"
Nisawa tayi Sannan tak'ara cewa *hanna* kinsan yanda d'iya da mahaifiya suke duk laipynda ta aikata bazanso ganinta Cikin tashin hankali ba,"

*Hanna*  plz kiyafe mata, "
Hameeda Ce tace *hanna* plz let d bygone be bygone."
No family is perfect we argue and fight, sometimes we stop talking to each other but *hanna* family is family, luv will alway's be there. "
Ganin sunason damunta kawai tafuce tabar masu d'akin basu bitava suka zauna ad'akin itada Hameeda."
Tana futa taga bbu kowa zuruf tashige d'akin Ammah kamar mai tsoron karwani yaganta, "
Azaune tasamu Ammah nata rusar kuka kamar ranta zai fita har wani dushi dushi take kallo,"
Zuwa *hanna* tayi tazauna agabanta Sannan tasa hannu tashare mata hawaye, "
D'agowa tayi tace *hanna*  sa hannu tayi ala66anta tace shiiiishshsh Ammah kidena kuka na yafe miki Allah yayafe mana baki d''aya."
Cikin kuka tace *hanna*  nagode, nagode Allah yamiki albarka, "
Amin *hanna* ta amsa Sannan tace Ammah dan Allah kimin alk'awarin bazaki sake cutarda niba,"
Kar sai na saki jiki dake ki k'ara cutarda ni. "
Ammah bama niba ko wani dan Allah karki k' ara cutarda wani,"
Girgiza kai Ammah tafayi kuka nak'ara k'ok'arin kwace mata tace *hanna* ki yarda dani na gyara halina wallhy yanzu ko kwaro bana iyajii zan cutar balle kuma d'an adam."
Jijjiga kai *hanna* tayi Sannan tace Ammah ciki abinci dan nasan rabonki da abinci tun da safe, "
Murmushi Ammah tayi tanajin son *hanna* nashiga zuciyarta,"
To 'yata jeki kawo mana abincin sai muci tare nasan kema bawai kinci bane dariya *hanna* tayi Sannan tace nikam Ammah complex zansha wollah bazanci tuwo ba. "
Ammah ne tamiqe tace mukam ai saida tuwo, bari kiga nashiga ne eba inyaso sai kishiga ciki akwai complex d'in ." K'arfe tara dai-dai su adda hindu suka isoh gabaki d'aya ta shigata, "
Jin tsayuwar mota yasa *hanna* dake d'akin Ammah mikewa tace su adda hindu sun iso,"
Ammah ne takalleta tace dama tana hanya ne, "
Eh Ammah yau ta haihu tafad'a ta zumud'i,"
Haihuwa shine dan rashin hankali zasu kamo hanya. "
Fita duka sukayi daga bakin hanya Ammah taga duk sunyi laushi daga ita har jaririn,"
Aikuwa nan tajasu sukayi shashinta batareda su mama sunsan da zuwansu na, "
Bata zauna ba ta kunna heater na toilet d'in tashiga yiwa adda hindu wanka,"
Sanda tagasata sosai sannan ta koma kan jaririn shima ta wankeshi tass ta nad'eshi. "
Dama kafin ta Fito *hanna* tahad'a mata tea mai kaurin gaske nan danan ta shanye ita kuma *hanna* tayi shashin mama tad'auko farfesunda tayi mata da kawo sata agaba Ammah tayi Sanda taci tasha romo sannan ta kawo mata tuwo dkyar taci tuwon tukunna tasamu k'arfin jikinta, "
Ammah ce tace ta kwanta kafin nan Aikuwa tana kwanciya bacci yayi gaba da ita."

To be continued

Ur's
*Z33yyb3rw3r*
[9/24, 8:50 AM] +234 810 367 2210: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r)_

*Get well soon besty (mom manal)*😭😰."

*Get well soon doughtern besty (action baby)* 😭😰

Page 49

*
Yaya auwal ne bayan yaje yayi sallan da suke kansa, yafito daga mota ya wuce masallaci dake gidan bbu nisa da masallacin, sannan ya gabatar da sallolin dake kansa sannan yawuce Cikin gida. "
D'akin mama yawuce kai tsaye, ganinsa yasa mama da umma fara juye juye ko zasuga hindu."
Ganin yazauna yasa umma kasa hakuri Sanda tace wai ina hindatun? "
D'an zaro ido yayi sannan yace," umma sun shigo fa tun d'azu da *hanna* . "
Dankwalo umma tamasa tace ungo naka mu abokanan wasan kane?"
Allah umma bawasa bane hadda Ammah ma, su suka shiga da ita, "
Jin haka yasa hankalinsu kwanciya,"
Amma mamaki ne fall aransu Jin cewa wai a d'akin Ammah take hakanne ya k'ara tabbatar musu da cewa Ammah ta shiryu, "
Kuma suma basusan lokacinda *hanna* ta shiga d'akin ba amma hakan yamusu dad'i dan hakan yana nufin ta yafe mata kenan."
Basu fita ba dan duba adda hindu dan hausawa ansansu da kawaicii idan sukaje dubata hakan yana nufin Basu yarda da irin riqon da Ammah tamata ba, dukda zuciyoyinsu nasan

ganinta Ammah sun daure dan sunsan idan sunyi hakuri zuwa gobe zasu ganta."

K'ofar *hanna* ta kulle sannan itama ta bi adda hindu suka sha bacci." koda hafsat taji K'ofar akulle kanta tsaye ta koma d'akin mama ta kwanta. "

K'arfe sha biyu dai-dai, yaron adda hindu yafara kuka tsallara kuka yakeyi bbu ji bbu gani,"

Ga adda hindu baccinta takeyi batasanma yanayi ba, haka *hanna* tayita rarrashinta dak'yar yakoma bacci. "

Aikuwa befi 1 hour da kwanciya ba yak'ara tashi nanne Ammah taji kukan ta Fito daga d'akinta ta shigo d'akin."

K'ar6ansa tayi ta fara lallashi, sai can yayi shiru dan tasan kota tashi hindu bbu abunda zaisamu. "

Nan yak'ara komawa bacci Ammah ta bada shi ta koma d'akinta."

Yaro kamar wanda ysan amma tafuta yak'ara farkawa, "

Aranar *hanna* tasan sunyi haihuwa dan ko baccin kirki batayi ba sai asubahi sannan yaron yasamu bacci."

Haka Allah yad'aurawa *hanna* son yaron sosai, shiyasa takasa bacci ta kwana reno."

Sanda tayi sallah sannan ta bi yaron suka kwanta, "

Ita kuwa adda hindu sassafe Ammah ta had'a mata ruwan wanka ta wanketa,"

Kollon Ammah tayi tace Ammah in d'aukoshi ne kimasa wankan? ".

Ammah ne tace A'a kyalesu suyi bacci dan jiya baibari sunyi bacci ba."

Tausayin *hanna* ne yakama adda hindu da kuma wata soyayarta, dan tasan idan ba d'an uwanka ba bbu wanda zqi maka wannan abun. "

Ga kuma mamakin halin amma daya sauya, dan da ko isasshen kallo basu isheta ba."

Amma tasan wannan amsar sai *hanna* tafarka. "

Shiryawa tayi ta karya sannan tafuto ta nufii shashin mama."

Ganinta tsaf bbu alamun gajiya ko yunwa ajinkinta, hakan yasa su mama sunji dad'i."

Tambayan jaririn mama tayi, tace mata ina yaronne kokuma rowa zaki mana? "

Dariya tayi sannan tace mama yana nan suna bacci shida *hanna* wai jiya bai barta tayi bacci ba."

Sai kusan 10 kafinnan yaron yatashi kuma yatashi *hanna* . "

Sai alokacin Ammah tamasa wanka sannan *hanna* ta d'aukoshi suka Fito tareda Ammah suka nufii d'akin mama."

Zqma sukayi suna hira atsakaninsu hakan kuwa bak'aramin dad'i yamusu ba dan before basu samun wannan had'in kai d'inba. "

Aranar anan sukaci abincin rana kowa ransa farii kall."

Koda abba da baba suka samesu ahaka bak'aramin dad'ii sukaji ba, dan sunsan ko bayan ransu yaransu zasu had'a kai. "

Aranar abba yashirya ya koma shida Yaya jalal dakuma salman."

K'arfe tara na dare *hanna* nazaune kirqn MG ya shigo dan sai alokacin yasamu dama yakirata. "

Sanda wayar ta kusan katsewa sannan ta d'auka,"

Cikin husky voice d'insa yayi mata sallama, "

Sanda ta lumshe ido sannan ta bud'e su,"

Tunda take bata ta6ajin murya mai dad'ii da gard'in nasaba, "

Duk lokacin da yayi magana saitaji muryan har Cikin jikinta."
Sayya sauk'ar mata da kasala."
Dak'yar ta tataro nutsuwarta, ta Gaisheshi, "
Amsawa yayi da muryarsa wanda kaman tilastshi akeyi saiyayi magana,"
D'an tsaki taja aranta sannan a zuciya tace" yafara yiwa mutane magana da kasaita kenan kamar wanda akasashi dole. "
Abinda bata saniba shine afili tayi maganar." murmushi yayi wanda saida kumatunsa suka lotsa. " Shiru suka d'anyi na'yan secounds. "
Sannan kaman mai shirin yin kuka tace nifa bakowani irin lokacii nake d'aukan waya ba,"
Amma kai saika kiranii kuma baka Cemun zaka kiraba, ta k'arashe maganar had'eda murguda baki, kaman wanda yake kallonta. "
Girgiza kai yayi dan dagajin wannan maganar yasan kawai magana take nema."
To wani irin sanarwa kikeso nayi? "
Cikin neman rikici tace ohh hakama zakace?"
Aisaika kira na d'akin d'in tukunna, "
Tafad'a tana shirin kashe wayar,
Saurin katseta yayi yace am srry tam idan zan kiraki zan rinqa miki Massages tukunna amma plz karki ki d'aukan wayana."
Shiru tayi ba tace komai ba sannan yace mata "
Idan zaki rinqa futa plz kiringa kulawa, karki na fita akoda yaushe."
Cikin Jin haushin maganarsa tace "
Sai kajira dasauran lokaci kafin kafara bani wannan umarnin,"
Dan gani tayi wannan maganar ya matukar raina tane."
Dafe goshinsa yayi sannan yace, *yah rabb " sa''iidunii* bahaka nake nufii ba"
Kawai ki kiyaye ne kinsan yanzu sai ahankali mutane kiringa kula daywa ba kowa zaki yarda dashi ba. "
Cikin halin ko inkula tace To ni tunda bbu wani wanda yacuceni kuma bbu wani mai shirin yin hakan sai yanzu."
Ganin baxata fahimta ba yasa yaga gwara yayi mata bayani. "
Cikin murya da kaman wanda kake yiwa k'aramin yaro magana kuma kanaso ya fahimceka yace."
To yanzu intambayeki,? "
Tace inajii,"
Idan 6ter d'inki tamiki laipy agida me kike mata? "
Kinsan dai ta girmeki baza ki mata rashin kunya ba, kuma baza kice zaki daketaba dan tafii k'arfinki."
Cikin rashin sanin abinda yake nufii tace, wayanta nake 6oyewa. "
Yawwa yace an dalilin dayasa kike 6oye wayanta?"
Mugud'a baki tayi tace waini meyasa kakemun wannan tambayoyinne kamar wata k'aramar yarinya? "
Srry but ki amsa."
Idan kin amsa zaki zami taki amsar. "
Sabida tanason wayanta," Tafad'a adak'ile. "

Ok tam dalilin da yasa zaki kula kenan dan inasonki,"
Hmm tace sannan tace sai kace wani d'an siyasa wanda ake neman kashewa zakace wani na kula?."
Cikin ransa yace ya rabb wannan yarinya Allah yad'aura mata taurin kai. "
Yace eh kusan hakan ne tunda ni soja ne kuma kingani yafi d'an siyasa hatsari,"
Kama ha6anta🤔 tayi sannan tace ehh hakafa, "
Amma ai maganar da kayi kamar akwai wanda suke nemanka ne."
Ya rabb,, kina fa da surutu yace Cikin gajiya da tambayoyinta, "
Turo baki tayi sannan tace ai bani nace kakirani ba,"
Balle nadameka da surutu, "
Tana fad'in haka d'iff takashe wayarta,"
Murmushi yayi sannan ya Girgiza kai, "
Sannna afili ya furta, Allah ka nunamin rnda yarinyar nan zata daina kashemun waya."

Sanda ta kashe wayan da yan minute wani abu ya fad'o mata. "
D'aga wayan tayi sannan takira anty samha da saurii,"
Tana picking tace anty bawa yaya abubakar bbu musu ta miqa masa, yasa kar6a ko gaisawa basuyi ba tace, yaya abubakar shine? "
Shinewa?" ya tambayeta? "
Shine?" takara cewa, "
*Hanna* ban fahimci me kike nufii ba fa kimun bayani."
Yaa abubakar shine sojan k'asa da k'asa? "
Sauk'arda ajiyar zuciya yayi sannan yace eh shine *hanna*, Aikuwa Sanda gabanta yafad'ii datajii shine." sallama tamasa yace *hanna* wani abinne yafaruu? "
Gyara nutsuwarta tayi sannan tace A'a dama bansani bane nake tambaya,"
Oh ai har hankali na ya kwanta shine, "
Ok sai anjima."
Bazan bawa samhan ba?" yatambaya eh kabarta Kawai saida safe tana fad'in haka ta kashe wayar ta. "
Tana kashewa ta kira amira tana d'auka tace mata beb, ina wannan mutumin da mukajii ana zancen kasheshi lokacin da mukaje office d'in dady?"
Amira ce tace ehh menene yafaru? "
Kinsan daga baya nace miki naga news an harbeshi."
Kai beb Kardai haryanzu baki manta da wannan zancen ba, "
A'a ba haka bane beb shine fa,"
Tsaki amira taja sannan tace shine wa? "
Um Um ta tsaya cewa dan ita batasan da sunanda zata kirashiba,"
Dan ko sau d'aya bata ta6a kiran sunansa ba ita hasalima batasan asalin sunansa ba tajidai labba nacewa yaya yareema. "
Amira ne tagaji ta jira tace kefa nake sauraro,"
Cikin saurii kamar wanda takejin shakkan maganar tace shine yayan labba, "
Wani irin ihuu amira ta kwala wanda Sanda *hanna* tacire wayan a kunnenta,"
Ihuu takeyi tanayi tana rawa da murna iya k'arfinta, "

Wanda hakan ba k'aramin kularda *hanna* yayiba ta fad'a mata ta tayata jimami amma ihun murna takeyi."
Sanda tagama ihunta tace beb mun tafii wallhy. "
Tsaki amira taja sannan tamayar mata yanda sukayi da MG."
Itama amiran jikinta ne yayi sanyi tace beb kisa aranki bbu wani abu, in sha Allah bbu mai cutarda ke kinji, nan amira tayita kwantar mata da hankali Sannan sukayi sallama, "
Haka adda hindu tayita zama a d'akin Ammah ranar suna yaro yacii sunan sa Aliyu, sunansa Kawai yaci amma sai yazo dai-dai da sunan mahaifin Ammah, Aikuwa murna awajenta ba'a tonawa dan iya bajinta tayi bajinta asunan,"
Sosai sunan yayi armashi. "
Anty samha bata samu zuwaba, dan baba ne yahana yace satii biyu kenan da auranta bbu yanda zataje."
Washe gari umma ta koma kano, yaya jalal ne yazo yad'auketa, "
Hameeda kam tace idanta koma To k'afarta k'afar amarya."

To be continued

Ur's

*Z33yyb3rw3r*
[9/24, 8:59 AM] +234 810 367 2210: *BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

_Godiya mai tarin yawa ga masoyana, naji dad'iin addu'oiinku da kuma kula warku, wannan shafin nakune, " *mamman hassan, mmn waleed, zainab bawa(namesake), maman fodio, mamn khish, jameelah, ayusher ayuba isma'il, Ameena* nagode da kulawarku."_

_Y'an group d'ina inasonku sosai Allah yabar k'auna kuna ssakani nishad'i, BIBIYATA AKEYI 1&2 da kuma QUEEN ZEEYY. Allah yabarmunku zeyybawa takuce."_

Page 50

*
Bayan suna da kwana biyu, Zaune suke ad'aki su shida,suna hira, *hanna* , Hameeda, amira, hafsat, adda hindu, rabi'ah,"
Amira ne tad'an gyara zama, ta kalli *hanna* tace, ke nifa wajenki nazo, biki sai k'aratowa yakeyi, amma ko zancen anko banji kin fara ba. "
Ta6e baki *hanna* tayi sannan tace ni wasu k'awaye nake dasu da har zan wani fidda anko."
Harara adda hindu ta galla mata, sannan tace da'allah tafi kibawa mutane waje, "
Amira ne tace" adda wallhy bakiga yanda 'yan matan level d'inmu masu shegen girman kai suke kirana akan idan an fidda anko nakawo masu."
Daa se shegen girman kai ko kallo mutane basu ishesu ba."
Amma yanzu sai wani kirana sukeyi, wato sunsan cewa nice frnd d'inki insasu acikin frnd. "
Dariya Hameeda tayi tace ai wollah ko nice zan yi haka, dariya dukkansu sukasa." "
Adda hindu ne tace wallhy kuncika yarinta da yawa, "
Harara *hanna* ta galla mata tace wai dame kika girmenine?"
Wani irin kallo adda hindu ta watsa mata tace" ke nifa inada yaro. "
Saidai yaronkan injii rabi'ah,"
Dan kinsan nidai baki girme niba. "
Yakamata dai kufara bani girma danni yanzu na wuce sa'ar ku." inji adda hindu,
Hafsat ce tace nikam dan Allah kubar wannan abun yanzu musan abinyi,"
Dan gaskiyar amira ne yaci ace yanzu munfara shirye shirye. "
Ana cikin haka Massages ya shigo wayan tana dubawa taga MG ne."
Anrubuta zankiraki 8pm plz pick it. "
D'an siririn tsaki taja wanda yaja hankalin Hameeda ta kai kallonta kan screen na phone d'in,"
Rike baki tayi tahau salati, yanzu ke *hanna* idan zae kiraki Sayya nemi izini? "
Ina ruwanki bansan munafurcii," inji *hanna*
Rabi'ah ne tace kyaji dashi anaso ana kaiwa kasuwa."
Idan ba haka ba waye zai samu mijinda samunsa na wahala kuma kice bakyaso inbanda gulma. "
nifa kun fara isata inji *hanna* idannace bana sonsa ina ruwanku?" ai ba'aso dole."
Hameeda ne tace ku rabu da ita duk munafurcii ne."
Allah adda baku ga ranarda muka fara had'uwa dashiba dan ya tsaya yimun magana shinefa ranta yabacii ta koma Cikin gidanki da b'acin rai. "
Kuma idan ba haka ba gata ku tambayeta,"
*Hanna* ganin batada na cewa yasata yin shiru da suka isheta ta fice tabar musu d'akin."

Ummii ce zaune a falonta, itada afeeya da anty hibba da kuma afeeya,"

Shirye shiryen zuwa had'o kayan lefe sukeyi, jibi zasu tafii Yayinda intisar kuma nanan wani irin zazza6i ne yarufeta, har kullum wani irin son MG ne yake rufeta wanda, tarasa yanda zatayi duk wani hanya dazata bi wajan nuna masa tana sonsa abun ya faskara dan baimasan tanayi ba."
Yana chan yana son maso wani kamar yanda itama intisar takeyi,
Koda affan yaji mai yake damunta hakuri kawai yabata dan ya tabbata cewa yayansa yayi nisa baijin kira, "
Dan irin sonda MG ke yiwa *hanna* Koda ta aureshi wahala kawai zatasha,"
Da haka yayita bata hakuri sannan yace har in dai mijin kine to bbu makawa sai kin aureshi, komin dad'ewa, dan yayi aure hakan bawai yana nufin bazai k'ara wani ba kenan."
yayi mata haka ne kawai dan kokad'an baison intisar ta aurii MG dan aganinsa kokad'an basu dace ba."
Kamar yanda yakejin intisar amatsayin yar uwa haka yakejin *hanna* bazaiso ko d'aya ta cutu acikinsu ba,"
Da haka intisar tasamu ta warware, dan yanzu tasa aranta ko bayan auren saita samu hanyar da tayi ya aureta."

K'arfe takwas dai-dai, MG yakira *hanna," yana kwance akan bed da pillow a chest din sa ya matsae pillow d'in sannan yaa k'urawa fan ido, jiran kawai tayi picking yakeyi,"
Sanda takusan katsewa kafin ta d'aga,
Sallama tayi ciki-ciki,"
Jin muryarta haka ya saukar masa da kasala dakyar ya iya amsa sallamr. "
Itama lumshe idanuwa tayi sakamakon yanda muryar ta daki dodon kumnuwanta,"
Duk yanda takejin rashin sonsa aranta amma fa ba k'arya itama tasan komai nasa yayi saidai kawai tak'i fad'a. "
Cikin ranta kuwa ji takeyi kamar bata ta6ajin muryar ta takai tasa dad'ii da gard'ii ba."
Jin shiru yasa shi tunanin kota ajiye wayanne, "
Are u there? Yayi questioning Cikin whisper voice, umm kawai ta amsa Jin irin muryar da yake magana da ita wanda take hanata aikata komai."
Kin wunii lpy?"
Ya tambaya, sai sannan taji kunyar gaidashi , "
Ina wuni tace sannan yayi 'yar dariya kafin ya amsa,"
Turo bakii tayi sannan tace kai ko?"
Dafe goshinsa yayi yace owwh Allah nime? "
Sai kayi ta yiwa mutane dariya tafad'a had'eda twisting lips d'inta kamar wanda yake kallonta."
Inbar dariyan? "
Yatambaya eh tace kanta tsaye Eh"
Siririn murmushi yayi sannan yace to ai bama kowa nakeyiwa ba."
Umm kawai taqara cewa,"
Zuciyarta ne keson masa tambaya duk lokacin da yakirata amma saita kasa."
Daurewa tayi tace masa, in tambayeka mana? "
Ehem inajii yace,"
Cire wayan tayi ta harareta sannan ta kwaikwayi irin maganarsa, "

Yana yiwautane magana cikin gadara, mtsew."
Yaushe ta ta6a kallona lokacin da kace in yarinya kuma a'iina? "
Yi yayi kamar baiji mai tace ba yace, gobe ina hanya, takaicine yacikata nak'in amsa mata tambayarta tace ni karkazo."
Baisan lokacin da yatashi zaune ba ya waro eye's dinsa yayinda eyeballs d'insa masu shape na oval suka k'ara girma, yace karfa inzo kikace? "
Eh ta amsa atakaice,"
To idan banzo ba yaya zamuyi mu tsara yanda event's dasu kasance? "
Ni basai anyi event ba,"
Siririn murmushi yayi wanda sanda both side na dumfull nashi suka lotsa."
Sannan yace nifa naga alamu har yanzu akwai yarinta mai tarin yawa ajikin ki, "
Ranta ne ya6aci jin kiranta da yarinya da yayi, kamar zatayi kuka tace nidai wallhy kadena cemun yarinya,"
Rufe bakinsa yayi sannan yace nadaina,"
Fusata tayi jin abin kamar zolaya ma yazama masa tace kaid'in dame ka girmeni? "
Duk irin dakiyarsa da rashin son yin dariya amma baisan lokacin da ta kwace masa ba yahau yinta kuwa bbu kakkautawa,"
Jin ya maida ita mahaukaciya yasata kashe wayar, sannan ta kifa kanta a fillow tasha kukanta ta koshi. "
Batabi takan zancen zuwansa ba ta kwanta tayi baccin ta koda safe ma tanayin sallah ta koma bacci, sai 9 tatashi, bayan tatashi ne tatuno da zancen zuwansa, ta6e baki tayi tace ai tun da nace banso yazo halama yafasa, haka tacii gaba da damuwowinta."
Kusan 10 taji shigowar sako wayarta, "
Dubawa tayi taga MG ne, an rubuta in sha Allalh zuwa 1 zamu sauka."
Rasa yanda zatayi tayi, idan taje tafad'awa mama dole zata mata fad'a. "
Shiga kitchen tayi yanda amma ke zaune ta inna kaltu suna aiki,"
Ra6e-Ra6e tafarayi kaman munafuka, "
Ammah ne tajuyo tace" *hanna* meyafaru? "
Sosa kanta um um tafara cewa, kallonta Ammah ta tsaya kawai,"
Ummm dama wai zaizo ne k'arfe d'aya, Ammah ne tace waye zaizo? "
*Hanna* tace shii man, 6ata rai Ammah tayi tace ke banason shashancii shii wah?"
Ammah yareema "
Yareema?" Ammah ta maimaita zaizo yau? "
D'aga kai *hanna* tayi,
Tun yaushe yace miki yana zuwa?"
Ammah tatambaya, kamar wanda take tsoron kar Ammah takai mata duka sai wani kakkare kanta takeyi da hannuwanta tana Sosa kai tace tun jiya, "
Salati Ammah tayi ta sanar da ubangiji wanda haka yafuto da mama dake d'aki tana tambayar maiya faru?"
Ammah bata tsaya bata amsa ba tace lallai 'yarnan kin cika marar kunya, wato ke ba' aisa afad'a miki magana bako? "
Yanzu da kike fad'amun k'arfe goma da rabi mai kike tunani zanyi kenan?"
Aikuwa ke yanzu zaki Shiga kasuwa kuma kidawo da wuri azo ad'aura musu abincii

shashasha kawai, mama ganin basu gayya cetaa ba cikin maganar yasa taja kafafuwanta ta koma. "
 Kud'i Ammah tabata suka Shiga kasuwa itada hameeda da hafsat, duk wani abunda zasu buk'ata sun sayo, suna dawowa suka hau yin aiki batareda su Ammah sunsa musu hannu ba dan sun iya komai nasu."
Dake aikin ba mutum d'aya bane 1 dai-dai suka gama aiki,, su MG kuwa dake sun d'an samu delay sai lokacin jirginsu ya tashi, dake tsakanin bauchi da kano ba wani nisa bane yasa basu jimaba suka sauka masallaci suka nufa sukayi sallah dashi da wayanda suka rakoshi, yaso tafowa shi kad'ai amma hakan bamai yiwuwa bane, "
Baisanar da zuwansa ba amma duk da haka sanda yasamu wanda sukazo tar6ansa ciki kuwa harda governor,"
A government house suka yada zango, a lokacin kuma hanna ta Shiga wanka aka gyra falon baba yayi kyau banda kamshi bbu abinda falon yakeyi, wanka tafito ta sanya jan swiss d'in da anty maman amal ta d'inka mata tunda tasa agidanta sau d'aya bata k'ara sawaba,"
Shi tad'auko tasaka yamata kyau sosai, sannan tad'auki bak'in mayafii. " Light makeup tayi tabi duk jikinta da humra mai dad'ii, "
Nikuwa nace *hanna* ana ba'aso amma irin wannan kwalliya haka🤔🤷‍♀️
Sai pass 2 kafin suka iso gidan, falo saleem yakaisu, sannan ya fita yabasu waje sucii abincii, captain Ahmad ne ya mtso kusada wermer's d'in yace bari mufara cin abinciin amarya tun daga yanzu, harara MG ya dalla masa, "
Haka suka zauna sukacii abincinn MG kuwa kokad'an bai ta6a ba."
Shida yaransa guda tara sukazo shi cikon na goma, "
Shida captain Ahmad da captain bala da wani wanda bansan ko waye bane sukasa jamfa yayinda sauran kuma duka kakii ne ajikinsu,"
Captain bala da wasu sauran uku ne kawai fatansu yad'anyi duhu suma ahakan sunada haske agaban sauranne fatarsu tayi duhu dan su d'in sauran ba blacks bane. "
Danna wayarsa yayi yak'ira *hanna* a lokacin amira ta iso tare suka tashi suka nufii d'akin da su hud'u da amira hafsat hameeda da *hanna* da sallama suka Shiga lokacin sun gama har sun gyara wajan, gaisawa sukayi sannan su amira suka mike da niyyar futa, "
Wannan d'aya wanda yasa jamfa d'innan wanda tare sukayita bibiyar *hanna* da captain bala ne yak'urawa hafsat ido har suka fice ainihin kama suka masa da *hanna*   sai bayan sun fita ne sauran sojojin suka fara gaisheta, amsawa tayi amma da captain bala da kuma wannan d'ayan suka gaidata kin amsawa tayi tabisu da harara, ".
Wanda su kansu basai anfad'a ba sunsan ma'anar hararar yayinda MG ya riqe dariyarsa,"
D'ayanne wanda bansan sunansa ba yace yalla6ai anema mana afuwa tuba mukeyi. "
Kollonta MG yayi bqice komai ba."
Sosa kai captain bala yayi yace ayi hakuri madam, "
Kawarda kanta tayi batace komai ba,"
MG ne aransa yace yar rigima, "
Gyara zama yayi sannan yayi gyaran murya, lokacii d'aya dukansu suka tashi suka fice yazamana daga ita saishi,"
Turo baki tayi tace ina wuni, Ipy ya amsa atqkaice nan suka gaisa, yace yau zamu koma nazone naji shirye shiryen da zamuyi ta6e baki tayi tace nifa bzanyi wani shirye shirye ba. "

Karkace kansa yayi yace waii dama da gaske kikeyi?"
D'aga masa kai kawai, baisake cewa komai ba yace ban phone d'inki bbu musu ta mika masa,"
Numb d'in amira da hameeda yayi dialing yace suzo ba 6ata lokacii suka zo su uku, sannan ya kira captain Ahmad yace yazo shida c bala da kuma c bilal, ba 6ata lokacii suka Shigo nan suka fara shiri kamar wasu sune amaren sosai suke shiri saikace auran y'ar shugaban k'asa, sake baki kawai *hanna* tayi tana kallonsu sanda, suka gama sannan MG yace yanaso ya gaisa dasu mama, saleem ne yamasa iso har ciki yashiga ya gaidasu,
Suna gamawa ya damqawa amira atm sannan suka wuce. "

_Idan kunga mistake afuwan bansamu lokacii gyara ba."_

Comment

To be countinued

Ur's
Z33yyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

_*Y'ar uwa, Y'ar uwa Y'ar uwa, kalmar nan tamkar zinare take, agaskiya ina alfaharii dake Y'ar uwata my other half, antyna ba na wata ba,"*_
*Anty rashida wannan shafin nakine durungum ke d'aya ina sonki ina alfaharii dake.*

*
Shirye shiryen bikine yafara kankama daga kowanne bangare,"
Kokad'an yanzu su *hanna* bbu zama yau Suna chan gobe Suna chan, "
Koda ita bamai yawan k'awaye bane amma tanashan mamakin irin mutanen da amira ke gayyata takeyi,"
Acikin week d'in hameeda tatafi kano dan itama akwai abunda takeso tayi acahn d'in, kuma baza'a rasa mutanen da zata gayyata ba. "
Acikin satin su amira da *hanna* akayi resuming skull,"
Alokacin abubuwa sukayi musu zafii,
Yanda abun yazo dasauki ma dake IT zasu tafii, "
Kuma *hanna* komai na IT d'inta agarin bauchi tacika,"
A accnt d'in da yabada atm su amira suka cire kud'ii mai yawan gaske, aka fidda anko masu kyau da tsada,"
Kala uku-uku, kowacce k'awa aika mata da nata akayi,"
Aikuwa murna wajen k'awayen ba'a tonawa, "
Sai satiin biki za'a kawo lefe,"
Ana biki sauran satii biyu, "
Kawai ranar saiga ummii ta aiko larabawa guda biyu masu gyaran jiki,"
Abun yabawa su mama da Ammah mamaki, " Dan aganinsu su yakamata su nemi mai gyara musu yarinya sai ga, mahaifiyar ango nan taturo,"
Ba'ad'auki tsawon lokacii ba aka ware musu d'aki ashashin Ammah, "
Nan da nan suka fara gyarata ba'a barin kowa yashiga ganinta ko MG ma sun hanata d'aukan wayqrsa duk yanda yaso kiranta akashe kullum wayanta, abun ba k'aramun damunsa yayi ba," yaso yazo amma shima nashi hidin dumin ya masa yawa, "
Har IV na bikin su amira ne suke rabawa hameeda ta dawo tare suke fita,"
Idan sunfita tun 11 basu dawowa sai dap magrib, "
Yanzu gabaki d'aya amira ta dawo gidansu *hanna* dazama,"
Dayake aabubuwa sunyi yawa,"
Cikin kwana biyar *hanna* tadawo itada larabawan babbancin kad'anne dan bakaramin kyau tayiba, "
Dakyar su amira ke samun ganinta sau biyu ko uku arana, da abin yafara yawa suka nemii mama ta acanja musu gida,"
Da farko mama tak'ii amma daga baya umma da amma suka ce su kansu amaren zasufii sakewa, har indai suka samu privacy, "
Gidan Anty maman amal suka koma dayake ita ma ta koma gida tun da bikin ya matso kuma mijinta yayi tafiya,"
Sosai sukaji dad'in gidan dan yanzu Suna d'an samun sakewa, ita kanta *hanna* yanzu tafijin dad'i Suna tareda su amira yanzu ana barinsu su zauna waje d'aya tunda gidan a Rufe yake,"
Ko abu *hanna* taruqe sai yayi sassanyar kamshinda takeyi balle wajanda ta zauna, ko tawuce,

"
Itada hafsat hameeda amira ne sai hafsat da kuma way'annan larabawan,"
Abida da Aisha, "
D'aya matar tad'an manyanta d'aya kuma matashiyace dabazata wuce shekaru 30 ba."
Sa'ii Sa'ii umma na mata aika. "

Su labba kuwa iyayen biki ko ganuwa ba'ayi duk wani hidin dimu itace akan gaba,
Hatta anko da suka cire ma sanda suka tura mata taganii sannan suka fitar." da hameeda zata tafii sai tatafii mata dashi. "
Suma chan sunyi nasu anko dun,"
Duk da cewa nasu classical ne, "
Dan swiss k'arshen tsada sukayi order d'insa,"
Suna son sufita daban Suna shiga agane cewa dangin ango sunzo wannan na ranar diner kenan, "
Sauran ranakun kuwa shirin da sukayi saisu Kansu dan bamai fad'uwa bane."
Idan kaga intisar zakaceq ba ita bane,"
Dan ta kwantarda hankalinta, kokad'an yanzu bbu damuwar komai atattare da ita, "
TA ware abunta shiirye shiryen biki kawai takeyi, itama barnarda kud'ii takeyi wajen bikin, kilishi har mamakinta takeyi,"
Hakanne yasa takirata d'aki zaunarda ita tayi ta dafa kafad'unta, sannan tace"
Intee kin daina son yareema ne?? "
Girgiza kai tayi tace haba umma ya kike wannan zancen kinsan bazan ta6a daina sonsa ba."
Kilishi ne ta nisa sannan tace mai hakan yake nufii kenan? "
Kinfasa burinki na auransa?"
Nan ma Girgiza kai tayi tace wallhy umma ina nan akan baka na, bazan ta6a hutawa ba harsaina aureshi. "
Nisawa umma tak'arayi tace tom wannan wani irin rawar k'afa kikeyi a auransa?"
Intisar ne tace oh umma duk way'annan tambayoyi  ki ajiyesu amsosunsu sunqnan zuwa. "
Tana fad'in haka tatashi tafice tabar kilishi da zullumi Tunani takeyi to menene yasa ta farin ciki haka bayan tana sonsa?"
Haka dai kawai tayi hakuri da way'annan tambayoyi. "
Gashi wani k'arin abun haushin ma bai wuce yanda 'ya'yanta suke narkarda naira akan wannan bikin ba."
Da intisar taso ya aura. "

*Ina labarinn najeeb*
====
Najeeb tun lokacin dayaga *hanna* ta amince da auran MG yazama k'aramin mahaukacii yabar suma tayi wani buzu buzu a kullum da ciwon son *hanna* yake kwana a kullum yatuna abun da yamata laifin kansa yake kallo,".
Yayi kuka har yagajii kamar ba babban saurayi ba ya fawwalawa Allah komai, dan yanzu magana ma wahala take masa,"

Kokad'an bai shiga harkokin jama'a yafii ganewa kullum yana d'akii dan yanzu ya tabbatar *hanna* tamasa nisa, "

MG ga baki d'aya yau yanajin sa kamar me, yatashi da sonjin muryar *hanna* Gashi ya kira wayarta a kashe."
Massage yashiga rubutawa kamar duk wani lokacin da ya kira yaji wayan akashe sai yatura massage, "
Massages d'insa sunfii ak'irga acikin wayar amma ita batsanma ya turo ba."
*Hanna* ce zaune afalo su hameeda sun fita, itakuma zaman kad'aici ya isheta, kawai ta tsuncii kanta da son kunna wayarta, "
Jakarta ta nufa ta d'auko wayan, tayi plugging din cherger sannan ta kunna wayan, sanda tagama ta kunnu tafara kallon Massages d'in MG atake tajii wani tausayinsa yakamata,"
Danna numb d'insa tayi zata kira, haryana shaurin yin ringing tayi saurin katsewa, "
Aikuwa kamar yasan ta kunna a tym d'in yasake trying numb d'in sai gashi yashiga,"
Kallon phn d'in tatsaya yi har yakatse bata d'aga ba sanda, wani call d'in yasake shigowa ne ta d'aga,
Ajiyar zuciya yasauke wanda har cikin waya sanda tajii, "
Cikin worried voice yace, sweety I miss u,"
Batasan lokacin da bakinta ya furta I miss u mor,,,,, saurin Rufe bakinta tayi bata k'arasa ba."
Dad'ii yaji jin shima tayi missing d'insa. "
Sweety zanzo yau da daddare,"
Rufe baki tayi tace no karkazo, "
Meyasa?" yatambaya, "
Bazasu bari kaganni ba."
Nidai zanzo kisan yanda zakiyi yana fad'in haka ya kashe wayar baijira cewarta ba. "
K'arfe shida su amira suka dawo itada hameeda da kuma hafsat."
Suna zuwa dukansu suka zube jikin *hanna*  ihuu tasa tana turesu ni da'allah menene hakan kutashi, "
Hameeda ce ta d'ago tace beb kinga lefenki?"
Wallhy ko atarihi banta6a ji ko ganin wanda yasamu lefe kamarkiba, amirace ta nisa tace beb akwatunan talatin kamar amafarki, "
Beb duk kayan ciki kyawunsu bayi fad'uwa, beb ko rabin akwatin ba'@bude ba kowa yagaji,"
Hafsat ce tace kud'in kan akwatii kinsan nawane? "
Rufe mata baki tayi tace banson jii,"
Ganin zasu dameta da surutu ga lokacin magrib yayi yasata tashi tabarsu kamar wanda sukayi gamoo, "
Sallah tayi tazauna akan pray mat tana jiran ayi sallan isha azao akwa6a mata abun ajikinta,"
Wayanta ce tafara ringing dan tunda ta kunna bata kashe ba, tana dubawa taga MG ne. "
Tana d'auka yace mata yana waje,"
Futa tayi ta na sand'a har tafice agarden taganshi yana zaune kamar wanda yadad'e da zuwa, "
Kallon ta yakeyi tun daga nesa, da badan zuciyoyinsu na manne da juna ba da yayi musu cewa ba ita bane."
Har takaraso bai saniba kamshinta ne yasanar dashi isowarsa, "

Sallama tayi ta gaidashi ya amsa, sannan yace sweety kinyi kyau sunkuyar da kai tayi tana wasa da yatsunta," sanda sukafii mintii goma bbu wanda yasake cewa komai, kallonta kawai yake yi, " sannan yatashi yace natafii fligt d'ina 7:30 zai tashi akano nakeso nayi sallar isha, bud'e baki tayi tace dama kawai kazo, murmushi yayi sannan yace ganinki aiba kawai bane,"
Ahaka taraashi har bakin gate dake bai Shigo da mota ba leqawa tayi taga gidan zagaye da sojoji, "
Bud'e baki tayi tana kallonsu,"
Muryarsace ta dawo da ita kina mamaki ne? "
Tun randa aka kawoki gidannan suke zagaye dake, yana fad'in haka yajuya,"
itama juyawa tayi da gudu ta shige gida, "
Nan sojojin suka k'arkame kofa,"
Juyawa tayi tana mamaki wato shiyasa kai tsaye yasan yanda take. "
Tana shiga bata samu kowaba tashige tayi sallah sannan akazo aka fara."
Yau takasance gobe za'a fara event duk wani shirye shirye anankai har makeup artist anrigada an shirya su yanda komai zai tafii dai-dai washe gari ya tashi ranar laraba ranrda za'ayi kamu tun safe aka fara shirye shirye. "

To be countinued

Ur's
Z33yyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*
_
_Bismillahirahmanirrahim_

_
Writting by

© _zaynab_ _bawa_
( _z33yyb3rw3r_ )

*_If a friendship last longer than 7 year's, u are not just a frnd u r family, " just like we are *MAIMUNAT* *_this whole Page is dedicated to u my frnd,"_*
*_Wsh u safe journey y'an kano zasuyi missing d'inki_*😉

*
Page 52

K'arfe sha d'aya 11:00 Suna zaune afalo, Suna shirya yanda kamu zai kasance,"
Sallamar labba kawai sukajii, "
Juyawa sukayi cikin mamaki, alokacin angama zanawa *hanna* lalle kenan yayi masifar kyau irinna larabawa dan sunema suka zana mata."
Angama mata itada hameeda ana yiwa amira saura hafsat, nan labba tashigo itama tayi kyau sosai, ga zanen lallen ta yayi kyau saidai kawai baikai na *hanna* ba. "
Wasu irin sirararn zane masu kyau har kyalli sukeyi da wani irin kamshi zanen lallen *hanna* ,"
Labba ne ta zauna tana subhanallahi 😍😘 antyna kinga irin kyau da kikayi? "
Wallhy Idan ahanya naganki ganeki zaiyimin wahala."
Kai gaskiya ya yareema yayi za6e, kin ganki kuwa? "
Har wani sheki kikeyi kamar wata taurqruwa,"
Harara *hanna*
_Ina kike aminiyar kwarai qawar albarka, kisani ina sonki ina alfahaari dake_
_*murjanatu(gimbiya)* wannan shafin nakine ke kad'ai."_

================

Page 70

Page na farko taga anrubuta." I LOVE HER." abunda aka rubuta kenen, na biyu kuma SHE'S AN ANGEL."
sake bud'e third Page d'in tayi, SHE'S STUBBORN, abunda aka rubuta kenen."
Murmushi mai kyau *hanna* tayi sannan ta bud'e fourth Page d'in, SHE WAS BORN IN 29/MARCH/1998."
Page na biyar tada bud'e ne taga rubutu mai yawa zama tayi sosai sannan ta fara karantawa Kamar haka."
On 29/march/2007." the day I first saw her."
Runtse ido *hanna* tayi, sannan tacigabada karatu."
Da misalin k'arfe 7:45.am." na safiyar litinin, tushen aiki." alokacin kowani d'alibi k'ok'arinsa yaga ya isa makarnta."
Takowani lungu ka leqa dalibaine Da uniform kala-kala."
New GRA sky crest d'alibaine birjik gaban makarnta assemly akeyi kowane d'alibi tsab-tsab dake kasancewar ranar farkon satii."
Brown d'in skirt ne dakuma milk shirt sannan sai brown mini hijab."
Yawancin student d'in kayanda ke jikinsu kenen."
Sai kuma gefe d'aya dana ganii Brown skirt Da milk d'in hijab Da riga." Alamu yanuna cewa junior ne masu wannan shiga."
Daga can gefe kuma yarane Da green d'in check, bayan angama assemly d'in kowanne yanufii class d'insa."
Motocii ne suketa wucewa hanyar."
Wasu Motocii ne sukazo ajere da'amu akwai mai mulkii cikintq." Motocii guda biyarne duka hud'u nagaba Da baya an musu paint na sojojii, yayinda d'aya Daga cikinsu takansace bak'a wuliik." yarane makill, wanda suke jira su tsallaka, uniform d'insu ya ban tanta dana d'yqn skull d'in. Tsallaka titin sukesonyi, amma yawan motociin dasuke wucewa yahansu, tsaye suke

cirko-cirko, MG ne dake cikin dake cikin bak'in motar yayiwa guard d'insa magana aka su kashe titin student su tsallaka."  tsayuwar motar ne yasa student suka fara tsallakawa, hanakalin MG ne yakai kan wata mota, stliet ce ta tsaya bakin sky crest ta sauke Wata yarinya, Da bazata wuce shekara tara ba."
 Sannan motar ta juya zuwaga makarantar dake opposite d'inta sa'adu zungur."
 Sauke sauran yaran yayi, wanda da'almu y'an uwan tane,  amma abun yabashi mamaki ganin ita ansauke ta a private schooll sukuma y'an uwanta ansauk'esu a government schooll."
 Juyawa yayi zauwaga yarinyar dayaga ansuke."
 Gabansane yafad'ii da ganin yarinyar yarasa dalili kawai yakasa d'aga idanuwansa daga kanta."
K'ura mata ido yayi tsam, magana takeyi wanda baijin mai take fad'a, amma kuma daga alamu yagane cewa magana ake mata akan sandal datasa, kowani student yawuce sandal na kafansu brown ne kokuma black."
 Ita kuma nata pink ne."
 Bayadda ba'ayi tacire sandal d'inba amma tak'ii, dariya abun yabashi ganin yanda yarinyar keda taurin kai."
 Ahaka har kusan 15 minute sukuma soldier's d'in ganin haryanzu baiabsu order natafiya ba, yasa kowa yayi shiru."
 Gateman d'in ganin tak'ii cirewa ne yasa su cewa tom sai anmata bulala na latti, turjewa tafarayi tana kuka amma haka bbu imani, sanda ya zuga mata d'aya runtse idanuwa MG yayi danhar ajikinsa yajii zafin bulala."
 Bud'e idanuwa yayi yaga yanda take ihu."
 Ganin tana kuka yasa Gateman d'in yace ta wuce, tafiya takeyi tana kuka hankalin MG inyayi dubu yatshi ganin yanda tatafii tana kuka."
 Ahaka yatsaya harta shige."
 Juyawa yayi ya kalli driver ya nuna masa wani d'an waje anrubuta kobii senima asaman wajen duka sukayi parking."
 Yunwa sukeji duka dan saukarsu kenan zasu wuce zaranda hotel, su huta k'arfe biyu sunada meeting."
 Sai 1 aka tashi su *hanna*  sunfito y'an primary kad'ai."
 MG leqe yakeyi amma baiganotaba Sai can wata yarinya tanata kwala kira *hanna* *hanna* direction d'inda take kallo ya kalla dan sunan yamasa sosai, idauwansa yayi tozali da yarinyar dayagani d'azu."
 K'arasawo tayi tace wai nii menene kiketa kirana?"
 Bud'e baki MG yayi ganin k'aramar yarinya amma Sai shegen tsiwa."
 Yarinyar ce tafara magana tace d'azu anty tace muyi wshing d'inki is ur birthday today."
 Eh kawai *hanna* tace sannan takawarda kai tanufii wajan wani mai rake dake bakin titii, sayan raken tayi sannan ta koma ta zauna, bata dad'e dad'e zamaba wasu frnd d'inta sukazo, tsayawa sukayi cirko-cirko akanta, hqrara ta aika musu sannan tace menene kuma zaku wani tsayamun aka,,,,,,,, aibata k'rasaba suka juye mata bokitin ruwa." Razana MG yayi ganin yanda tasa ihuu da kuma yanda numfashinta ke sama-sama."
 Had'e baki sukayi sunacewa Happy birthday, saurin fitowa MG yayi daniyar taimakonta, alokacin motar babansu ta danno wajan tsayawa yayi cakk, ganin babanta yafito dasaurii ya

nufeta babbar riagarsa yacire yanad'eta yad'auketa zuwa mota."
Ganin su MG yatsayayi yarasa dalilin dayasa Yarinyar tatsaya masa araii, baibai wajanba har saida ya ga yafiyansu."
Juyawa yayi ya kalli captain bilal dake kusa dashi yace."
Wancan mai raken kaje kabashi jaree, banso yak'ara sayarda rake."
Dahaka suka isa masaukinsu, sannan suka wuce meeting."
Washe gari yakamata MG yakoma amma haka yakoma washegarii da safe."
Dai-dai lokacinda *hanna* tazo jiya."
Sanda yaga shigarta har zuwa tashinta sannan ya koma."
Alokacin *hanna* hawaye kawai take gogewa, ko batazo k'arshe ba tasan MG masoyintane."
Share hawayen tayi tacigaba da karatuu."
Sanda yayi kwana uku yana zuwa makaranta yana jiran tashinta."
Ana hud'unne yabita har gida."
Tun daga lokacinda yaga gidansu yabar captain bala da captain bilal masu jiranta."
Koda yaushe suna k'ofar gidan idan anguwa zata tafii itqda yayyaunta to suna biye dasu."
Ko shago *hanna* taje ta siya abu tom wannan mai shagon Sai anbashi jareenda zai iyayin uku ko hud'un nasa nad'a."
Mutane daywa sun samu sauk'i daga talaucii ta dalilin *hanna* wanda ita kanta batasan anyi ba, shikuma wanda yakeyin shima baisanii ba."
Koda gyada *hanna* taganii ahanya tasaya mai gyadanan Sai anbii har gidan iyayenta anmata kyauta."
Alokacin da MG yake wannan abun shikansa baisan mai yake ji gameda *hanna* ba."
Aranar juma'a *hanna* ta zo makaranta bbu P.E dress, abakin gate aka tsareta, MG na cikin mota dan dama yadad'e awajan."
Duk yanda akayi da *hanna* qkan tasa tace ita bazata sakaba."
Kamar yanda ya lura da *hanna* kullum Sai anyii rikici da ita akan pink d'in abuu."
Ahaka bayanda suka iya suka barta dan idanda saboo yakamata su saba da halin *hanna*."
Washe garii MG yakoma kano."
Bayan yaje bai b'oyewa mahaifiyarsa abunda yake faruwa dashiba duk da dai bai shaida mata cewa wacece Yarinyar ba?"
Kuma bai fad'a mata shekrunta ba."
Alokacin ummii ta shaida masa cewa sonta yakeyi."
Bbu yanda batayi akan yafad'a mata gidansu da adress d'insu ba."
Amma firr yak'ii yace mata dasauran lokaci."

Zuwa sunday Sanda yakoma bauchii dan kwana biyu dayayi baiganta ba jiyakeyi Kamar ya shekara duk yavii ya susuce."
Yana isa mai makarntarsu yafara nqima yashaida masa komai kan yanaso acanja uniform zuwa pink, mai makarantar ganin kud'ii nan danan ya amince."
Monday dake student kowa yazo za'a bashi unifor kyauta."
Pink colour *hanna* tayi murna sosai."
A"inda iyayen yara sukayi mamakin ganin yanda mai makarntar yakeda son kud'ii amma harya iya kyautan uniform."

Ahaka *hanna* tacigaba da karantawa har zuwa lokacinda suka shiga secoundry na dariya tayi dariya na kuka ma tayishi."
Kukantane ya tsananta Alokacin da taga MG yarubuta sojojina sun dawo masu saida rake dan ta dalilinki, sojojina sun zamq masu shago ta dalilinki."
Sojojina sun zama y'an taxi ta dalilinki."
Duk wani taxi takika shiga iya tsayon girmanki, ina tsare dake, wannan abuun nayi shine dan kar ki had'u da wanda zai sayemun zuciyarki."
*Hanna* sojojina har kwasan kwata na layinku sunyi dan tsaron lafiyarki."
Aduk yanda kike sojojina *BIBIYARKI SUKEYI*."
Aduk lokacinda da kike wani abuu idan kin cire mutanen gidanku tom ina *BIBIYE DAKE* k'arfin da kukan *hanna* yayinee yasata barin karatun Sanda tayi kukanta t koshi sannan kuma afili ta furta tabbas banyii laifii ba danace *BIBIYATA AKEYI*   Share hawayenta tayi sannan tacigaba da karatun."

To be continued

Ur's
z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirrahmanirrahim_

Writing by
© _Zaynab Bawa_
( _z33iiyyb3rw3r_ )

_Like my page on Facebook :::Zaynab BAWA novels_

Followed me on instagram ::::mhiz_z33iiyyb3rw3r

*Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi yace."  Duk wanda yakaranta wannan addu'a, la'ila ha illallahu wahdahu la sharika lahu, lahul hamdu wa lahul mulku yuhyi ayumitu ahuwa hayyul layamutu wahuwa ala kulli shai'in k'adir."  Allah zai rubuta masa lada dubu sau dubu sannan zai yaye masa zunubi dubu sau dubu."*

*Yanada kyau karanta addu'ar nan bayan tashi daga bacci."   Alhmdllhillazii ahyana ba'ada ma amatana wa'ilaihinnushur."*

================

Page 71

*
Share hawayen fuskarta tayi sannan tacigaba da karatun."
Page na gaba da bud'e, Alokacin da tafara girma, alokacinne fargaba yadad'u wa MG yanda yaga dare haka yake ganin rana haka yake kallon dare, Koda bacci yakeyi mafarkinsa bai wuce na *hanna* ba, akwai lokacinda wani malamin su yadaketa akan batayi note ba sanadiyar korarasa daga aikii kenan."
Tsayawa *hanna* tayi da karatun tarufe bakinta da hannunta tabbas tasan lokacinda wannan abun yafaru kuma tundaga wannan lokacii bbu wanda yak'ara dukanta tabbas abun har mamaki yake bata, tarasa dalili sai yanzu tasamu dalili."
Cigaba tayi da karatun, quarter na teacher's dinku sojojinane, narasa wani irin so nakeyiwa *hanna* ko alabarii banta6ajin Labarin makaman ciyar soyayaya irin wanda nake mataba."
Ko a film banta6a ganiiba balle azahiri."
Hak'ika wannan jarabawa ta ubangiji ne, wanda ke jarabtar bayinsa Aduk yanda yaso kuma Aduk lokacinda yayi niyya."
Hak'ika wannan jarabawa ta fad'a kan MG, duk lokacin birthday d'in ta, Aduk k'asarda MG yake saiya dawo yayi wshng d'inta birthday ya ajiye mata gift da Hannunsa, har yakawo lokacinda *hanna* tafara mensturation, ana farko harsanda suka dangana da asibiti, ganin bayan ansallametane sukayi baincike abunda yakwantarda ita, aikawa MG details na komai sukayii."
Awatan yasa aka canjawa likitan asibiti zuwa wani babban hospital, sannan yad'auko wata female doctor wanda takware afannin mata, yasata a asibitin, wani month da *hanna* suka dawo bayan tagama yimata treatment saita buk'aci data runga zuwa tun kafin date yacika."
Ahakanne yad'an samu relief, shikuma  MG yananan yana bibiyar rayuwarta, Ahaka abubuwa sukayita tafiya dan har zuwa gama schooll ne secoundry,"
Tayi jamb ta samu admissn, tun daga ranarda tafara zuwa makaranta tun wannnan rana MG ke cikin fargaba, dan yasan yanayin jami'a dole za'asamu wanda zaija hankalinta."
Yanda yaci sa'a *hanna* bata kasance d'aya daga cikin masu rawar kan samarii ba."
Kodan batada farin jikinsu ne ohow🤷‍♀️, Yad'aura da cewa, nasha wahala sosai na rashin yin aure da wuri sannan na fuskanci matsaloli da dama tafuskan hakan." Amma har indai akan jiran *hanna* ne zan iya komai zan iya jira ko hakan yana nufiin zan iya had'uwa da wata matsalar, banjin arayuwa, banda ta fannin iyaye akwai wani abunda yafimun ita mahimmancii aduniya, banjin ko rayuwarda nakeyi takaimun tata,"
Bansan maiyasaba amma nasandai haka kawai nayanke shawarar barinki harsaikinkai 19 kafin naasanar dake, Sai gashi, zuciya ta tana taraddadin hakan, Kuma amma nakasa sanardake ko mahaifanki."
Akowani lokacii nakan rasa wani abune ke tsayarda nii daga yin hakan."
Sau dayawa naso sanarda mahaifina amma kuma konaje gabansa ban iyace komai, Hakanne yasa na tattara lamurana na miqasu ga Allah."
Ina addu'a kawai dannasan Allah zaijii kaina tun dashi yad'auramun wannan lalurar kuma zai yayr mun."
Wani page ta bud'e dasabon rubutu kamar haka,  Ayau na kasance cikin bak'in ciki, marar misaltuwa shine ranarda d'aya daga cikin soldier's d'ina yasanar dani cewa, *hanna* tafito daga lecture's har taje siyan abun shago, yabige wani mutum taje fad'uwa har yakamata, aranar

nashiga rud'ani dan hankalina yakasa kwanciya,  nakasa yarda da wannan mutum, K'arfe tara dai-dai na dare, tracer na wayar *hanna* ta  nunamin kan call yashigo wayarta."

Ya tsincii kansa da son Jin wayan, bud'e wa yayi ya fara jii, kafin yagama duk yabii yashiga tashin hankali."

Suna gama wayar akayi tracing na wayar sa."

Alokacin yasamu duk wani impormation dayakeso akan sa."

Ya nemo kuma yasanii, amma bai yi Tunaniin zai iya rabashi da *hanna* ba, dan alamu masu yawa sun nuna tana sonsa."

Ahaka MG yacigaba da rayuwar k'uncii amma hakan baisa yakaraya ko Sau d'aya daga sonta da kuma burin auranta ba."

Shidai kawai yabata lokacii ne itada saurayin nata."dan kokad'an jikinsa bai bashi cewa wancan zai aurii *hanna*  ba, yana yawan yin mafarkai akan cewa ya aurii *hanna*  dayarnsu, Koda mafarkai ba gaskiya bane amma kuma yanajin dad'ii da wannan mafarki."

Ranarda labarii yazomin cewa *hanna*  sun rabu da najeeb, narasa awani halii na tsincii kaina, ina tsananin tausayin *hanna*. "

Bayan karanta page dadama ne, yabud'e page d'in da MG ke cewa."

Yau ne takasance ranar farin ciki agareni, *hanna*  ta yarda zata aureni, Koda nasan batasona amma inada yak'inin wataran zata sonii."

Labarai ta runga karantawa kala-kala duk randa suka had'u da MG ko Murmushi tayi sayya rubuta."

Balle yakaiga dariya."

Har zuwa ranar d'aurin aure su, har diner da aka yi sanda ya rubuta."

Har zuwa tafiyarsa."

Rufe littafin tayi tana kuka sosai wanda har zuciyarta zafii take mata, tana cewa Allah natuba, natuba Allah wayyo Allah na, mijina kayafeni, wallhy nima inasonka, Allah wani irin soyayya ta ka jarabcii wannan Bawa naka da ita wanda komai nayi baya ganin laifiina."

Allah natuba, tanayii tana riqe cikinta, dan zuciyarta tana mata suya gabaki d'aya haushin kanta takejii."

Ga wani irin son MG dayaa kamata wanda ita kanta batasan akwaishi tun daba, ko kuma lokacin yashiga ba."

Tafii 30 minute Ahaka amma kuma bbu sauk'i zazza6ine ma yafara rufeta." Tashi tayi ta niyar gyara akwatin, tana d'agashi yafad'o yazube, pics d'intane ne acike da k'atuwar trolly d'in tun tana yarinya har izuwa girmanta, abundai bbu yadda za'a fassarashi."

Bata k'ara kaiwa awaa d'aya ba zazza6ine mai zafii yarufeta, ko iya d'aga hannunta batayi, Ahaka matar abid tashigo tasameta, kiran doctor tayi amma shima soldier ne, yaduba ta yakawo mata maganganuwa, batafii kwana 2 ba zazza6in yasauka zai kuma azabar sonjin muryar MG takeyi tanasonjin awani halii yake ciki?."   takira wayarsa hatta gashi baya shiga gashi 2 weeks kenan bbu wanda yajii Labarin su."

Itakam *hanna*  Idan kaganta tayi rama sosai, kullum ararrashinta matan abokansa sukeyi, dakyar takecin abincii."

Ummii ne zaune tasa afeeya agaba, fad'a takeyi kawai akan itadai aje ad'auko mata y'arta bazata iya da rashin abu biyu ba bbu yareema kuma bbu matarsa *hanna* dan kimanin 5day's

kenan kota kira wayar *hanna*  ba'a d'agawa."
Duk yanda sukayi su shawo kan ummii abun yagagara."
Suma kansu Suna cikin tashin hankali.".     Awashe garii afeeya tashirya da tatafii rushia da niyar dauko *hanna*."

To be continued

Ur's
Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirrahmanirrahim_

Writing by
© _Zaynab Bawa_
( _z33iiyyb3rw3r_ )

_Like my page on Facebook :::Zaynab BAWA novels_

Followed me on instagram ::::mhiz_z33iiyyb3rw3r

*Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi yace, (Hajaral muslimu akhahu.") wato musulmi ta k'aurace d'an uwansa."  Manzon Allah SAW, yace (kasafki damihi) wato kamar yazubarda jinin jikinsa ne. Hak'ik'a mai yanke zumunta yana cikin tashin hankali, Allah ka k'ara mana son y'an uwanmu acikin zuk'atanmu."   Ameen ya Allah."*

*Manzon Allah SAW yace, ita wannan duniya da kuke ganii, (alsijnil muminun) wato takasance kurkuku wajen mumini."   Yayinda tazama aljannah wa kafirii."   Ya Allah ina rok'onka kada kasa dad'in duniya ya rud'emu, mukasa aiwatar da abunda zai fisshemu aranar alqiyama, Ya rabb, kabamu ikon bauta maka akowani hali muka tsincii kanmu, sannan Aduk abunda muka mallaka muyi amfanii dashi wajan bautata maka."  Ameen ya rabbil izzatt."*

================

Page 72

*
K'arfe had'u na yamma jirginsu afeeya yasauk'a arussia, taxii tatsara ya kaita har zuwa estate na manyan sojoji."
Tun daga farkon layin sojojina azube, ako ina, shiga wajan yayiwa afeeya matuk'ar wahala

dakyar suka barta tashiga izuwa estate d'in."
Koda ta isa bakin gate d'in bbu yanda batayiba anhanata shiga dan wajen manyan sojojine, acikin sojoinma sai kanada appointment kake shiga, ko kuma yakasance kana d'aya daga cikin masu tsaron wajen."
Har magrib afeeya na wajen, takira wayan *hanna* ba'a picking." har ranta ya6aci sosai dan tayi kusan 3hour's tana kira."
Wani tunani tayi nan danan hankalinta yatashi, batasan Kowani abune yafaru da *hanna* ba yasa bata picking."
Gashi Duk wani shaida dazai nuna cewa ita y'ar uwar MG ne batazo dashiba balle tasamu tadubata ko Ipy, dan tasan hakan ba halin *hanna* bane."
Itakuwa *hanna* nacan ko breakfast batayiba dake yau cikin matan abid da shahid bbu wanda yaahigo."
Dakyar tasamu tashiga tayi wanka dan yunwa tacii jikinta sosai." Koda bayan tafito wayarta tad'auka taci gaba d kiran MG kamar kullum."
Abinda tasabaji shi akace wayar akashe take,"
Kukane ya kufcemata batasan awani hali MG ke ciki ba, ta tabbata da yana Ipy zai nemeta, maiyasa zaimata haka?" maiyasa sai lokacin da take matuk'ar sonsa zai tafii ya barta."
Dakyar ta tsagaita kukan ganin magrib tana neman wucewa, ta tashi jirii ne yafara ebarta, dasauri tazauna."
Sallarma sai azaune tayita."
Bayan *hanna* ta idarda sallan tana kan pray mat, tana kuka tana yiwa mijinta addu'a, dan tasan a halin yanzu abunda yafii buk'ata kenan."
wayarta dake can gefe ne ta k'arayin ring dan dama tadad'e tanajii tak'asa picking."
Cikin kasala tatashi amma yanzu jirin ba sosai ba tanufii phone d'in, dushi dushi take ganin wayar, picking tayi sannan takara a kunnenta, afeeya ne tasauk'e ajiyan zuciya Jin anyii picking."
Tana d'agawa bata jira amsa sallama ko gaiasiwa ba tace *hanna* ina gate, sunk'i su barnii nashiga."
To kawai *hanna* tace ta ajiye wayan." dakyar tafuta ad'akin zuwa falo nanma sanda tazauna tahuta tukunna, ta isa zuwa bakin k'ofa, d'aya daga cikin soldier's din dake tsaronta taaika dan bazata iya futaba."
Tana fad'a masa aikar tazube awajen ta kwanta tana numfashii sama-sama."
Shikuwa yana zuwa baisamu matsala wajen shigoda itaba."
Sanda yabud'e mata k'ofa yana riqe da trollyn d'inta sannan tashiga."
Adab k'ofa taga *hanna* kwance cikin saurii taqarasa ta riqota tana cewa, *hanna* *hanna* tanajii ana kiranta tayi k'okarin bud'e idanuwanta amma tana bud'e wa saiya koma luuu yarufe, dan wani irin jiri takeji wanda ko idanuwanta bazata iya bud'ewa ba."
Riqe ta afeeya tayi, Jin tana numfashi sama-sama yasata fita ariikice tayiwa soldier's magana nan danan akayi asibiti da ita." Asibitin dake cikin estate d'in suka wuce da ita, ana zuwa doctor yafara dubata, bai dad'e ba akayi admitiing d'insu."
Afeeya duk atunaninta ciki *hanna* kedashi, Allah Allah takeyi likita yazo ya tabbatar mata takira ummii tafad'a mata, dan tasan hakan zai kwantar da hankalin ta."
Bayan doctor yashigo, afeeya tace doctor meyake damunta?"

Nisawa yayi sannan yace batacin abincii ulcer takamata har tayi chronic  sannan tanqsaka damuwa sosai hakan har yana shirin sanya mata hawan jini."
Afeeya bata iya cewa komai ba gabaki d'aya tqusayin *hanna* ne yakamata tasan damuwarta bazai wuce akan mijinta ba."
Doctor ganin hankalinta baya jikinta yanakan *hanna* yasa yayi gyran murya."
Tana juyowa yace karki damu nan da safiya za'ayi discharging naku."
Daxaran drip d'in sun k'are zata farka."
Idan tatashi asamamata wani abunda zataci."
Y'ar karamar drawer yanuna mata yace,"  Duk wani abunda zaku buk'ata yana cikin nan."
Sannan yace bayan tacii abincii Idan tatashi tashige office na nurse akwai injections da madicines da zatayi taking."
Godiya afeeya tamasa yafita sannan kuma ta k'urawa *hanna* ido tana Mamakin irin ramar da tayi."
K'arfe 10:00 drip na *hanna* yak'are."
Sai, 10:25pm kafin ta farfad'o, waige waige tafara yi dan sanin inane yanda take."
Ganin afeeya tayi dake kan sallaya tana sallah batasan farkawarta ba."
Shiru *hanna* tayi tak'ura mata idanuwa har ta idar tajuyo da niyyar duba *hanna* ganin idanuwanta abud'e yasa afeeya tataso dasaurii ta isa wajen ta, sannu tafara yi mata itakuma banda Murmushi bbu abunda takeyi."
Tea tahad'a mata tabata dakyar tasha."
Sannan tad'anji k'arfii."  Juyawa tayi ta kalli afeeya tace Anty afeeya zanyi sallah."  d'agata tayi ta taimaka mata zuwa toilet tayi alwala."   Sannan kuma tafito azaune tayi sallah."  Tana sallah afeeya tafita taje takira nurse, dakyar akayiwa *hanna* allura sanda tahad'a da kuka."   har sanda tasaka Anty afeeya dariya. "  wajen shan maganii kuma ba'asha wahala sosai ba." riqeta afeeya tayi ta kwanta ajikinta tacii gaba da kuka."  dakyar tasamu ta sakata tayi bacci."
K'arfe 7:00am akayi discharging nasu."

_Kuyi hakuri da wannan wallhy Yau sai ahankali."_

To be continued

Ur's
Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirrahmanirrahim_

Writing by
© _Zaynab Bawa_
( _z33iiyyb3rw3r_ )

_Like my page on Facebook :::Zaynab BAWA novels_

Followed me on instagram ::::mhiz_z33iiyyb3rw3r

*Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi yace, kalmomi masu k'arfii akan harshe."* ```thaqilatan fil mizan``` *way'anda suka kasance masu nauyi akan mizani." kuma habibtan fir rahman." way'anda suka kasance mafii soyuwa awajan, Allah subhanahu wata alah." sune SUBHANNALLAHI WABI HAMDIHI, SUBHANALLAHIL AZIM."*

*wani mutumi yasamu Manzon Allah SAW ya tambayashi." yace* ```ya rasulillah man haqqan masu bihusnii sahabatihi````
*Waye ya wajaba akan mutane sufii kyautatawa."*
*Sai Manzon Allah yace mahaifiyarka, Sai wannan mutumii yak'ara cewa Sai kuma wa?" Sai Manzon Allah yak'ara cewa mahaifiyarka, Sai wannan mutumii yak'ara cewa thumma man, fa qala rasulillah thumma ummuk." sannan Sai Manzon Allah yace thumma abuk." yanada kyau ka kayautatawa mahaifiiya dan sanda Allah ya ambaceta sau uku kafin ya ambacii mahaifii." Allah kabamu ikon kyautatawa mahaifanmu."*

================

Page 73

*
Gida suka nufa, suna shiga afeeya tataimakawa *hanna* ta shiga wanka itakuma tafita dan shirya musu breakfast."
*Hanna* bata d'auki lokacii wajen wankan ba tafito dan ba k'arfiin jikinta takejii sosai ba." abakin bed ta zauna ta had'a kai da gwuiwa hawaye na zubo mata, tunaninta d'aya awani hali MG yake ciki." sallama afeeya rayi aqofar d'akin jin ba'a amsaba yasata shiga dan atunaninta bata futo awanka ba." ganin *hanna* tayi tahad'e kai da gwuiwa alamun kuka takeyi, dasaurii tak'arasa wajenta, ta ta6a kafad'unta *hanna* tayi saurin d'agowa cikin muryar damuwa afeeya tace *hanna* wai meke damunki ne? Kinsan kuwa mai doctor yace? Plz kidena saka tunani acikin ranki, jin haka yasa *hanna* fashewa da kuka tace anty ya zanyii wallhy wayarsa bata shiga tunda yatafii ko sau d'aya bamuyi waya ba kuma haryanzu bbu wanda yasan halinda suke ciki, k'ara wani kukan take tana anty nashiga uku wallhy idan wani abu yasameshi bazan iya rayuwa bbu shiba, anty kitaimakenii yadawo." wallhy inasaonsa anty duk abunda nafad'a k'aryane ban ta6a k'in saba, tasaka hannu akayi tana cewa nashiga ukuna." idon afeeya tabb yacika da kwalla tausayin *hanna* dakuma tausayin kansu narashin sanin halinda d'an uwansu yake ciki yakamata, tabbas tasan aranda akace sun rasa MG tashin hankali yashigesu har iya k'arshen rayuwarsu, mutumne wanda yafii kowa soyuwa aran dangii." bawai dan kud'insa ko mulkinsa ba a'a saidan kawai Allah yayishi dashiga ran alummah." zama tayi abakin gadon ta rungume *hanna* tana tana bubbuga bayanta dan duk wani abunda zaifito abakinta yanzu kuka ne shiyasata yin shiru kawai." hwaye tabb a'iidonta."

D'iga hawayen idonta yafarayi abayaan *hanna* aikuwa *hanna* ta k'ank'ameta tsam taqara sake wani kukan." shafa bayanta kawai afeeya takeyi dan bbu wata kalma dazatayi amfani da ita wajen nusarda ita, tasan dolene hanna ta damu, tausayinta ne ya dad'a malale zuciyar afeeyah,

Sunfii 15 minute ahaka sannan afeeya tasaka hannuwanta tashare hawayen idonta sannan ta d'ago *hanna* dake jikinta tasaka hannuwanta tana share hawayen tana mata murmushi cikin sigar lallashi tace kiyi shiru abunki kinji? jiya muna asibiti najii wasu soldier's suna cewa next week zasu dawo, dan haka ki kwantarda hankalinki cikin, nan danan *hanna* tafara murmushi, cikin zumudi tafara murmushi hawaye nazuba mata tace, da gaske?" jijjjga kai afeeya tayi tana gaskanta mata zancen tace kwarai kuwa."

Nana kaga fiskan *hanna* yahad'e hawaye dakuma murmushi riqo hannunta afeeya tayi tace maza tashi muje mucii abincii, *hanna* tace anty nak'oshi 6atarqi anty tayi tace hanna kina nufi idanya ganki ahaka zaiji d'ad'ine?" gara kicii abincii zuwa nanda satinn kya murmure sai yayi farin cikin ganinki, tashi muje tariqo hannunta, sai alokacin hanna tuna batada kaya ajikinta daga ita sai towel kunya ta kamata ta sunna kai ganinhaka afeeya ta gane mai take nufi, tasaketa tace kishirya saiki sameni afalo, sanna tamiqe tafuta, Tana gama shiri tafita falo tasamu anty afeeya tagama had'a musu komai zama tayi suka faracin abincin, batacii dayawaba tatashi da duk da damuwarta tad'an ragu amma fa haryanzu bawai dadin abincin takejii ba."

Tashi tayi takoma kan kujera tazauna ta lumshe ido ita ba bacci takeyiba amma kuma hankalinta ba'a wajen yake ba, zuciyarta duk wani abunda yahad'a ta da MG yakeyi, abubuwane yashiga yi mata yawo acikin kwakwalwarta, na murmushi tayi murmushi, duk abunda takeyianty afeeya na kallonta, itama murmushin tayi tana girgirza kai, tarasa wani irin so sukeyiwa junansu." wanda d'ayabazai iya rayuwa bbu d'aya ba."

Wucewa anty tayi dan gabaatarda sallar walha, tabar *hanna* sai juye juye takeyi amma idanuwanta alumshe." wani farin ciki ne acikin zuciyarta Jin cewa MG yakusa dawowa." koba komai yanzu hankalinta xai kwanta, zata samu peace of mind."

================

Hava mama yanzu dan Allah 1month hadda 2weeks kuma kice bazan fita ba." dama su saleem d'in basu fita yawo bane dasai suje, dan Allah mama karkice a'a wallhy nagaji dazaman gida." nisawa mama tayi tace toh karima tsoro nakejo gani nakeyi kamar idan kika futa wani abuu zai biyo baya." wallhy bbu komai mama bbu wani abunda zai biyo baya." yanzu zan sayo miki nadawo." nisawa mama tayi sanna tace ok tom kishiga wuntii dan tafii kusa, sai ki dawo dawuri."

Abida dake kusa dasu tace mama aike kika kulata, sai kace dole ance mata karta fita amma sai taurin kai." harara karima ta galla mata tace banson rainii ansa dakene? Kawarda kai gefe abida tayi sannan karima tacigaba dacewa dan Allah mama wallhy yau haka kawai nakeda sha'awan fita, nisawa mama tayi sanna tace kid'auki kud'in amma kada ki dad'e." toh tace sannan ta shiga ta zumbulo hijabii, tafito duk da haka hankalin mama bai kwanta taba tace, karima dawo kisa niqab bbu musu tadwo tasaka sanna tafice."

Tana fita da wuce wuntii market, tayi sayyayanta tsab, sanna tad'auki hanyar dawowa,  round about dake wuntii tana tsayae tana jiran keke napep, alokacin motan najeeb ya danno kai, ya juya  titi kawai idanuwansa suka sauka kanta, sanye take da blue na hijab har k'asa sai niqab, bbu abinda kake kallo banda kwayar idanuwanta." gabansane yayi mugun fad'uwa tun rabuwarsa da *hanna* bai ta6a ganin wanda takwanta masa araiba sai ita,  bai k'ara tsintar kansa awannan yanayi ba sai yanzu, dukk da dacewa baiga fusknata amma taa kwanta masa." ya nutsa cikin tunani harta tsari keke napep tafara tafiya." sai lokacin yadwo cikin tunaninsa yana kallo tafara tafiya yayi saurin bin bayqn keke napep d'in."
Ganin andoshi angiwarsu *hanna* sanda gabansa yafad'ii haka harzuwa k'ofar gidansu, alokacin yagama cinkewa, besan waceec ba, sanun kansane ba *hanna* bane to wacece, ita?" Haka yayita zama awajen har kusan 1hour ganin bata k'ara fitowaba, yasashi jan motar yatafii."

Waahe gari da 11:00am najeeb yaje gidansu *hanna*  yadad'e ak'ofar gidan yana jira ko zata fito amma shiru."  yakusan 3day's yana zuwa amma duk da haka bai ganinta, hakan yasa kawai yashare yacigaba da al'amuransa, amma kuma bawai dan yamanta da itaba yasa rai duk ranarda yaganta, in sha Allah sayya yi mata magana ."

_Plz kiyi hakurii da jina shiru kwana biyu, wasu y'an matsalolii ne amma nagode, da kiranku da massg d'inki, kj kwantarda hankalinku lpyna klau kawaidai y'ar matsalace."_

_Kujira na dare yau biyu zanyi_

To be contiuned

Ur's z33yy bawa

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirrahmanirrahim_

Writing by
© _Zaynab Bawa_
( _z33iiyyb3rw3r_ )

_Like my page on Facebook :::Zaynab BAWA novels_

Followed me on instagram ::::mhiz_z33iiyyb3rw3r

*Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi yace, "  *laula an aahukka ala ummatii*  yace dabadan zan takurawa al'umma taba yace, ```la'artuhum bissuwak inda kullil salat```  *yace dana umurcesu dayin aswaki ako wace sallah."   yin suwak babbar sunnace ta Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi, yanadakyau bin sunnonin Manzon

Allah Allah kabamu ikon bii."*

*Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi yace, " kullaa ummatii yadkulal jannata illa man abah, duk alummata zasu shiga aljanna, harsai wanda yak'ii, mamaki yaakama mutanen dake wajan sukace ya rasuliahi yanzu waye zaiqii shiga aljnnah?" sai Manzon Allah yace wanda yamun biyayya tabbas zaishiga aljannah, sannan yace wanda yasa6ani kuwa to tabbas yak'ii." Allah kabamu ikon yin biyayya ga manzonka."*

================

*Wannan shafin nakune ku kad'ai, sanda nijar, da QUEEN, nagode da k'aunarku garenii nijar inasonku sosai." ILYSM."*

Page 74

Washe garii *hanna* tataashi dasauk'in damuwarta, amma wani shafin na zuciyarta yana fargaban halinda yake ciki, idan kuma tayi tunanin hakan Sai tayita addu'a." hartajii sanyii acikin zuciyarta, haka har aka shiga sabon satii." anty afeeya kuma bata tafii ba, dan ita tafiso tatafii tareda *hanna* ." Washe garii tun sassafe *hanna* kwalliiya sosai ta shiga kitchen da kanta ta shirya masa abincii." sosai tayi kyau." zuwa yamma jikin *hanna* yayi sanyii sosai." anty afeeya dake zaune agefe tana kallonta tun d'azu gabaki d'aya tausayinta yagama kamata." ganin magrib ta doso yasa *hanna* tajuya ta kalli anty dake zaune cikin alamun karyewar zuciya, da rawar murya da sark'ak'iya tace anty haryanzu shiru bbu labarin dawowarsu."
Girgiza kai anty tayi tace, a'a *hanna* kada kiyi kuka kinsan fa ba rana aka yankeba kuma ba sanarwa akayi ba, tom ki yi hakurii, amma kuma mujirra zuwa gobe tukunna, ai shiru *hanna* tayi batace komai ba."
Har 10:00pm *hanna* afalo tana zaune sanda anty afeeya ta takura mata sannan tashiga takwanta."
Washe garii ma tun sassafe *hanna* ta tashi tafara aiki, kamata jiya sanda yagama komai sannan tashirya cikin ran tsattsen less mai kyan gaske." tayi kyau sabon y'ar rawar ta tafara buya,"
Anty afeeya da bata kallonta bbu abun da takeyi, duk tausayinta saiyabii yacikata." yauma komar jiya *hanna* batayi baccin kirki ba." sanda *hanna* ta shafin kimanin ten day's tanayiwa MG shirin dawowa amma bbu shi bbu labarinsa, ita kanta afeeya sanda tayi danasanin k'arya da tayi mata nacewa zasu dawo, tayi hakanne duk dan ta faranta mata rai."
Washe garii suna zaune afalo *hanna* tayi mata shi ta cinyan afeeya suna d'an ta6a hira, yana tace tafara ringing dake hannun *hanna*." ganin wandabekekira yasa jikin *hanna* yayi sanyii, dan tana mijinta ne, ita kuma nata mijin batasan awani hali yake cikiba." nan take mood nata yacanja."
Batasan mai anty afeeya ke fad'a ba hankalinta baya jikinta." tana gama wayar tadubii *hanna* wanda hankalinta baya wajan tace *hanna* shiru bata amsaba ta6ata tayi, firgitgit tataashi, Girgiza kai kawai anty tayi tace, *hanna* ki shirya yau muwuce nageria, abban adheel yakirani bayada lpy yanzu haka yana emergency, tak'arashe maganar cikeda tsantsan

damuwa."  dasaurii *hanna* yatashi tace subhanallhi, anty tatashi tace anty adheel kuma?"
Eh *hanna*  tashi ki shirya mutafii."  Girgiza kai *hanna* tayi hawaye na zirara tace anty kije kawai nikam zanjirashi." Girgiza mata kai anty afeeya tayi tace, a'a *hanna* bazan iya barinki anan ba."  tana kuka tace Allah anty bazan iya binki ba, wallhy zanzauna najirashi har iya k'arshen rayuwata,"  bayadda anty batayi *hanna* tabita ba amma tak'ii haka tana ganii takoma, ita kuma zauna zaman jiran MG."

================

Karimace dake zaune tana yiwa abida masifa tace, wallhy nidai zantafii, kintsaya kina 6ata mana lokacii, kina so jimawa kad'an *mama tace tafasa."
Itakuwa abida santa tagama iya shegenta sannan suka futa suka samu hafsat dake jiransu." futa sukayi zuwa gidan anty, idan kagansu baza kace ba y'an uwa bane, iya kulawa ana bawa su karima, dan bbu wani bamabamcii, soyayya sosai suke samu daga iyalan gidan."  iyakacin soyayya mama tana nuna musu, duk kwakkwafin mutum bazai gane ba ita ta haifesu ba." Itakuwa."  suma sun riqeta gamm tamkar mahaifiyarsu."
Gidan suka nufa, suna shiga suka sami antyy maman amal nazaune, da sallama suka shiga abida tak'arasa gefenta da gudu tazauna."  dan jininsu yahad'u sosai."
Rabon najeeb da gidan anty, tun auren *hanna*  dan fushi yakeyi dasu daga ita har mijinta, aranar kawai yajii sha'awar zuwa gidan kai tsaye gidan ya nufa."

============

Yau duk eatate yad'auka, gidan tv da radio Sai sanarwa ake da dawowan soldier's gobe, ai kuma farin ciki da fargaba duk yataruwa *hanna*   tanason ganin mijinta amma batasan awani hali zata ganshii ba, batasan yana raye ko baya raye ba."

_Nacika alqawarii_

To be continued

Ur's
Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirrahmanirrahim_

Writing by
© _Zaynab Bawa_
( _z33iiyyb3rw3r_ )

_Like my page on Facebook :::Zaynab BAWA novels_

Followed me on instagram ::::mhiz_z33iiyyb3rw3r

*Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi yace duk wanda yakaranta* ```waraddal lahul lazhina kafaru bi zaigaizihim lam yanaluu khaira akafallahull mu'umininal qital wakanallahu qawiyan aziza``` *Allah zai kareshi daga sharrin kowani irin hallita,*

*Allah subhanahu wata ala yana cewa, wala'iin shakartum la'azidannakum, yace idan kuka godemin nikuma zan k'ara muku, yanada KYAU fad'in kalmar Alhamdulillahi domin nuna godiyarka GA ubangiji. Koda ace Allah yajarabceka ta wata hanya, alokacin faruwar abun kalmar Alhamdulillahi ne kawai yakamata tafito abakinka A wannan lokacii." Allah yasa mudace ameen ya Allah*

================

PAGE 75

*

Kai tsaye gidan yayansa ya nufa, dan yayi kyewar gidan sosai, kobabu komai gidan na tariyo masa al amura dayawa."

Yana isa yafito yabud'e gate kasancewar bbu mai gadii, ya shiga da motar sa, parking yayi sannan yafito yanufii k'ofar shiga gidan, entercorm ya danna, jin k'ara anty dake zaune tadubii karima tace je Ki bud'e kofa, bbu musu karima tatashi dake ita baimai surutu bane sosai."

Hijab d'inta tad'auka tsumbulele har k'asa dake, dariya dukansu sukasa, anty tace saikace wata matar liman, cikin gidanma sai kinsa hijabii." abida ne tace anty rabuda ita Allah lokacinda muna gida gyallalukanta ma k'ananune." juyawa karima tayi ta nufii k'ofa ta rabu dasu dan ita yanzu, tafison manya manyan hijabai, zuwanta bauchi yasa tajii tana sha'awar canja d'abi'unta, duk da tunda d'abi'unta ba munana bane amma tanaso na yanzu yafii nada kyau." k'arasawa k'ofar tayi ta bud'e."

Shikuma kansa na k'ofa yana jira A bud'e, tana bud'ewa sukayi ido biyu gaban kowanne daga cikinsune yafad'ii, saurin yin k'asa da kanta tayi tanajin wani irin yanayi tace, kashigo, shiru yayi yatsaya yana kallonta itakuma ta sunkuyarda kanta tana wasa da yatsun hannunta, tunanine fall aransa yasan shakka bbu ita ce wannan yarinyar dayaganii, kasancewar, yanayin daya tsincii kansa irinna ranar, hijabin ta irinna yarinyar ranar, kuma gashi yau yaganta a gidansu *hanna* yau awajen anty hakan yanuna sunada alaqa da ita kenan."

Ganin yak'i cewa komai yasata juyawa takoma ciki, tana shiga anty tace wayene?" cikin sanyin jiki tace umm anty bansan shiba, amma nace masa yashigo." baisan tabar wajanba sanda yadawo daga dogon natsarinsa." nisawa yayi sannan yace ya Allah kada ka jarabceni DA abunda zaifii k'arfiina, ya Allah kada kasa mun son yarinyar nan kamar yanda kasamun na *hanna* na azabtu da shii, Ya Allah kamun za6in alkhairii."

Cikin sanyin jiki yasa kansa afalon had'eda yin sallama." dasaurii anty tajuyo tace A'a uncle munyii fushi kakoma kawai, fara sosa kansa yayi yana dariya yace agafarcenii, kaina k'asa

natuba, yana fad'ii yana k'arasowa."  dariya anty tayi tace dalili d'aya ne zanyafe maka." Dai-dai lokacin ya k'araso yana zama yace ai ahakanma nagode."

Kallon abida anty tayi tace tashi kije kidauko masa drinks da abincii."  saurin tsaida ita najeeb yayi yace a'a barshi kawai nagode, wucewa zanyii nace barina biyo, 6ata rai anty tayi tace badai baka huce ba?"  murmushin dole yayi yace, ai dolena nayi hakurii, tunda bawani yajamunba."  nima kaina bansan dalilin yin hakanba, jikin anty ne yayi sanyi tausayin najeeb yakamata, tace A Allah zaimaka za6ii mafii alkhairii, nisawa yayi baice komai ba."  sai alokacin suka gaisheshi ya amsa idanuwansa nakan karima, yatashi yace ni barin wuce, zandawo akwai maganar zamuuyii, toh sqika dawo kawai anty tace, sannan yatashi yafita."

================

Jin dawowarsu MG yahana *hanna* bacci kwana tayi tana sallolii da addu'oii, har gari yawaye *hanna* bata runtsa ba."

Addu'a kawai takeyi, dakyar ta iya tashi tafara yiwa MG girki, sosai tagwada nata basirar, masu aikii dama kullum sukan shigo suyii gyara amma yau itada kanta ta tayasu suka Gyare ko ina sannan, ta turara gidan, kowani lungu da sak'o yad'auki kamshii."

Shiga tayi itama ta fara nata wankan tadad'e tana wanka, sannan tafito turare kawai ta iya feshe jikinta dashi, amma ko powder kasa sawa tayi balle man le6e, fargaba tafii komai yawa aranta yanzu, doguwar riga ta zura, sai d'an kwalinta."  sannan tasauko palour ta zauna, bata dad'eba matar shahid taahigo dasaurinta tace, wa *hanna* ta tashi sutafii barrack, dan yanzu haka ance sun kusa sauk'a."  da Kallon tambaya *hanna* tabita tace dama banan zasu sauk'a ba."  girgiza mata kai tayi tace ainan gidajensu ne, zamuje taryanzu a barrack, mamakine yakama *hanna* ganin yanda bata damu sosai ba, hakan yana nufiin harsun fara sabawa kenan, waje sukayi sannan suka Shiga mota, ba'ad'auki lokacii ba suka isa."

Sun shiga *hanna* *hanna* sai kallo take binsu dashi ganin yanda matan soldier's da y'ay'ansu, tako ina ta leqa matane da yara, kusan duk matan fararen fata ne, d'ai-dai kune blacks, sai kuma soldier's da suke barbarje a barrack d'in."  12:00 alqrm yabuga na jirgi yasauk'a, kowacce sai raba ido takeyi wasu matan kuma wak'a sukeyi, ba'afii 12:30 ba sojoji suka fara shigowa wannna wajen, wasu na shigowa riqeda akwatin gawa ahannun su."  sai sunshigo ciki su ajiye."  duk wanda tahango mijinta aguje suke tafiya su rungumesu, wanda suka hango akwatii da pics na mijinsu kuma wasu zubewa sukeyi ak'asa, wasu na ihuu tashi d'aya wajen ya karad'e ga sojojii basu fasa shigaba, *hanna* kuwa gabanta yafara dukan taraa tara idanuwanta sunkawo ruwa, banda hawaye bbu abunda yake zuba."

Aikuwa can saiga abid ya shigo, yaronshine yafara hangoshi, jan hannun mamansa yayi yace momma momma yana nuna mata abid yace pappa, ganinsa sukeyi  gaban akwatin wata gawa, soldier's dayawa sun d'aukota da alamu ta babbane, nan gaban *hanna* ta matar shahid yafad'ii dan tabbas acikinsu mijin d'ayane."  kasa zuwa matar abid tayi dan daga alamu hankalinsa atashe yake, kowacce acikinsu raba idanuwa takeyi kozataga mijinta shiru bbu MG bbu shahid basusan wanene acikin akwatinba."  gashi basuga d'ayaba balle su tabbatar."  ganin an nufosu ne yasa zuciyoyinsu karyewa, har gaban, farisa sukazo matar shahid suka ajiye gawar sannan kowa yacire hulansa Aikuwa nan danan ta zube kan gawar tana kuka kamar rqnda zai fita zuciyoyinsu duk yakarye."  anrasa wanda zaiyi kanta ya rarrasheta, yaranta

k'ananune amma sun fahimta nan suka fara kuka Awanna lokacii *hanna* itama kukan takeyi natausayin fariisa dakuma nakanta narashin sanin halinda mijinta yake ciki." da guduu ra'iisa matar abid tashige jikinsa tana kuka, na tausayin y'ar uwarta, ita kuwa *hanna* ganin sojojii sunfara k'arewa harsuka k'are, yasata farajaa dabaya, mai hakan yake nufii kenan? Badai wani abuu yasamii MG ba yana asibitii, rufe kunnenta tayi tafara kuka inaaaa hankainta bazai iya d'aukan wannan zance BA."
Ficewa tayi tashige mota aguje, ta ce driver yatafii, suna isa bata barii yatsaida motarba tafice, aguje tashiga d'aki ta rufe kanta." kuka takeyi kamar ranta zai fita."

*NIGERIA*

karfe 1:00pm Dai-dai, jet yasauke MG A cikin gidan sarkii, jin jirgii ya tabbatarwa iyayensa shine ya iso." yana futa bai 6ata lokacii ba yashige shahin ummii ganin yanda tarame, ya bashi tausayi dasaurii yak'arasa yazube akan guiwarsa, ya rungumeta tsam, fashewa tayi da kuka, tak'ara k'ank'ameshi, dakyar ya rarrasheta ya saketa sannan yace, ummii na nadawo lpy dan Allah kidaina kukannan, share hawayenta tayi tace nadainaa, d'ana, tashi yayi yace barin shiga gun abba, dasaurii yatashi yafice dan damuwarsa kawai yawuce shahinsa yaga *hanna* , mai martaba yayi murnar ganin d'annasa, damacan yana boye damuwarsa ne dan yanda ummii kesaka damuwa ranta."
Baidade ba yafito ya nufii shahinsa ganin akulle abuu yabashi matukar mamaki juyawa yayi zuwa shashin ummii yasamu afeeyya har ta iso labarii ya isheta, ta guduu tatashi ta rumgumeshi tana cewa yaya ya baka fara zuwa wajan *hanna* ba?" dagota yayi yace dama *hanna* bata dawo ba?"
Gyada masa kai tayi tace yaya tak'ii dawowa, nan tafara bashi irin labarin damuwarda *hanna* tashiga, sannan tace masa har ciwo tayi, ai nanda nan idon MG yakad'a, son *hanna* yana k'aruwa azuciyarsa, jii yakeyi kamar amafarkii wai *hanna* ne take wanna abun kansa," yawuce gidane domin ganin *hanna* dan yanada ya'inin bazata zauna zaman jiransaba, amma kuma yasamu sabanin hakan, juyawa yayi zai fice, ummii tace ina zakaje katsaya kacii abincii." no ummii zan tafii wajan *hanna* bansan awani halii ta ke ba narashin ganina." share hawaye ummii tayi sannan tatashi yariqo, hannunsa tad'auki wermer tadamka masa tace, kacii abincii ahanya Allah yamuku albarka, sumbatar goahinta yayi ya fice."
Nan suka d'auki hanya dake jet ne k'arfe goma na dare suka isa, yana shiga alokacin *hanna* harta galabaita tsabar kuka." yawuce sama yanda yaga wuta akunne alamu da mutum aciki."
Dasaurii ya isa yana k'okarin bud'e kofar yajii akulle, da k'arfii yace, sweety am home, kamar amafarkii *hanna* tajii muryarsa aida gudu tatashi tabude, tana Kallon Sa atsaye da gudu tashige jikinsa, tana kuka sosai, har cikin jikinsa yakejin kukan, cikin kukan tafara inasonka wallhy inasonka idan kasake tafiyya kabarnii zanmutu." runtse ido yayi yanajin maganganun ta har cikin zuciyarsa, ganin takii daina kukanne yad'ago kanta, yahad'e bakinsu waje d'aya, ga mamakinsa *hanna* batayi kok'arin kwace kantaba sqima biye masa datakeyi."

To be continued

Ur's

z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

_Bismillahirrahmanirrahim_

Writing by
© _Zaynab Bawa_
( _z33iiyyb3rw3r_ )

_Like my page on Facebook :::Zaynab BAWA novels_

Followed me on instagram ::::mhiz_z33iiyyb3rw3r

```Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un😭😭😭😭 Allah yajikanka Allah yarahamsheka Allah yasa aljannah ce makomarka😭😭😭😭😭 , dan Allah muna buk'atar addu'arku, Allah yayiwa lecturer d'inmu rasuwa, mal muhammad muhammad, addu'arku tafii komai mahimmancii```
😭😭😭

*Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi, yace," ayatul munafiku na salatha, yace alamomin munafukai guda uku ne, izha hadatha kazaba, idan yayi magana yayi karya, wato mak'aryacii yana d'aya daga cikin alamun munafurcii, kuma yace," wa''iza wa'ada aklafha, kuma idan yayi alk'awari yasa6a yanadakyau riqon alk'awari, domin mai karyashi Manzon SAW Allah yace mana munafiki ne, sannnan yace waizaa tu'umina kana, kuma idan aka yarda dakai kayi ka cii amana." Allah katsaremu dacin amanar y'an uwanmu."*

*Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi yace," da'a ma yuribuka ila mala yuribuka, kabar abunda kake kokonto akansa izuwa wanda bakada kokonto akansa, wallahu ta'ala a'alam, Allah shine mafii sanin gaskiya, Allah kasa mudace."*

================

Page 76

*
Sunfii 30minute ahaka, sannnan MG yasaketa, kollon fuskarsa ta tsaya yi har sanda ya hura mata iska a idanuwanta lumshe idon tayi sannnan ta sake bud'esu akansa, ahankalii takai kanta saitin dai-dai zuciyarsa ta kwantar da kanta, dasaurii-dasaurii takejin bugun zuciyarsa." zagayeshi tayi ta hannayenta da k'arfii sannnan ta runtse idanuwanta."
Murmushi MG yakeyi yana k'ok'arin ganin fuskarta amma tab'oyeta cikin k'irjinsa." ganin atsaye take ko motsin kirki batasonyii yasashii sunkuyawa dai-dai kunnenta, yace heyy nadawo fa batafiya zank'arayiba, nokewa tayi tak'ara shigewa jikinsa, y'ar dariya kawai yayi aransa yanacewa yaushe *hanna* tafara sonsa haka, yanayinta kad'ai yanuna irin damuwar da
```

tashiga."  d'an rusuna tsayinsa yayi yad'auketa cakk zuwa cikin d'akin, har bakin bed yakaita ya zauna, sannnan itama ya zaunarda ita akan cinyarsa, k'ara shigewa jikinsa tayi, d'agota yayi yace bafa guduwa zanyi ba, girgiza kai tayi tace ni dai kawai kabarnii, Murmushi yayi kawai, ya sa hannuwansa yamata rumfa, rufff yarufeta a k'irjinsa, Haka suka zauna kowanne yanajin bugun zuciyar d'an uwansa, *hanna* jitakeyi batak'ii su dawwama ahaka har iya k'arshen rayuwarsu ba."  kaiwa bakinsa yayi dai-dai kunnenta, yace sweety inaso nayii wanka, d'agowa tayi ta dubeshii sannnan tace nikam bazan sakeka ba."

Lumshe ido yayi yad'an tsotsi lips d'insa yace, tom aiba damuwa saimuje muyii tare," dasaurii tad'ago kanta ta dubeshii, tace nifaa Allah wasa nake maka zansauka, tafad'a tana k'ok'arin sauk'a,"  riqeta yayi gamm yace aikuwa sai kinjee, yana fad'in haka yamiqe da ita yanufii toilet, tana wutsil wutsil amma bai diretaba sai cikin toilet, yana ajiyeta yafara k'ok'arin rage kayansa, saurin juyadda kanta gefe tayi ta runtse idanuwansa, sanda ta tajii k'aran ruwa ta tabbatar ta yafara wanka tafice da gudu, sauk'a k'asa tayi d'an tanadar masa abunda zai cii."  snacks da tayi kawai tasamu ta d'auko da drinks wanda tayi da kanta, a cikin d'akin tashiga ta ajiye masa, sannnan tafice dan girka masa abunda zai kama cikinsa."  kitchen tashiga tafayii masa abincii mai squk'ii wanda zaicii dawurii."  30minute tafara yin  abincin harya kusa kammaluwa, d'aki tashiga dan ganin koya fitoo amma har lokacin bbu shii bbu labarinsa."  komawa tayi sanda abincin ya kammala tazuba ay'ar karamar cooler tad'auka tayi sama, tunowa tayi bbu plate takoma tad'auko had'eda spoons da serving spoon tayi sama, sai alokacin tasamu ya fitoo, kallonsa tayi tace kafa kusan 1hour a bathing kawai, yana goge knsa da k'aramin towel bai d'agoba yace, sweety yazama dolene nayii wankan samada hour, kinsan nakanyii satii acan banyii wankaba, riqe baki *hanna* tayi sannnan ta zazzaro ido tace, 1 week fa kace, lallai kazama, d'agowa yayi ya6ata rai, ai lokacii d'aya tayi shiru yace nazama mehh."

Had'iye miyau tayi tace kazama jarumii, Murmushi yayi sannnan ya girgiza kai yak'arasa jikin dressing mirror, ganin bbu manda yake shafawa yasashi sauk'a k'asa, dan nemosu, baifii 15minute ba saigashi yadawo, bud'e k'ofa yayi ahankalii yashigo, kamshim da *hanna* tadad'e batajii bane yaziyarcii hancinta, harwani lumshe idanuwa tayii, tak'ara bud'esu sannan tajuya zuwaga k'ofa."  da Murmushi ta taryeshi harya k'araso, zama yayi kusada ita, yajawota zuwa jikinsa yace, wato nikike shirin cewa kazamii ko, yafad'a yana d'aga girarsa d'aya, girgiza kai tayi tace nifaa ba haka naceba ba, tafad'a kamar wanda maganar take tsoron  maganar, kamshin turaren MG ne gabaki d'aya yake fisgarta."  to me kikace yafad'a yana shafo wuyanta, lumshe ido kawai tayi takwanta ajikinsa, sannan tace bakacii abincii bafaa, nisawa yayi yace tohh kin danneni yakike tunakin zancii abincin,"

D'agashi tayi sannan tafara zuba masa abincin, kamshin abincinne yadakii hancinsa, lumshe ido yayi ya bud'e sannan yau zancii abincin matata kenan, d'aga masa kai tayi tacigaba da zubawa."  tana gamawa tasa spoon ta eba tafara kaimasa bakinsa, kwayar idanuwansa cikin nata bud'e baki kawai yayi tazuba masa."  Lumshe ido yayi dan dad'in abincin, sannnan ya bud'esu akanta, cikin muryar rad'a yace, i have the best wife, in this world."

Dariya kawai *hanna* tacigaba da bashi abincii yanacii yana santii yana gwada mata duk duniya bbu wanda yakaita iya girki, haryaciinyee plate d'in duka, drinks da eba nanma abaki tabashi, shima ya amsa ya shanye, sanda MG yai damm sannan *hanna* tabarshii, tana k'ok'arin miqewa yariqo hanunta yace sweetyyy, nasan kemafa bakicii komaiba, yunwa kikejii kicii abincii, shafa cikinta tayi tace tunda naganka sai najii na koshii, balle danaga cikinka

yacika, sai nima nawa yacika," Lumshe ido yayi yanajin wani nishad'ii nashigansa yace najii amma duk da haka cikii abincii." Bbu musu tadawo ta zauna tafaracii shikuma ya k'ura mata ido kawai, batacii sosai ba tatashii ta tattarii kayan tayi waje."
Tabar MG yana tunani kawai wani dad'ii yakejii waishine yau *hanna* take tarairaya, jiyakeyi kamar amafarkii, afilii ya furta, ya Allah kasa kodaa mafarkii nakeyii kada nafarka har abada."
Yana cikin wannan yanayin tashigo tasameshi tace, ka kwanta kayii baccii kahuce gajiya, afilii ya furta idanma mafarkii kikeyii kidena, danni ba baccii zanyiba kuma bansan ranarsa ba."
*Hanna* tade yafahimcii mai MG ke nufii yasata, shigewa band'akii dan yin wanka, gabantane yake fad'uwa, tana fargaba amma kuma bazata iya yiwa MG gardama akan abunda yakesoba, ayanzu yanda takejin sonsa akowani gabbai najikinta."
Shima runtse idanuwansa yayi Cikin zuciyarsa yana addu'a ya Allah kada ka jarabceni da abunda bazan iyaba, ya Allah kada ka nunamin ranarda zan rasa *hanna* arayuwata, bansan wani halii zai shiga ba." Ahaka har jirginsu yayi landing *hanna* tana bacci, baisan katseta daga baccinta data lula kuma alamun baccin yana mata dad'ii, hakanne yasa ya cewa su ummii su fara gaba, shi zai k'araso daga baya, akawai abunda zaiyine, su ummiii way'anda sukazo taryansu daga fadah sukabii," shikuma yazauna jiran *hanna*, ga mutane dayawa dasuka zo taryansa, kama daga shugaban k'asa governor's, ambasador's ministers, Senate, dasauran su."
Tafii 30 minute tana bacci, wata ajiyar zuciya tasaki, sannan tayi miqa ta had'a da addu'an farkawa daga bacci, ware idanuwanta tafarayi, akansa ta ware idanuwannata tass, murmushi yasakar mata, itama murmushin tamayar masa," juyawa tayi da niyyar ganin su umma amma taga wayam dasauri tamiqe tazauna, zaro ido tayi tace ina ummii suke?"
Suntafii gida." zaro ido tayi tace toh mu me muka tsaya yi?." kajimun yarinya, me kike tunanin natsaya yii, kozan tasheki a bacci ne?" ehem, common tashi mutafii." marairaice fuska tayi tace yi hak'uri dear, aida ka tasheni." intasheki kuma?." A'a kam gaskiya bazan iyaba." yanzu kawai tashi muje, nasan ana jirana." miqewa tayi tada'uko gyalenta ta yafa." ya riqo hannunta suka futa." ana bud'e door na flight d'in, flashes ne suka fara kashe musu ido, sa hannu *hanna* tayi ta k'are fuskanta, saida tad'an dad'e kafin tabud'e fuskan." sojojine atsaye bakin jet d'in, alamu ya nuna sundad'e a tsaye awajen," suna sauk'owa mutanen da sukazo taryansu, suma suka k'arasaso, hannu suka fara bashi kowannen su wasu na haugging d'in sa." amma dukda haka hannunsa yana cikin na *hanna* gam yariqeta, dan yasan *hanna* yanzu saita rikice batason hayaniya sosai, barin yanda yalurada ita kwana kinnan."
Ahaka har suka rakashi zuwa ga mota, duk yanda y'an jarida sukaso zantawa dashi bai tsayaaba, damuwarsa yakai *hanna* gida ta huta, dakansa ya bud'e wa *hanna* Mota tashiga yayinda mutanen wajan tsan-tsan mamaki ya tsaresu, lallai sun tabbatr duk Mulkin mutum sayya sauk'arda Kai a wajan mace, bud'e masa motan akayi sai shima ya shiga, haka suka tafii gayya guda zuwa fadah."
Bayan sun isa ne aka bud'e k'ofan *hanna* tayi saurin fita tanufii shashin ummii." su kuma
```

dasauran jama'a aka wuce cikin fadah."
A palour tasamu su ummii nan ta shiga tayi sallololinta tafito, tasamu abinciii tacii sannan tazauna A palour tarashe."
Data gajii da zaman ne tashige d'akin labba takwanta dan batajin dad'in jikinta." bacci tayi sosai sai Bayan sallan magrib tatashi." tayi sallan ta sannan tak'ara dawowa palourn tasamii ummii, su afeeya sun tafii."
Har kusan k'arfe 9 tana wajan ummii, sai lokacin marshall yazo suka wuce shashin su, komai agyare suka sameshi." saboda gajiya wanka kawai sukayi sannan suka kwanta."
Washe gari kuwa agida suka yini bawanda yafita, dan sun dad'e basu samii hutu irin hakaba."
Suna zaune afalo hanna tad'aura k'afofinta kan cinyan marshall tana danne danne awayanta," kallonta marshall yayi ya maido duk hamkalinsa gareta, yace, cutie, uhmm ta amsa, yakamata kije kingaida umma (kilishi) yau," kinsan gobe bbu lokacii kina wajan zancen walimah, bata d'ago ta kalleshi ba tace, zuwa jimawa zanje." tom kawai yace yacigaba da kallonsa dayakeyi."

K'arfe takwas dai-dai *hanna* ta zumbula hijabinta tanufii shashin kilishii koda taje a palour tasameta, da fara'a, kilishii ta k'ar6eta sai riritata takeyii, itakuwa *hanna* taji dad'in hakan, kilishii ne tayi wata y'ar dariyar da kana kallonta kasan ta munafurcii ne tace, y'ata nashiga tashin hankali sosai, lokacin tafiyarsu yareema, gashi kuma kema kika shiga wani hali, ga baki d'aya hankalin mu atashe yake, mungaza sukunii, sunkuyarda kanta *hanna* tayi tace, ai gashi mundawo umma yanzu hankalin ku zai kwanta, wata dariyar kilishii tak'arayi tace ai kuwa y'arnan, yanzu munjii sanyii sosai." aff kinga na sha'afah tun d'azu nahad'a miki zobo akan zan aika miki tunda kinzo aisai ki tafii dashi tafad'a tana miqewa, wani irin kwad'ayine yazowa *hanna* gabaki d'aya yawunta ya tsinke, Allah Allah takeyi akawo zo6on tasamu tasha, Har wani had'iye miyau takeyii."
Da k'aton jug kilishii tadawo riqe ahannunta, ajiyewa tayi agaban *hanna*, cikin kunya *hanna* tace umma a'iina zan samu cup, inaso nasha ne," dasaurii kilishii takwala wa wata kuyanga kira, umarnii tamata data d'auko cup, bata dad'e ba kuwa tadawo hannunta riqeda cup, ajiyewa tayi agaban *hanna* sannan tanemi izini ta zuba mata, k'ar6a *hanna* tayi takafa bakin ta tahausha zuciyarta d'aya, sanda tashanye sannan tatshi zata fita, umarnii kilishii tayi da a d'auki jug d'in abita dashi, godiya tayi sosai sannan tafice."
Wata dariyar rainin hankali kilishii tayi tacce lallai wannan yarinya, shsshasha ce, kokad'an batasan mai sonta ba, inbanda abinki niceh zan miki zo6on? toko shi mijinnaki baikai wannan matsayinba, taja tsaki."
Itakuwa *hanna* tana komawa sashenta, da kad'an kad'an taringa shan zo6on harta shanye tass, dan wani irin kwadayin zo6onne yakamata."
Sanda tashanye kafin ta tuno bata ragewa Marshall ba, d'aga kafad'unta tayi🤷‍♀️, sannan tace ohow, idan yazo zangaya masa." dan tunda yafita d'azu haryanzu bataga idanuwansa ba, shirye shirye bikkunan da za'ayi yasa Marshall baidawo gidaba Sai kusan 10:15pm." *hanna* na jiransa afalo dan yakanyii wuya ta iya bacci idan baikusada ita shiyasa take jiransa Yadawo."
da sallama yashigo ta amsa masa tana murmushi, yana zuwa ya zauna kusada ita."
Sannu da dawowa yauwa cutie ya gidan?" Lafiya klau, ya ayyukan? klau cutie na, gaskiya yakamata abarmunkai ka huta haka, uhmm ainakusa fara hutuna, sai nayi months banfita ko nan da door ba, dariya *hanna* tayi sannan tace," kahuta Sai kayi wanka naga Kamar agajiye

kake, kaman kinsani nagaji dayawa."  yafii 30minute akwance a cinyanta, idanuwansa alumshe, amma Kuma ba bacci yakeyii ba." *hanna* na wasa da gashin giransa dake had'e waje d'aya, bud'e idanuwansa yayi yace dear nagama hutun zanyi wanka." ok tom tashi muje."
 Bayan yafito awankane Har yayi shirin kwanciya, *hanna* ta dubeshi, afff namanta honey, naje nagaida umma,  harta bani zo6o."  gaban Marshall ne yayi mugun fad'uwa Jin ta ambacii zo6o, shikqnsa baisan dalilin fad'uwar gabanba."  shiru yayi baice komaiba, Sai Bayan *hanna* takwanta Har bacci nashirin ebanta, cutie yakira sunanata, uhmm ta amsa alamun bacci yafara kamata."  kinsha zo6onne?"
Uhmm nasha kayi hak'urii ban bar makaba amma gobe zanyi mana wani." I LOVE YOU, yafad'a tana k'ara gyara kwanciyarta, uhmm kawaii yace baik'arayin maganaba."
Kusan 3 nadare hanna ke kwance tana baccinta,
Shikuma Marshall Yana sallah, dan tunda *hanna* tafara way'annan irin abubuwan, bai iya bacci."
Bayan ya idarda sallan yazauna Yana addu'oii wani irin ihuu *hanna* takwala, tatashi tana ihuu tana riqe kanta,  tana cewa honey zasu kashenii, gasuncan, wayyo Allah tak'ara sake wani ihunn, tana shirin sauk'a daga gadon, da gudu Marshall yayi kanta."

To be continued

Ur's

z33iiyybawa

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by
*©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

_Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'S_

```Wani sahabi yace, rana mun kasance muna Sallah a bayan Manzon Allah (S.A.W) da Annabi ya dakko daga ruku'u sai ya ce Sami'Allahu Liman Hamidahu sai wani mutum daga cikin sahabbai yace Rabbana Walakal Hamdu, Handan Kasiran Dayyiban Mubarakan Fihi da aka gama sai Manzon Allah ya waiwayo sai ya ce Wanene ya fadi wannan sai mutumin yace Ni ne ya Manzon Allah sai Manzon Allah ya ce Naga Malaika talatin da "yan kai suna rigagato wazai rubuta wannan aiki yaje ya gayawa Allah.```

.
```

================

Page 83
*

Riqeta yayi, tayin saurin shigewa jikinsa tana kuka tanacewa Wallhy zasu kamanii."
Shhhhh yasa hannu abakinta dear bbu wanda xai kamaki."  kiyi shiru."
Shirun tayi tana ajiyar zuciya addu'oii yaringa tofamata Amma duk da haka tak'i sakeshi, Kuma tak'yin bacci."
Kiran sallah ne yasashi yatashi yanufii band'aki kank'ameshi tayi tace Ina zakaje?" toilet zanyii alwala ankira sallah."  girgiza Kai tayi Kamar mai shirin yin kuka tace dan Allah kayi sallah anan kada kafita, murnusawa yayi sannan yace tom dear taso muje muyi alwala, tare kuwa sukayi dan ko nan dacan bataso yamatsa, bayan sun idarda sallan ne yace cutie jeki kwanta nizan futa."
Girgiza masa Kai tayi hawaye na shirin zuba, matsowa kuasada ita yayi yace ya rabb, bazan fitaba maza wipe ur tear's, bbu musu ta goge hawayan," Jan hannunta yayi yakwantarda ita Shima yakwanta kuasada ita." addu'a yayi ta mata Har tayi bacci."  Sanda yaga baccin nata yayi nisa ne, yazare jikinsa yafice, dan biki za'ayii a government house, na murnar cigabanda k'asar tasamu na marshall."  7:00.am dai-dai, *hanna* taji Ana tashinta, cutie, cutie, uhummm ta amsa cikin muryar Mai bacci, tashi maza, bak'i zasu fara zuwa baki shiryaba." toh tace tana k'okarin miqewa, tashi tayi tazauna tana murmurza idanuwanta."  cikin shagwa6a tace wallhy ni hone,,,,,,,,  saurin yin shiru tayi ganin yadda ta bud'e idanuwa bataga komaiba."  wani tsorone ya ziyarcii zuciyarta."  tashi tayi jikinta Yana 6ari tayi bandaki, Kai tsaye bud'ewa tayi kozataganshi, nanma Wayan Kuma batajii bud'e k'ofa ba."  suran wayanta tayi tafuta, abakin k'ofa tatsaya tatambayi wani soldier nan yashaida mata ai tun asuba yafita, bata iya komawa cikin gidanba, Kiran labba tayi tace, habibty dan Allah kizo yanzu kitayani zama, toh labba tace sannan takashe Wayan."
Kiran hameeda tayi nan ma tace da'allah tazo."   jiran labba tayi Sanda tak'araso sannan suga shiga tare."
Tad'ii suka zauna yii, ba'adade ba kuwa saiga hameeda nan tashigo itada hafsat, dagudu ta rungume hafsat tana murnar ganinta."
Sunfii 15 minute suna hira kafin *hanna* taji muryar ammah, aikuwa da gudu tatashi tayi Kan Amma, itama Amma murnar ganinta takeyii."  sauk'a sosai *hanna* tamata Har tarasa mame zata kawo mata."  Ammah batafii 20 minute ba tatashi tace Jalal na jiranta amota."  kuka *hanna* tasaka tana cewa haba Ammah na, wata na nawa bangan Kiba? Da kina zuwa zakice Zaki tafii."
Jawota Ammah tayi tana fad'in haba d'iyata, kibar kuka, zuwa jimawa zandawo dakyar ta lallasheta tayi shiru."
K'arfe 4 dai-dai akafara walima, zuwa 6 aka gama, mama batazoba, saboda su karima."
*Hanna* sashinta tawuce, bayan angama,  tayi sallah ne tashiga kitchen, tafara had'a masa abincii, bata d'auki lokacii ba tagama dan dama bawani Mai nauyii bane."
D'aki tashiga tayi sallan isha, tafito tashiga kitchen dan dawoda abincin dining."  da k'arfii ta ji muryar Marshall Yana cewa cutieee, itama da k'arfin ta amsa, yess honey, am home, ok boo am

coming tafad'a tana wanke hannuwanta tafito."
Wayam tagani babu kowa afalon da k'arfiii tace honey where are you?" Jin shiru yasata shiga d'ayan falon nanma shiru babu kowa, Kuma da'alamu ba'a bud'e k'ofaba."
Komawa tayi nan danan jikinta yad'auki rawa, kudin dinewa tayi Akan Kujera, sai Kusan 11:30 taji k'arar bud'e k'ofa lokacin tayi kuka harta gaji, abubuwan dataji a wannan lokacii naban tsoro baya fad'uwa." Jin bud'e k'ofa tayi saurin juyawa." ganin Marshall dasaurii tak'arasa da gudu ta rungumoshi, tana cewa honey kafita dani daga gidannan, wallhy akwai aljanu aciki nibazan iya zamaba." kuka takeyii Kamar ranta zai futa."
Rungume ta yayi sosai Yana rattshinta, Amma *hanna* ta birkice masa, bayanda baiyiba daga baya Kuma tafara ihuu Kamar wata mai aljanu."
Da k'arfinsa yariqota ya rungume tsam ajikinsa." bayadda batayi ta kwace kanta ba, Amma takasa, dan ko jijjiga bayayi." Sanda yaga tadaina muzul muzul yad'agota, idanuwansa sunyii jawur, yarasa maiyake damun *hanna*, yarasa tayadda zai shawo Kan matsalarta."
Ido ya k'ura mata ganin yanda take sauk'e ajiyar zuciya."
K'ara maida ita jikinsa yayi, ganin bacci yad'auketa yasashi tashi da ita yanufii Sama, kwantarda ita yayi sannan Shima yawanta agefenta, Sanda yakai 2hours kafin yatashi yad'auro alwala, yafara nafila."
Bashi yatashi daga sallaya ba, saida yauma Kamar jiya, da ihun *hanna*, yaukam Har Gari yawaye bbu wanda ya k'ara rintsawa acikinsu."
Gari na wayewa Kuma wani irin bacci yad'auketa,"
Sai 12 tafarka,"
Marshall yab'oye damuwarsa kwataa kwataa yakii gayawa ummii maiyake faruwa, dan gani yakeyi Kamar zaishawo Kan matsalar."
Ahaka ya wunii bbu yanda yajeshi Yana tareda *hanna* itama bataso yafitan dan haka yazauna."
Saida 9 nadare yayi suna zaune akujera, sallamar intisar ce ta ziyarcii kunnuwansu." Amsawa sukayi ta shigo tazauna, gaisheda Marshall tayi tazauna, sannan ayatsine tadubii *hanna* tace sannuu, *hanna* Kuma ko kallonta batayiba. Balle tasan tanayii."
Miqewa Marshall yayi yace yawwa tunda ga intisarnan barina shiga wajan ummii na nemo Miki kindirmon kijiranii yanzu zandawo." to kawaii tace yamata peck a forehead ya fice." haryad'an fara tafiya yatuno bai tambayeta da yamrii takeso kokuma furaba, juyawa yayi yakoma palour d'in." muryar intisar ce takatseshi daga magarnarda yake shirin yii, tana cewa aike banza ce tunda nafad'a miki Saina rabaki dashi Kuma baki hannani kusantar yanda yakeba." idon Marshall harwani k'ankancewa sukeyi tsabar 6acin rai, idanda kalmar daya tsana arayuwarsa bai wuce a ambacii rabuwa tsakaninsa da *hanna* ba." cii gaba tayi dacewa, Kuma nayi rantsuwa bazanyi kaffara ba, sai kin d'andani rashinsa akusadake." *hanna* wacce kwataa kwataa batason hayaniya ta lumshe idanuwanta ko tanka mata batayiba."
Wata tsawa Marshall yadaka mata wacce ba ita d'aya ba Har *hanna* Sanda tarazana, Yana k'arasowa wajan yad'auketa da marii, bata ankara ba yak'ara mata wani."
Saida tafad'ii Kan kujera yanunata da yatsa yace fucemin, fucemin nace tun kafin na tattaka ki." da gudu tafice tana kallon tara-tara wani ikon Allah ne kawaii yakawota sashin kilishi, Jin kukanta kilishi tafito da gudu, ganin fuskar intisar akumbure, Maiya sameki? tafara tambaya, cikin kuka intisar tafad'a mata abunda yafaru." Wata ashar kilishi ta lailayo tasake, dan kaza

kazansa Akan wannan matar tasa zaimiki haka to wallhy nayi rantsuwa saina rabasu, saita fara haukar Tata da gaske, yanzu bakad'an takeyiba?"
To wallhy saitayi haukan gaske."  Kuma aure Kamar kin aureshi angama tafad'a tana surar wayarta tayi ciki."

To be continued

Ur's

Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by
*©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

_Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'S_

*Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un, plz ur prayer's are needed, yarinyar 6tana ta karye ak'afa😭😭😭 wallhy har cikin jikina nakejii, dan Allah ku mata addu'a."*

================

*Weldone dear, kinyi namijin kok'arii, a littafinki na BAYAN AUREN💑 , Allah yataimaka, yakara kaifin basira, muna jiranki alittafinki nagaba."  jinjina gareki."*

.

================

Page  84

*
K'arasawa kusada ita yayi yazauna, yace cutie kiyi hak'uri kinjii?"  am srry, jijjiga kai tayi sannan tace bbu komai tak'ara komawa ta lafe akan kujeran."
Haka yakasa futa dan tunaninsa d'aya, wani hali zata shiga idanya barta."

kilishii ce zaune a bedroom dinta, waya takeyi tana cewa, wallhy nagajii da wannan yarinyar,

duk abubwan da nakeyi amma abuu yacii tura, shawararki ta farkon kawai zanbii."  yanzu ki kirashi basai safiya ba, ahaukatarda ita, shiru tayi na y'an wasu dakikai sannan tace, to ai yanzu nagane, yanzu abunda nakeso kawai zuwa safiya, nafarka najii, ance tahaukace,"  zuwa safiya zanturo miki da kud'in."
Kashe wayar tayi tana hucii."

Da daddare kuwa marshall ganin yanda jikin *hanna* yayi zafii zazza6i yarufeta, baisamu daman yin sallah ba."  kwana tayi ajikinsa tana kyarma, shikuma yana riqeda ita haka bai iya runtsawa ba."
Da asuba dakyar yasamu ya kwaci jikinsa yayi sallah itakuma *hanna* ko sallah bata iya tashi tayiba."
Kusan 7 yasauk'a kitchen yahad'a mata tea mai kaurii, yahau sama, duk yanda yaso *hanna* ta sha tak'ii, dan bakintama rawa yakeyi."   har 9:00.am *hanna* bata bud'e idanuwanta ba, zuwa wannan lokaci iya tashin hankali marshall ya shigeshi."
Idanuwansa sunyiii jazirr, kamar qauta, hawayene kawai bai zuba a idanuwansa ba." hakanma dan yakasance mai taurin zuciya ne shine yahanashi zubda hawaye."
Sai 10:00.am kafin *hanna*  tatashi, sai yazamana kamar ancire mata ciwon."
Riqo hannunta yayi yace, yawwa cutie tunda kintashi, muje kisa wani abuu bakinki."  yatsine fuska tayi tace banfa yi sallah ba."  ok tom sha tea d'in da ke gabanki tukunna, ai lapiyanki klau baki fashin sallah, lalurine ko dear, gyada masa kai tayi, yad'auko cup d'in yana shirin kaiwa bakinta, wani irin juyawa kanta yafarayii, dafe kanta tayi saikuma tasake, tatsaya tana kallon sa."  kaiwa cup d'in bakinta yayi ta saka hannu ta bige cup d'in ya watse ajikinsa." kallo yabita dashi yace dear why?"   tsaki taja tatashi tayi hanyar waje, runtse idanuwa yayi."  kafin lokacin harta fita palour, dasaurii yatashi yabita, har yak'araso wajan ta, fincikota yayi yana cewa ina zaki je?"
D'agowa tayi ta sharara masa marii sannan tace gidan ubanka zanje, dasaurii tak'ara cewa nace gidan ubanka zanje, ta fad'a tana juyawa zata k'ara tafiya, mutuwar tsaye marshall yayi a'iiya saninsa *hanna*  bazata iya aikata hakanba."  afili ya furta something strange is happening."  k'arasowa yayi kusada ita yajawaota yariqeta gamm, ihuu tafara tana kwararo masa ashar tana dukansa harda cizo, ganin abunna ta yawuce tunaninsa yasashi kalleta tabaya, yanufii shashin ummii hankali tashe."

Kilishii zaune ad'aki sai zurga-zurga takeyi, ganin bazata iyayin hak'uri bane yasata d'aukan wayarta takira ta, tana d'auka ko gaisuwa babu tace nifa najii shiru."  haryanzu bbu wani labarii wannan matsiyaciyar bata haukace ba."    daga cikin wayar najii ance, kekuwa mai kikecii nabaka yana zuba?."  ya tabbatarmun zata haukace amma gaskiya bazatayi hauka tu6urum ba, dan suna yawan yin addu'a, eh kmadai menene tayi, inyaso saimu 6atarda ita."
Ahaka takatse wayar."

Yana shiga baisamu ummii apalour ba ad'aki yasameta da gudu yak'araso kusada ita cikin tashin hankali yafara cewa ummii *hanna*  ummii *hanna*  batada lpy, dasaurii ummii tamiqe

ganin halinda d'annata yake ciki, dukda bbu hawaye afuskarsa, amma kuma cikin kwayar idanuwansa ta fahimci irin tashin hankalin yake ciki."
Itama da saurin ta surii himarinta ta bishi abaya, danshi yarigada ya futa."
Tsakanin shashin ummii danasu *hanna* danisa amma few minute ne suka kaisu."
Bud'e k'ofan yayi suna shiga, aikuwa sukayi turuss ganin yanda jinii yake zuba jikin *hanna* ga baki d'aya tayi caka-caka da falon."
Duk ta yayyanka jikinta da gilasai, jin bud'e k'ofa yasata juyawa, aikuwa tana ganin su, ta jefo glass na humra dake hannunta, tarewa marshall yayi da hannunsa, nan da nan, hannun yatsage jinii yafara zuba, dagashi har ummiin kanta sukayi yana zuwa kuwa yariqeta kamar wanda take jira ariqeta, tayii luuu tafad'ii hannunsa, sumammiya." kuka ummii tafashe sosai tanayi tana magana." futada ita mota mukaita asibitii." cikin tsawa tace nace maka mufice asibitii."
Waje yayi da ita ummii nabinshi abaya tsabar tashin hankali tunkafin yazo har an bud'e masa mota tsabar irin kirin da yakeyiwa sajen."
Ganin marar lafiya yasa sajen yanufii asibitii direct."
Suna isa aka karbeta ciwukan jikinta akafara, mata dressing, sannan aka ce tana buk'atan jini dan yazuba ajikinta sosai."
Ajikin marshall aka eba aka fara k'ara mata."
Dakyar yayarda shima aka masa dressing ciwonsa, dan yafii jin zafin ciwon jikin *hanna*, ummii Dakyar tasashi yakoma gida yaje yagayawa mai martaba, dan ita bazata iya tafiyaba, alokacinma jimawa kad'an tashare hawaye jimawa kad'an tashare hawaye." Doctor yasanarwa da momy cewa *hanna* tana d'aukeda juna biyu na wata d'aya kacal, kuma sunyiii iya bincikensu basu samiii wata matsala akwakwalwarta ba."
Kuka ummii tarushe dashi na tausayin *hanna* da kuma abunda yake cikinta."
Roqon Doctor tayi da karya fad'awa marshall, dan batasan irin tashin hankainda zai shiga cikinba."
Kwanan *hanna* biyu a asibitii amma abuu gaba yake dad'awa, ganin haka yasa ummii tayanke shawarar sanarda umma, aikuwa ranar sunshiga tashin hankali barinma hameeda da yaya jalal." umma ne tahana fad'awa mama dan tana gudu mata tashin hankali." lokacii d'aya ummii da marshall suka zabge dan kowannensu cikin damuwa yake."
Idan kagansu zaka d'auka sune majin yatan."
Ganin ciwon yak'ii warkewa yasa mai martaba yacewa affan yaje yad'auko modibbo, sukuma likitoci sun bada shawarar fita da ita wajan likitan kwakwalwa."
Dasaurii affan yafito daga shashinsa, wuce kilishii yayi afalo tana zaune, kwala masa kira tayi, kai inazakaje?" umma wallhy abbane, yace ind'auko modibbo inkaishi asibitii, koda abunda zaiyii akan ciwon, matar yaya yareema,"
Gaban ummane yafad'ii, had'erai tayi tace maza jeka kad'aukomin intisar tana gidan hajiya salamatu, waro ido yayi yace umma, abban,,,, tsawa tadaka masa, kai da'allah rufamin baki, kaje kad'aukota tunda bawai guduwa modibbo d'in zaiyii ba."
Fita yayi ransa yana suya, yana fita takira wayan kawarta, tace ke abu ynason kwabewa, yanzu kiyi saurii kafin yaronnan yaje yadawo, a6atarda ita kawai tabar k'asar ga baki d'aya sannan, sannan arufe bakinta kada hankalinta yadawo bazata iya bud'an baki tafad'ii daga ina takeba."

  Daga cikin wayan aka ce mata kinsan shifa baya aikii saida sharad'ii, kilishii tace koma menene nad'auka, yanzu fa ko 30 minute kada ak'ara takashe wayan."

To be continued

Ur's
    Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by
    *©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

 _Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'S_

*Manzon Allah sallalahu alaihii wasallam yace, ku karanta suratul kahfii ranar juma'a, Allah zaicika maka haskenta har wata juma'ar, zaka kasance cikin haske da farinciki."*

================

*Godiya masu kirana danjin mai jiki, Alhmdllhy jiki dasauki, siyama na amsa gaisuwarku tana godiya, nagode sosai queen najii dad'in, kulawarki sosai, Nagode all, Allah yabar k'auna."*

.

================

Page 85

*
  Umma ce zaune itada ummii cikin aminity, suna hutawa, sunfita sunbar *hanna* ita kad'ai hameeda kuwa tatafii yin abinci, ko *hanna* zataci dan idan akayi sa'a, dan wani lokaci akanyi sa'a ta d'ancii abincin ko kad'an ne."
 *Hanna* na hango tafito daga cikin d'akin da take, doguwar riga ajikinta, kanta ko d'an kwali bbu."  hankalin su ummii kwata-kwata bayi wajan, kamar wanda wani abun yad'auke musu hankali."
Har *hanna* tafice acikin wajan bbu wanda yajuyo, haka harta fice daga harabar asibitin bbu wanda yatsayarda ita, dukda alamomii dayawa ajikinta yanuna ba cikkken hankali atattare da

ita."
Tana fita ta tsaya atiti kamar mai jiran abun hawa, wata taxi ne tatsaya da wani mutum aciki mai wata irin halitta, wanda kollonsa kad'ai zai saka cikin shakku, kayi tunani koba mutum bane."
Nikaina zuciyata tafii kar kata, dacewar aljanine, magana yayi cikin wata irin murya, mai rikitarwa yacewa *hanna* shigo muje, bbu musu hanna tabud'e motar tashiga gidan baya, nan kamar wata walqiya yaja motar yayi gaba."
Kusan awah biyu suka shud'e."
Can nahango *hanna* tana tafiya duk k'afofinta sun fashe alamun tayi tafiya sosai."
Tana tafiya har tahau kan titi, unexpected wata mota k'irar jeep tazo wucewa ganin mutum akan hanya yasa tayi gefe da niyyar kaucewa, amma inaaa, sai dayazo dabb kamar wanda aka tunzurata, saijin kawai sukayi sun bigeta, salati mutanen cikin motar sukasa, nan suka samii waje suka tsaya, matan dake baya cikin motanne sukayi saurin fitowa sukayi kanta." ganin jinii yanabin kanta yasasu, kwalawa wanda yake driving d'in kira, dasaurii yafito, wani saurayine kyakkyawan gaske, duk wani alamu najikinsa yanuna, cewa shi cikkken bafulatani ne, dan da fullan cinma suke yin magana, amma saidai yanda najii suna fillancin gabaki d'aya ya banbamta, dana k'asar nigeria, kinkimanta yayi yasata acikin motar dake seat ukune da ita, asibiti suka nufa lokacii guda, dake manyan mutanene ba'atsaya bincikeba aka k'ar6eta aka shige ciki da ita."
Basu dad'eba aka futo aka shaida musu cewa, jikin alhmdllhy bataji, wani ciwo sosai ba."
Sannan d'an dake cikintama lapynsa klau."
D'aya matarne tadubi, D'ayan wanda da'aalamu tagirmi D'ayan, tace, diddii naga kamar k'qramar yarinyace kuma budurwa."
Allah dai yasa bawasu mugayen bane suka mata fyade suka yasarda itaba." nisawa wanda aka kira da diddii tayi tace,"
Allah shi yabarwa kansa sanii hussentu, abunda yakamata yanzu ina shii sadiq yashiga?" nisawa hussentu tayi Sannan tace," ya tafii k'ar6o maganinne, to Allah yadawo dashi lpy."
Bayan yadawo da 1hour *hanna* tafarka, duk iya tambayar duniyarnan anyi mata amma takasa bud'e baki tafad'i ko kalma d'aya," da suka isheta da zantuka kawai saita sheqe musu da dariya, harda kyakyatawa, ganin haka yasa suka nemi likita." yana zuwa yafara dube dube, nan aka shiga da ita d'akin na'urorii, iya bincikensu baigwada musu akwai wata matsala, akwakwalwarta ba."
Hakan yafito yashaida musu sunyii matuk'ar mamaki, tunda duk wani alamu yanuna ta6in hankali attatere da ita." 2days aka sallamesu gidansu suka nufa."
Nan diddii tabuk'acii sadiq daya d'auki pics d'inta yazagaya ya aika gidan redio, television, dasauransu, ko za'a dace, Hakan kuwa akayii, and'aukii 5days sadiq yana sanarwa, amma bbu ko batan hanya da wani yazo dan nemanta."
Agajiye liqis sadiq yadawo yazauna, wata mata wanda daga ganii y'ar aikice takawo masa ruwa, bai iya shan ruwanba, yadubii diddii yace," diddii duk iya cikiya nayishi, aksarnan bbu yanda bankai cikiyaba amma bbu."
Nifa atunanina yarinyarnan ba y'ar k'asar camroon bane, camroon na maimaita cikin raina😳🙆, Allah kawai yakamata mu miqawa komai mucigaba da mataa addu'a, kuma muna nema mata maganii."

Diddii bata iya cewa komai ba sai Allah yabata Ipy."

Basu ankara da cewa *hanna* batanan ba saida hameeda takawo abincin tazo da samesu, aresting room d'inda suke zaune tace," Umma nakawo abincin, dasaurii ummii tamiqe tace barina je toh ko zata cii na rarrasheta, d'akin tanufa tana shiga taga wayam, koda mamaki ne yacikata dasaurii tayi toilet nan ma bbu kowa, fitowa tayi nufii gun Umma tana cewa kinga yanda *hanna* tayine? Dasaurii Umma tamiqe tace banganeba? Aimuna zaune dake anan, *hanna* bata d'akinne? Ummii bata tsaya bata amsaba, tawuce tafara dube dube a cikin asibitin, Umma ma tabii bayanta jikinsu duk rawa yakeyi." duk girman asibitin acikin few minute suka zagayeshi, bbu ita bbu dalilinta, bakin gate suka yi suna tambayar masu gate ko sunga fitarta,"
Aikuwa sukace basu ganiba, dan kamar wanda aka rufe musu ido."
Waje sukayi suna tambaya nanma bbu wanda yace yaganta, sunshiga tashin hankali kam sosai, kowacce kuka takeyi bbu mai lallashin wani."
Wani d'an tsoho dazaikai 80yrs, wanda tun fitowar *hanna* shi kad'aine yalurada ita kasancewar, yanada d'an bud'edd'en ido, yamatso kusada su yace," bayin Allah wa kuke nema haka?." dasaurii Umma tace y'armuce tafice daga asibitin kuma kowa yace baiganta ba." shiru yayi nawasu lokaci kafin yace," kafin yace naganta da doguwar riga ajikinta, dasaurii ummii tatashi tace itace wallhy itace."
A'ina take?" girgiza kai yayi yace kucii gaba da addu'a, Allah zai bayyanata, Su kansu wanda suka d'auketa basufii k'arfin Allah ba." zaro ido sukayi mekake nufii kenan da Hakan?" wata y'ar dariya yayi yace, ai addu'a da kuke yi, da wanda mijinta keyi, da wanda ita kanta keyi yasa basu cutarda itaba, yanzu haka tana hannun mutanen arziki, idannace ku kwantarda hankalinku nikaina banmuku adalci ba." kawai kuyita mata addu'a, bbu abunda yafii k'arfinta, atake ummii tazube awajan sumammiyya, dasaurii sukayi kanta, dai-dai tsayuwar motan abban wanda yad'auko middibbo,"
Dasaurii yak'arso baitsaya tambaya ba, ya kinkimi ummii yayi cikin asibitin da ita, Umma kuwa alokacin suka nemi mutuminnan samada k'asa suka rasa, dasaurii sukayi ciki, duk iya tambayar affan bbu wanda ya iya bashi amsa," ganin Hakan yasa yak'ira marshall ya shaida masa yazo hospital."

_Kuyi hak'uri kuyimun uzuri, bayadda na'iya, amma in sha Allah cikin month d'innan zangama_

To be continued

Ur's
z33iiyybawa

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by

*©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

_Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'S_

```Dan Allah kada mu gaza wajan taimakawa y'an uwanmu akan buk'atunsu, dan Allah damuwar wasu ta Zama tamu damuwar, koda bazaka iya taimakawa, ta wani hanyarba, yanada kyau, ka taimakeshi tahanyar addu'a, dan kaima watarana, zaka buk'acii ataimaka maka koda tahanyar addu'a ne danshine babban tainakon da mutum zaimaka aduniya." nidai zaynab bawa ina buk'atar addu'oiinku daga bakunan ku masu albarka."
Balaifii bane kuma ba gazawa bane ko kankastar dakai neman taimako na addu'a ba, tabbas bakasan bakin wani ba, danna roqii alfarmar addu'a awajenku nasan zakuyimunne, nagode."```

================

```This page is dedicated To you, FATIMA IBRAHIM(MUNEERAT)
and SAWWAMA QAWWAMA (doughter) Allah yabarni tare daku har abadan."```

.

================

Page 86

*
Jin kiran gaggawa daga asibiti yasa hankalin marshall masifar tashi, tun d'azu kawai yana meeting ne amma kuma hankalinsa na hospital, yarasa dalilin dayasa tunda yatashi gabansa ke fad'uwa hakanne yasa dakyar sanda ummii tasaka baki kafin ya halarcii meeting d'in."
Ana cikin yii ko excuse bai d'aukaba ya fice, soldier's suna kallonsa sukayi saurin bud'e masa k'ofa, dasaurinsa yashige, drivern yafara driving har suka iso hospital d'in, dasaurii ya fito ya nufii ciki suma suka mara masa baya, sanda yazo bakin k' kofar shiga d'akinda aka kwantarda *hanna* ne sukaja suka tsaya, shi kuma yak'arasa, ganin ummii akan gadon marassa lpy dasaurii yak'arsa yana tambayarta mai yafaru?"
Ummii wani abune yasameki?" maimakon naga *hanna* naganki kota samu lpy ne?"
Muryan affan ne dake bayansa yakatseshi, yace yaya wallhy tund'azu nafad'a musu su sanarda ni abunda yake faruwa amma kuka kawai sukeyi bbu wanda yakulani."
Dasaurii yakuya wajan Umma yana cewa Umma wani abunne yasamu *hanna* Umma dan Allah kifad'amun, jijinsa rawa kawai yakeyi."
Kawarda kai gefe Umma tayi bata iya bashi amsa ba, gabaki d'aya tausayinsa ne yayi mugun kamata, kuka kawai takeyi, yajuya zuwaga hameeda dake k'asa numfashinta yana kok'arin d'aukewa, ai kafin yak'arso yasamu damar tambayar ta numfashinta yad'auke cakk, nan ta

sulale k'asa sumammiyya."
Muryar ummii ne ta daki dodon kunnuwansa,
Tana cewa Abdallah *hanna* ta6ata wallhy bamusan yanda takeba."
Zuciyarsa ne tayi wani irin bugawa take wani abuu ya tunkaroshi da k'arfii ak'ok'on Zuciyarsa, abun tasowa yakeyi har wuyansa, tashi d'aya yayi wani tarii gudan jini ne yafad'o wanda duka d'akin sanda ya suka jijjiga, dasaurii affan yayi kansa yana kiran sunansa amma, d'aga masa hannu kawai yayi yatsaya cakk, yayinda shi kuma yaja da baya, yajingunu da bango, yazauna ya sunkuyarda kansa, d'akin yad'auki 10 minute ahaka bbu wanda ya'iiya magana, ga hameeda asume marshall kuwa ban isa ince yana sume ko yanada rai kokuma baudashi ba."   ga ummii itama hankalinta yayi masifar tashi naganin aman da marshall yayi."
Umma kuwa tadawo mutum mutumii."
Haka ummii tasauko tanufii marshall Tana kuka tana masa magana amma ko kiftawa idanuwansa bayayi, haka tayita jijjigashi ko motsi bai yiba."
Zama tayi kawai agabansa, tana kuka, ganin abunda ke faruwa, yasa affan ficewa yasanarda mai martaba, ba'ad'auki lokaci ba ya'iso, hospital d'in,

Yana zuwa ganin abunda ke faruwa, yasa hankalinsa mugun tashi, nan aka kira doctor's aka tafida hameeda, yayinda shikuma marshall mahaifinsa yayi kansa yana masa magana, amma ko motsi baiba."
  Ganin haka yasa mai martaba dakyar ya lallashi ummii aka tafii da ita gida, Umma kuma tana wajan hameeda."
Awah ukuu curr marshall yad'auka awannan hali."
Wata ajiyar zuciya mai k'aran gaske ya sauke, itane tajawo hankalin mahaifinsa, k'arasowa kusada shi yayi yana kiran sunansa, d'agowa marshall yayi da jajjayen idanuwanshi, yatsare mahaifin nasa da kallo kamar wanda yau yata6a kallonsa."
 Nisawa mai martaba yayi yace, yareema tashi mutafii gida, girgiza kai yayi yace A'a abba bazan tafii ba, zata dawo, zan jirata."  girgiza masa kai mai martaba yayi yace Zamu nemota kataso mutumii, zaiyi magana mai martaba yayi saurin katseshi yace, kada muyi haka dakai, yareeema ka tashi mutafii, har indai nine nahaifeka kabii umarnina, miqewa yayi yana Shirin fad'uwa mahaifinsa yayi saurin riqoshi, haka yafita dashi daga cikin asibitin yariqe hannunsa kamar k'aramun yaro, shikuma yana ta kalle kalle, haka mai martaba ya sashi amota suka nufii, gida."

   *PLZ KUTAYANII DA ADDU'A WALLHY INACIKIN DAMUWA SOSAI ,😭😭😭😭😭 INA CIKIN MATUK'AR DAMUWA , DOLE INA BUK'ATAR ADDU'A DINKU , KUYIWA GIRMAN ALLAH KUJII TAUSAYINA KUMIN ADDU'A ."  KARKU GA TYPING YAYI KAD'AN AYANAYIN DA NAKE CIKIMA DA BAZAN IYABA, BUK'ATAR ADDU'A DIN KU DA NAKEYI NE YASA , NAYI , DAN AllahT KADA KU MANTA DANI ."*
*KU D'AGA HANNU KU ROQAMIN ALLAH YABIYAMUN BUKATUNA.*

  *Kuyi hak'uri ko zakuga mistake, wallhy dada rana nayi typing da yayi yawa amma yanzukan sai neman gyaran ubangiji."*

To be continued

Ur's

Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by
*©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

_Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'S_

```Manzon tsirada amincin Allah su tabbata agareshi Yana cewa Allah ya jikan wanda ya yi sallar nafila raka'a hudu kamin la'asar.```

```Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi yace, Wanda da yi Sallar nafila a cikin duhu inda bawanda zai ganshi to Allah zai' linka masa sau ashirin da biyar na sallar da zai yi wani ya ganshi.```

```Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi ya ce, Wanda yayi sallar walha (Sallar hantsi/Luha) rakaa hudu kuma yayi rakaa hudu kamin sallar laasar, Allah zai gina masa gida a cikin aljanna.```

.
================

Page 87

*

Fad'in irin tashin hankalin da marshall yashiga wannan ma tsayawa, bata lokaci ne, gabaki d'aya yazama wani iri,  bud'e idanuwansa ma wahala suke bashi, balle aje ga cin abincii ko wani abun."  nauyii idanuwansa ke masa, alokacinne yak'ulla mugun alaqa da ciwon kai, wanda akullum kansa ke barazanar tsagewa gida biyu,
Baida sukunii, baida wani sauran kwanciyar hankali, kullum cikin zullumi da tunanin yanda *hanna*  tashiga yake, tunaninsa ko awana irin hali take, baisani ba." a kullum har wani hucii ne
```

mai d'umi yake fita daga jikinsa, idanuwansa kuwa idanya bud'e yanda kasan garwashi, har shakkarr bud'esu yakanyi, dan har indai mutum yana kusadashi sayyya razana,  sa'ii-sa'ii yakanyi aman jini, amma bai bari kowa ya lura ba, koda sallah ma ad'aki yakeyi, ummiii tayi kukan harta gajii,

Ganin bbu Wata mafita yasa umma takira mama akan tanason ganinta idan zata samu dama suzo suda baba, dafarko mama tayi tunanin su hassana da hussaina,
Hakan tafad'awa umman, amma umma tace mata tabarsu ma ammah tazo, ganin zancen mai k'arfii ne yasa tasanarda baba, kiran k'aninsa yayi awaya, abba yacewa baba gaskiya yanadakyau zuwannasu, haka suka shirya washe garii suka d'auki hanyar kano, sha d'aya tamusu acikin garin kano, gidan Abba suka wuce kai tsaye, ganin Wata irin ramar da umma tayi mama ta matuk'ar tsorata, dasaurii tak'arasa kusada ita, riqo hannunta mama tayi cikin kid'ima tafara magana, yaya menene yasameki haka?"  yaya dama bakida lpy ne baki fad'amunba?, girgiza mata kai umma tayi kawai hawaye nabin fuskarta, da sallama abba yashigo falon, ganin umma na hawaye yasa yace ashsha assha, yanzu daga zuwansu kintaryesu da kuka, hava da Allah wai kekam bakyada hakurii ne, kuma bakida juriya, hava, idon mama har yacika da hawaye tashi d'aya yafara zubo mata takalli abba tace dan Allah kafad'amun ko wani abun ne ke damunta, rintsawa abba yayi kafin yace, kuzauna ku huta kafin namuku bayani, girgiza kai mama tayi tace, nidai bazan iya wani hutawa ba, bayan Ina kallon y'ar uwata cikin wani hali, juyawa abba yayi batareda yak'ara cewa komai ba, yanufii babban palour wajan baba."
Duk yanda mama taso tambayar umma abunda ke faruwa takasa sanarda ita, abba baifii 10minute da tafiya ba ya leqo yace, sutaso su tafii, tunda suka d'auki hanya bbu wanda ya iya magana, ganin sun nufi fadah yasa gaban mama da baba yayi mugun fad'uwa tunainsu d'aya badai wani abun bane yasamu *hanna* sunfii ma karkata da ko batada lpy ne, har suka isa fada, bbu wanda yatofa ko da kalma d'ayane, dama ansan da zuwansu, dan haka falon mai martaba, aka sauk'esu marshall na kwance tun shigarsu afalo, amma bai iya d'aga kansa ya kallesu ba balle susaran zai gaidasu abun bak'aramun mamaki yabawa baba da mama ba, banda umma da abba dan dama sunsan irin halinda yake ciki, tunda *hanna*  ta6ata bai k'ara furta ko kalma d'aya ba, ummii da mai martaba ne sukayi sallama suka shigo falon daga d'akinsa, waje mai martaba yasamu yazauna, sannan yabawa su abba hannu suka gogaisa da addu'a yabud'e taron sannan yafara magana."
Kusani cewa Duk wani abunda yafaru muqadda rine daga Allah, kuma Allah subhanahu Wata ala yace, la yukalliful lahuu nafsan illa wus'aha, yace Allah baid'aura rai abunda bazata iya ba." sannan Kusani kowani d'an adam da irin hanyardaa Allah ke jarabtarsa, sai dai muyi addu'a Allah yabamu damar cinye tamu jarabawar data fad'o mana, sannan d'aukan qaddara yana d'aya daga cikin cikon imani, musani Allah baid'aura mana abuu har sai dan yagwada imaninmu
Yaga yaya jamuyi dan yajarabcemu, tundaga wannan lokacii ummii tafara hawaye tana goge hawayen idanuwanta, nan mama tak'ara karyewa sosai tace," ku gayamun maiya samu *hanna* mu musulmaine tabbas zamu kar6i kaddar mu hannu bibbbiyu, zamu riqe wannan jarabawa, dakyau mumata kyakyawan duba yanda idan skamakon mu yatashi futowa zamu samu sakamako mai kyau."  ita kanta duniyar nawa take?"  kan ummii nak'asa takasa d'agowa takallesu tace *hanna*  ta 6ata wallhy *hanna*  ta6ata, gaban mama ne yafad'i rass, wani irin jirii ne yafara ebanta, amma kuma duk dauriyarta ta tattaro, da mamakin mutanen wajan gabaki

d'aya, murunushine kwance afuskarta, sannan cikin dakiya tace, kada ku damu da sanin Allah in sha Allah zai bayyanata, addu'arda zamu mata Allah yasa tana wajan kyakyawan hannu."
Shima baban dukda cewa abun yadakeshi addu'ar kawai yayi, share hawayen idonta umma tayi sannan tace, Aisha abun damuwar d'aya shine *hanna* bata cikin hankakinta lokacin da ta 6ata, *hanna* tahad'u da ta6ewar hankali, abunda yasa bangaya miki ba, bawanda yad'auka, zata dad'e cikin wannan jinyar, dan Allah kiyi hakuri, girgiza kai mama tayi tace hava yaya wani irin hak'urii kike bani?" bayan kuma mahaifanta ne, nasan kulawarda zaku bata, ko da inanan bazan bata hakanba."

Inada yak'inin kunfinii jin zafin 6atan nata, dan Allah kudena fad'in haka, kum,,, tarinda marshall yad'aukane yasa tayi saurin yin shiru, bai dad'e yana tarinba yalafa, mama ta kulada yadda wani abun da yafito abakinsa, amma yasa hannu yarufe, duk wannan abunda yakeyi, tashi mama tashi tak'arsa gabansa, batayi magana ba, kawai tasa hannunta tad'ago nasa hannun razana tayi ganin wani irin bak'ik'irin d'in jini, ga lebb'an bakinsa ma duk yaa6ci da jinin, dasaurii tajuyo tallaeshi tace abdallah tashi mutafii asibiti bakada lpy fa, shiru yake kamar yanda yasaba idan anmasa magana, ummii ne tace, kirabu dashi kawai ko zaki kwana kina masa magana ba kulaki zaiyii ba."
Koda bazai kulaba yakamata akira doctor yadubashi, umma tace, mamane ta amshe da cewa aman jinifa yakeyi, sai alokacin kuma duka hankalinsu yatashi, dan duk cikinsu bbu wanda yasan yana wannan aman."
Dasaurii mai martaba yad'aga waya aka kira likita, ba'a dad'e ba ya iso, dube-dube yafarayi, nan yajuya yakellesu yace, idanda hali asibiti yakamata mutafii, dan likitoci da damane yakamata su kasance akansa ayanzu haka, babane yace, doctor bafa zaije ba, ka kira likitocin nan suzosu, hakan kuwa akayi, nan yakira doctor's dakuma nurses, sukazo da motan hospital, hadda gado, buk'ata sukayi akan afita abarsu ad'akin, hakan kuwa akayi, sun d'auko awowi masu yawan gaske, kafin su fito, ababban falon mai martaba suk zaune, dukansu, anan likitocin suka semesu, bayanii likitocin sukayi sosai yanda hankalin mutanen falon gabaki d'aya ya tashi, d'ayan likitanne yace, gabaki d'aya zuciyarsa ta buga, kuma alamu yagwada ta dad'e cikin wannan halin, dan yanda muka duba tqkai kaman 2weeks, gaskiya abun yabamu matuk'ar mamaki, bamu ta6a kallo, kuma ko alabarii bamu ta6ajin wanda zuciyarsa takai wannan stage kuma yarayu ba."
Amma sai daiamakinmu ragaggene, idan mukayi la'akari da wanene shi, ayanzu haka dole yana buk'atar taimakon gaggawa daga nan, kafin ad'aukeshi, zuwa k'asar waje, abba ne yace yanzun abunda za'ayi kakira ambulance daga asibitin ku, akaishi can, sai ayi masa alluran bacci, dan jinya anan bazaiyiwu ba, nisawa d'aya litikan yayi yace, alokacin da zamu fara dubashi bbu irin alluranda bamuyi masaba, amma bawai yayi bacci bane kokuma hankalinsa yagushe ko d'aya, ahakan mukayi aikin, yanzu haka idonsa biyu sai dai kawai ba'a bud'e suke ba, sannan duk abubuwanda akeyi yanajii."
Ummii kam takasa magana, sai mamane tayi k'arfin halin cewa, kud'aukeshi ahaka, mutafii tare tafad'a had'eda miqewa, nurses ne suka tura gadon har zuwa gaban ambulance, tareda mama suka shiga, aminu kano suka nufa, nan aka kaishi aminty,"
Adakinda aka kwantardashi, mamane zaune itada umma da ummii,"
Satin marshall d'aya yad'an fara samun lpy, lokacin yakama 3weeks kenan da 6atan *hanna*

mamane ke jinyarsa asibitin, tana nuna kamar bata damu bane amma zuciyata nacike da kewa da kuma zulumin hainda y'artata take ciki, baba kuma yakoma, gabaki d'aya hospital d'in sanda aka zagayeshi da soldier, balle d'akinda yake kwance, doctor's ne suka samii mai martaba, akan ad'aukeshi daga wannan hospital d'in zuwa k'asar waje, dan sai sunyi kamar zasu shawo kan matsalar sai abun ya faskara, shawararda mai martaba yayanke kenan, shiga d'akinda aka kwantardashi yayi, yana kwance kamar kullum ba umm ba um umm, mai martaba yakalleshi sosai sannan yadubii mama da ummii yace, yaronnan kawai xan fiddashi ne hankalina yakasa kwanciya, haryanzu bbu wani takakkammen halinda yake ciki, yadubii mama sannan yace zankira Alh muhammad na fad'a masa zuwa jibi zaku wuce."

Muryarda yau watansu guda kenan, wanda suka dad'e basu jitaba, ne yakatsesu da cewa, ni bayanda zanje, ku barni anan, haryanzu ban fiddaran dawowar *hanna* kwana kusa ba."
Zaro idanuwa sukayi suna kallon ikon Allah."

To be continued

Ur's

Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by
*©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

_Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'S_

.

```Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi  ya ce Wanda ya yi sallar nafila rakaa goma sha! biyu tsakanin dare da rana Allah zai gina masa gida a cikin gidan Aljanna.```

```Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi yace, Wanda ya kiyaye yana yin nafila raka'a hudu kamin sallar azahar da kuma raka'a hudu kamin sallar la'asar to Allah zai haramta masa shiga wuta.```
.

```Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata agareshi yace, Wanda yake karanta ayoyi goma da daddare to baza'a rubuta shi cikin gafalallu ba, wanda ya ke karanta ayoyi dari to za'a rubuta shi cikin masu bauta ga Allah, wanda kuma ke karanta ayoyi dubu a cikin dare kullum to za'a rubuta shi daga cikin masu arzikin lahira.```
.

===============

Page 88

*
*Hanna* harta fara sabawa da mutanen gidan dan da farko ko abincii suka bata, baxata ciba, yanzu hartakan zauna idan sunyii abun dariya tayi tayi nawuce hankali,"

Hussentu ne tadubi diddi tace, diddi wallhy kullum idan naga yarinyarnan tausayi take bani, bansan su inne da yasa ishaq idan kusa dawo wani irin kallo zasu mata ba, bansan da Wata manufa zasu d'auketa ba, su halinsu yafice daban, wallhy diddi kaman bakene kika haifii yaya ishaq ba, kamar innece ta haifeshi, diddi batace komai ba, tacigaba da cewa, wallhy inason yarinyarnan har cikin raina, jinakeyi kamar y'ar uwata, Allah idan sukace tabar gidan saidai inbita mutafii tare, diddi dai shiru tayi saican tace wallhy nima inason yarinyarnan, sosai, banjin zanrabu da ita idan bawai tadawo hankalinta bane tanemi komawa gun danginta ba, yanzu tashi kije kidubamin metakeyi, kotacii abincin, tashi tayi tace to, azaune tasamu *hanna* tace, kincii abincin?"
Juyowa *hanna* tayi amma batace komai ba," ganin abincin tayi agabanta furr tak'ii cii, riqo hannunta tayi tace taho muje, tashi tayi tabita, dan yanzu komai nata da sauk'ii bandadai tayita dariya ba, bazaka ta6a ganewa da hauka ajikinta ba."
Tana zuwa tace diddi kinga tak'icii furr, dubanta diddi tayi da kalar tausayii tace, kinsan tanada juna biyu bakowani irin abincin suke so ba, riqe hannunta taje store da frigde kinuna mata koda abunda zataso, idan tagani zata nuna, jan hannun nata tayi zuwa frigde."

================

Da mamaki suka tsaya suna kallon sa, idanuwansa sunanan arufe kamar kullum, maganar ma bazakayi zaton daga bakinsa tafito ba,
Dama asali miskilancin sane yatashi, shiyasa yak'ii magana bawai dan bazai iyaba, bakuma dan maganar ta gagareshi ba."

Mama ta amshi maganar bakaso akaika to wani dalili zaisa bazaka cire damuwa aranka ba kasamu lpy, abdallah kayi tawakalli ga ubangijinka, kasan cewa jarabawace yad'aura maka, nan tayita masa nasiha, mai martaba ne yace ka shirya gobe da tafiyar dan nan d'innan bawai naga wani cigaba bane, idanuwansa arufe yak'ara cewa, har indai sai nafita kafin nawarke tom bazan ta6a warkewa ba."
Ummii ne takalli mai martaba tace dan Allah kabarshi anan d'in, tunda yayrada zaicire damuwa
```

aransa."
Mai martaba bai ce komai ba yafuce, office d'in likita yanufa, yana shiga litikan yatashi yana gaidashi, yana cewa ranka shi dad'e da kanka? Aida ka aika nazo, mai martaba bai kulashi ba yasamu waje yazauna sannan yadubeshi yace, nafasa fita dashi, Ina anan zaisamu kulawa sosai?'
Nisawa likita yayi yace zai samu amma saida taimaknku, dan mukad'ai abun yagagaremu, bazamu iya mukad'ai ba, dole aringa d'auke masa damuwa, sannan idan anan ne jinyan 2month zaidaukemu idan ak'asar wajan ne baifii 3weeks ba,
Mai martaba yace bbu komai, hakan kuwa akayi, anan aka fara jinyarsa, mama takanje bauchi tadawo,
Kuma kullum takansashi agaba da nasiha, harya fara cire damuwar,
Saidai abunda ba'a rasawa yanzu rashin magana harta nunka nada, dan saikayi sau 5baikulaba, watanshi 1yasamu lpy, amma sanda jinyarda suka yanke mata 2month dan yanda suka kalli yanayinsa mai karfin zuciyata, amma mafii akasarii akanyii 3-4month ana jinya, mai martaba ne yahana asallamesu har sanda yacika 3month cifff a hospital."

===============

Cikin *hanna* yad'an tasa kad'an, amma kana ganinta zakaga alamun tanada ciki, gawani kyau da takara, abun mamaki harda k'iba, dan yanda take samun kula,

Yaune takasance ranarda su ishaq ta inne zasu dawo, maimakon murna sai suka shiga fargaba da zullumii,"
Wasu rantsattsun motocine suka fara shigowa gate d'in, diddi ta kalli Hussentu wanda lokacii d'aya duka gabansu yafad'i tace, yi maza kisakata ad'akinki ki kulle dasaurii tajata suka shiga d'akin."

To be continued

Ur's
Z33iiyyb3rw3r

*BIBIYATA AKEYI*

*بسم الله الرحمن الرحيم*

Writing by
*©zaynab bawa*
*(Z33iiyyb3rw3r)*

_Like my page on Facebook=zaynab  BAWA novels_

_Join my group on Facebook= ZAYNAB BAWA NOVEL'_

.

================

Page 89

*

D'aki takaita, sannan ta kwantarda ita, tace bodd'i zauna anan, kijirani karki fito kinji, kamar wata mai cikakken hankali tad'aga mata kai."

Yawwa bodd'i na kinada jin magana tashafo fuskarta sannan tafice."

Wani kyakkyawan saurayi ne yafito daga motar, wqnda duk kyawunsu hussentu danake gani sainaga har sadik yafii kyau, hannunsa d'aukeda wata y'ar k'aramar yarinya wacce bazatafii 4yrs ba, gabaki d'aya saurayin bazai wuce sa'ar marshall ba."

Ko kad'an fuskarsa bbu annurii dan baiyi kama da masu dariya bama, dasaurii diddi tak'arasa ta d'ayan kofan, ta sa hannu ta bud'e, wata y'ar dattijuwa, nagano, kamar su d'aya sakk, da d'an saurayin daya fito daga motar, wasshe baki diddi tayi tana cewa, usse inne, wanda aka kirada, inne ta d'aga kai tayi kawai alamun ta amsa, daga yanayin matar yanuna tanada jin kaii sosai, tafiya tafarayii, diddi nabinta abaya, dasaurii hussentu tafito ta nufii yayanta, yarinyar datake hannunsa tamiqawa hannu amma yarinyar tamaqe, sake miqa mata hannun tayi da niyyar tad'auketa Ko bata so, daka mata wata uwar tsawa yayi ke wuce irin marar hankalin ne? Tace bazata zoba ana dolene?" jada baya hussentu tayi tana tsoron tayi gunguni yamaketa,
